[7/31, 10:34 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI.*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W.*

*Mmn Abduljalal.*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀
1-5.

*Domin Nishad'inku masoya.*😍😍

*بسم الله الرحمن الرحيم*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*"D*addy, gaskiya wnn qauye ya min,
ya ban sha'awa ba kad'an ba, har naji kamar na dawo nan da zama.

"D'an nema, tun yaushe nake binka mu zo tare da kai kana qi, an gaya maka ni d'in a banza nake son zuwa qauyennan ne.
Duk lokacin da na ziyarci qauyennan nakan samu nitsuwa ,kwanciyar hankali da nishad'i.
Snn yakan tuno min da abubuwa da dama wad'anda suka shud'e, shi yasa kaga bana jimawa ban leqo ba."

"Gaskiya daddy, nima ai yanzu na gane, tare zamu riqa zuwa."

Kallon shi na d'an lokaci daddy yayi.

"Kai Habibullah, wato babu maganar karatu a agender ka ko, har yanzu baka shiryawa tafiyar ba kenan kake ikrarin zamu rika zuwa nan tare.

Shafa kanshi Habibullah yayi yana neman abunda zai cewa daddy.

Isowar wata 'yar yarinya da gudu ya ceceshi dan ya rasa excuse din da zai bawa daddy.

Yarinyar tayi butu butu da ita, uniform dake jikinta duk yasha qura, gaba daya jikinta datti ne.

Kafa gwiwowinta tayi a kasa dab da tabarmar da suke zaune a kai, tana washe kananan fararen hakoranta, tana kuma haki, alamar taci gudu.

Idonta kan Daddy tace "Lah, baba Alhaji, yaushe kazo."

Shima kallonnata yakeyi da murmushi d'auke a fiskarsa, kafin daga bisani ya kawar da fiskarshi alamar fushi yake da ita.

"Nayi fushi 'yar Baba, tun jiya nazo garinku amma ban saki a ido ba sai yanzu."

Karyar da kanta tayi tace "Ayya, yi haquru Baba alhajina, bansan kazo ba."

Sai kuma ta rike baki "Lallai Innata da mugun hali take, yanzu a ce kazo tun jiya bata fad'a min ba."

Kallonta yayi yace "Um, um Bintu kada ki sake fad'ar haka, uwa bata mugun hali watakil dai ta manta ne."

Turo d'an qaramin bakinta tayi tace "Ba wani mantuwa da tayi, yoo in ba mugun hali ba baba Alhaji mai zai sa ma ta manta da zuwanka."

"To ko dai wani laifin kika mata 'yar baba?"

Gyara zama tayi nan kasa ta ce "tsaya babana in lissafa maka abunda nayi jiya ta rika make ni kamar na mata wani laifi.

Kaga da na tashi da safe, fitsari naje na fara yi, snn nayi alwala nayi sallah, na na wanke bakina, na tafi karatun allo, da na dawo sai hararata takeyi wai ina wasa a hanya na dad'e zanyi lattin Makaranta Ka ji d'aya.

Gyad'a kai yayi yace "Naji Bintun baba.

"Ban kulata ba, naje nayi wanka naci d'umame na na wanke hanu da bakina na na shirya na tafi makaranta.
Da na dawo ban san hawa ba ban san sauqa ba sai kawai naji dundu a bayana wai nayi datti da kayan makaranta na, ni qazama ce.
Kaji biyu.
Ta fad'a tana d'aga mishi yatsunta guda biyu.

"Naji Bintuna."

"Na uku kuma bayan naje islamiyarmu na dawo naci abinci nayi sallah, me ya rage?"

Ta tambayeshi tana waro mishi madaidaitan fararen idanunta.

Biye mata yayi da cewa "babu yar baba."

"Yauwa baba alhajina kana ji?"

"Ina jinki."

"Tunda babu abinda ya rage sai na fita na biya gidansu Indo muka tafi dandali muka warwasa ."
Tana fad'an warwasan tana girgiza jikinta irin ansha rawa d'innan."

"To meye laifina anan, kuma na manta ban fad'a maka ba dana dawo daga islamiyarmu ma
saida ta rankwasheni da zata aikeni wai saura kuma naje na zauna.
Kaji Uku.

"Duk fa nayi haquri na kyale shine kuma dan naje dandali ta kama ni ta zane ta kuma fad'awa
baffana ya min fad'a, dan Allah baba wnn ba mugun hali ba?"

Ta tambayeshi tare da kureshi da ido ita a dole amsa takeso ya bata.

"Bintu na kenan, ba mugun hali bane ,yar baba, tana yi miki hakane sbd ki zama ya ta gari, ki
zama mutuniyar kirki kinji ko?"

Gyada kanta tayi tace "naji baba alhaji. "

"Yauwa Bintun baba, daga yau idan an tura ki karatu ko aika ki rika dawowa da wuri ,ki daina
tsayawa wasa a hanya, kuma ki daina zuwa dandalinma kinji ko?"

Zaro ido tayi waje kamar an fada mata wani mummunan abu.
"Babana to rawanfa?"

"Kiyi a gida ."
Ya bata amsa a takaice.

Watsa hannayenta tayi tace "Ai gidanmu ba kid'a."

"To ki haqura da rawan ai ba dole bane, kuma ma karatu ya kamata kiyi ba rawa ba."

Ba tare da ta amsa ba ta maida kallonta kan Habibullah, da shi dinma ita yake kallo da mamakin yawan surutunta ba ko gajiyawa.

"Lah baba, ina ka samo dan Hindiyawa?"

Ta tambaya tana dubanshi sama da kasa.

"Yayanki ne, yarona ne shima Bintu."

"Tabd'ari amma aradun Allah, yayi bala'in kama da Hindiyawa."

Dariya yayi yace "A ina kikasan su."

"A TBn gidan kansila nake ganinsu."

Zuba mishi ido tayi ba ko kiftawa kamar yanda shima bai daina kallonta ba.

"Kai babana yaronnan akwai ruwan kyau."

"Kema ai kina da kyau Bintuna."

Farfara ido tayi tace "Allah, Baba Alhajina, to dani dashi wa ya fi kyau."

Qasa2 tayi da murya "Allah yasa yace nafi shi kyau aga ruwan yanga a garinnan."

Dariya dukansu biyu suke mata dan sunji abinda tace.

"Bintuna ai kinfi shi kyau, ya isa ma ya had'a kyanshi dana 'yar Babanta."

Wani murmushi jin dad'i ta saki tana kara qarewa Habibullah kallo.

Matsawa tayi kusa da shi tasa hanunta kan dimple d'inshi.

"Kai baba alhajina yaronnan gasa yake so yayi dani, kaga tayani kyaunshi irin nawa."

Dariya Daddy ya kuma yi "Ai naki ya fi nashi kyau."

Cire hanunta tayi daga fiskarshi ta mayar  kan fiskarta tana shafawa "Ni kodai kama mukeyi da shine, ko da yake ma Baba yace nafi shi kyau, shi dogon fiska ne dashi ni kuma nawa bai kai nashi tsawo ba."

Suna kallonta tana ta zuba shirmenta sai kuma ta mike da sauri "Baba alhajina Barin je inyi fitsari."

"To 'yar baba, daga nan kici abinci duka."

Kafin ya karasa tayi nisa dan ba karamin gudu ta kwasa ba.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Cikin nitsuwa ta fito tamkar ba itace ta gama zuba rawan kai awanni da suka shud'e ba.
Sake take da atamfa riga da zani sai d'an madaidaicin hijabi da ta saka light blue. Kafarta sanye da takalmin rubber.
Hanunta rike da 'yar ledar litattafan islamiyanta.
Tsaf tsaf da ita kamar ba ita ce tayi butu butu d'azu ba.

Nan inda ta bar su ta dawo ta samesu, kasan bishiyar mangoro, saidai ya ba suturar d'azu bane a jikinsu dukansu biyu.

Kusa da Daddy tazo ta rusuna "Baba alhaji na d'azu na manta ban gaisheka ba , ina wuni ?"

"Lafiya lau 'yar baba mun sameku lafiya."

Ba tare da ta amsa ba tace "Baba alhaji sai yanzu na samu na fito nan ma sbd zanje islamiya ne, ina fad'a maka innata ta b'aci da mugun hali kaqi ka yarda gashi ai ta fara nuna maka, daga barin je inyi fitsari in dawo ta rike ni ,saida naci abinci nayi wanka nayi sallah, ta kuma hana ni fita saida na kuma wani sallar kafin ta bar ni na fito."

"Bintuna ki daina cewa innarki tana yi miki mugun hali so take ki nitsu, ki rika hutawa , yanzu baki ga yanda kika fito fess dake ba, kinga kyaun da kika qara kuwa?"

Juya ido tayi "Allah babana?"

"Sosaima kuwa, yanzu dai tashi maza ki tafi islamiya idan kika dawo sai muci gaba da hirar mu ko?"

"To babana."
Ta fada tare da mikewa zata tafi.

"Baba alhaji sai na dawo, yaron baba alhaji kaima sai na dawo."

Habibullah dake kishingid'e ya mike ya zauna "Tsaya in rakaki islamiyyar."
[7/31, 10:35 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal.*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*5-10*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*G*aba tayi yana binta a baya har sukayi nisa.

Can ta juyo ta kalleshi taga da rata tsakaninsu.

D'aga muryarta tayi tace "Kai yaro, kayi sauri idan ba haka ba tafiyata zanyi in barka."
Sai kuma ta sauke murya tana cewa .
"Hmmm, idan kayi wasa idan ban barka ka bata ba, babanka yayi ta nemanka babu abinda ya shalleni.

Har ya iso kusa da ita mita take ta zubawa danjin haushin ya b'ata mata lokaci.

"Kaga yaro, wlh yanzu kam idan bakayi sauri ba tafiyata zanyi, kasan abinda nakeso inyi ne kafin na isa islamiyyar, ko so kake yau ma a tareni latti."
Ta karishe maganarta tana zumburo baki tare da fara tafiya.

Kamo hanunta yayi, "Wa kike cewa yaro?"

"Kai mana, to nasan sunanka ne, ba Babana yace kai yaron shi ne ba?"

"Idan ni yaronshine sai kema in zamo yaro a gunki, ganki yar mitsitsiya dake sai raini."

Kallonshi tayi fiska a daure, ganin shima nashi fiskar a daure tace " to aini bansan sunanka bane."

"Sunana Habibullah."

"Tabb, Habibalah."

Tace tana rike baki.

"Habibullah akace."

Ammafa sunan yaso yayi kama da na Abulahn gidan malam lawwalli."

D'aure fiska ya dad'a yi "Ke kika kuma b'ata min suna saina fasa bakinki."

"Yi haquri, kiran sunan ba dole bane, kuma ma naga bani na tambayeka sunanka ba, kai ka fad'a ko?"
Ta karishe da alamar tambaya.

"Ko ba ke kika tambaya ba sai kin fad'a daidai, dan bazan zuba miki ido kina cemin yaro ko bata min suna ba.

Suna ci gaba da tafiya tace "To kawai nace maka biba mana tunda sunan da tsawo, ni kuma ba iya wa zanyi ba."

Matse hanunta yayi da dan k'arfi har ta yi qara, "Kice Habi."

"Habi."
Tace da sauri.
Ya karasa da bullah."
Nanma ta maimaita.

To had'a ki fad'a muji."

Saida ta d'an d'au lokaci kafin tace "Bibillah."

"Ina kikabar harrufa biyu na farko, anya keko baffa ba asarar kud'in tara yakeyi ba?"

"Cabb, aka fad'a maka kud'in kirki yake ban ne balle yayi asara? Naira biyar ce fa, sai nayi sa'a ya bani goma wollah."

"To lissafa min, a sati nawa yake kashewa."

Shiru tayi nad'an lokaci daga bisani tace idan lissafin biyar biyar za'ayi a sati ishirin da biyar ne, idan goma ne kuma ishirin da biyar sau biyu, kuma ai ba kullum yake bani goman ba nace maka."

"Na wane ishirin da biyar sau biyu?"

"ishirin da biyar da ishirin da biyar."
Ta bashi amsa da full confidence dinta.

"Idan an had'a goma da goma fa?"

"Goma sha goma."
Nanma ta bashi amsa.

Nawa wnn?
Ya tambaya yana nuna mata gudan ishirin.

"shine ishirin din ai."

"To idan an had'ashi da wani ishirin d'in fa?"

"Ishirin da ishirin mana."

"Idan an had'a da goma fa?"

"Ishirin da goma."

"Gyara dai."

"To goma sha ishirin."

"Ammafa ke d'innan wawiya ce ta gaske."

Fizge hanunta tayi daga rikon da yayi mata "Kai Bibilah ni kake cewa wawiya da girmana?"

Duk da baiso yin dariya ba saida ya dara "Wai da girman ta."
Ya fad'a ranshi yana kuma murmushi.

"Yi haquri babba, muje kada kiyi latti."

Gyara tsayuwa tayi tana fiskantarshi "Bibi, ai, Habi, ba nace maka akwai  in da zanje kafin na je islamiyyar ba?"

"Ina ne?"

"Can gurin bishiyoyin yazawan (cashew) nan ka gansu can a jere, sai na cira zan isa islamiya raka ni muje kaji."
Har wani langabe kai takeyi ita gata mai wayo.

"Babu inda zaki sai kin iya kiran sunana."

"Na shiganga."
Ta fada tare da d'ora hanu a kanta."

"Yanzu duk kokarin da nayi baka gani ba? To qara fad'in sunan yanzu zan haddace."

"Ha.bi.bu.llah."
Ya fada mata daddaya.

"To me zai hana nace maka habu tunda yafi sauqi."

Zare mata ido yayi "Kinji nace miki Habu ne."

Kanta ta girgiza a tsorace tayi shiru kamar mai nazari, can tace "Habibi, dan Allah mu barshi haka ka rage min tsawon sunan.

Maimaita Habibi yakeyi cikin ranshi can kuma ya kalleta "Sake fad'a muji."

"Habibi nace."

"Yauwa barshi haka ma yayi."

Da sauri tace "To zamu je? Sai ka hau ma ka cire min na huta hawa, ko mai shi yazo yau bazan gudu ba dan nasan kana da karfi, ka jibgar min shi sosai fa, dama haushinsa nakeji kullum mutum yaje ciran yazawa idan ya ganshi sai ya mishi masifa, hhhh, yau kam zaka jibgu Baba audu."
Ta fad'a har da d'an tsallenta.

"Ta ina ne islamiyarku?"
Ya jefo mata tambayar.

Kaga wancan hanya? Da mun yanki kwanar can zakaga islamiyar an kewayeshi da karare."

Tana gama fad'i ya sunkuceta ba tare da yayi magana ba ya sab'a ta a kafad'arshi yabi hanyar da ta nuna.

"Kai, Habibi saukeni kada ka cuce ni, yau idan ban sha yazawan nan ba bazan ci tuwo ba."

Ko kulata baiyiba, ya ci gaba da tafiya.
Wuntsila kafafunta ta shigayi tana zamowa daga jikinshi.

A haka yaci gaba da tafiya tana ta zille zille da surutai har ya gane islamiyar.

Kofar islamiyar ya sauke ta ya had'e rai, "Maza shiga ciki kafin na kira malamanku su zane min ke."

Cuna bakin tayi ta shiga ji take kamar ta cijeshi ko zata huce takaicin da ya tura mata.

Zama yayi a kan wani gungumen itace kusa da islamiyar yana ta kalle kalle, har suka tashi.

mantawa tayi da cewa tare da wani take suka fito suna ta tsalle tsalle da qawayenta.

"Indo Innarki tayi gullun suwa?"

"Eh tayi anjima zan kai dandali."

"Muje ki ban rabona."

"Ki bari mana bintu saimun fita dandali."

"Allah yanzu zaki bani , ai kinsan ba ko yaushe nake zuwa dandaliba idan innata ta ganni hanani takeyi, jiya ma fa saida na sha duka da zagi da harara da rankwashi, ke innata muguwa ce fa."
Ta karasa tana rike hannun Hali dake gefen hanun hagunta.

"Hali ke kuma me innarki tayi?"

"Hana baba tashi."

Hadiyar yawu tayi tace "Yauwa indo mu fara zuwa gidan su Hali muci hana baba tashi kafin mu wuce gidanku.

Dadai sun karyi kwana zasu shiga lungun gidan su Hali taji an dawo da ita baya.

A tsorace ta kalleshi  ta waro idanu "Dama baka tafi ba, me kake jira ?"

Bai tankata ba yaja hanunta suka fara tafiya.
" Mun shiga uku turawa sun shigo gari sun fara satar mutane, wayyo Allah."
Indo ta fad'a da k'arfi.

Had'a baki sukayi dasu Hali suna kwala ihu "Jama'a ku zo ,ga bature ya saci Bintu."

Juyowa tayi tana dariya "Ku, kubari Habibi ne fa yaron Baba Alhaji, tare muka zo dashi yasin."

Jin ta fadi haka sukayi shiru suna kallonsu har sukayi nisa.

"Nifa yau kana ta cutata, ka hanani shan yazawa, kace d'aya."

Biye mata yayi yace d'aya."

"Ka hanani shan gullu suwa, kace biyu."

"Biyu ."yace

"Yauwa ka hana ni cin hana baba tashi, uku kenan ko? "
Tun bata ji abinda zai ce ba tace "Dan Allah baka cuce ni ba Habibi."

"Ban cuceki ba ke dai kika so ki cuci kanki, dan nasan idan kikayi dare duka zaki sha gurin innarki."

Dariya ta kwashe dashi "Kai yaro, ai Habu, wai,🙊 Habibi, ni fa bana cutar kaina da wayo na wlh, cin dad'i nakeyi son raina aradun Alla."

"Meye ma sunanki."

"Baka ji Babana yana ce min bintu ba."

"Banda shi fa?"

"Na ainihin kakeso in fad'a maka?"

"Eh."

"Na aininhin ainihin?"
Ta kuma tambayarshi."

"Eh, shi d'in."

"Fad'imatu ko Fatsuma amma fa bintu ake kirana."

"To ni Islam zan kiraki."

Wani wawan birki taci kamar wacce taji abunda ya tsoratata tace "Me? Islam, ban tab'a ji ba tunda innata ta haifeni, kuma itama tunda innarta ta haifeta bata tab'a ji ba nasan da ta fad'a min yasin."

"Ba sai kin taba ji ba ni hakan zan kiraki wuce muje."

Cigaba tayi da tafiyar tana mita a hankali "A a ba Islam ba idan yaso islamiya, haka kawai ka qala min sunan da ban taba jiba, kamar ma ba sunan mutane ba."

Sai kuma tace "Amma dai sunan Hindiyawa ne ko?"

" Ba a koya muku addini a makarantarku na boko?"

"Ana koya mana mana."

"To ya kuke kiran subject din?"

"I R K."
Ta bashi amsa."

"Menene full meaning na IRK."

"Ni nasan maka wani pulmin, zaka ta min yaren hidiyawa ance maka ina ji ne?"

Dariya yayi kadan yace "Turanci ni na miki ba indiyanci ba."

"To mu ba'a koya mana ba."

"Kina so na koya miki ?"

"Sosai ma , haba da anga ruwan yanga a garinnan wlh, yaro, au, Habibi sai wanda na ga dama zanwa magana aradu."

Dadai isowarsu kofar gidansu, ta fiskanceshi "Zaka koya min yanzu."

"Shiga gida Islam maghriba ta gabato sai mun samu lokaci."
Ya fad'a yana duba agogon dake d'aure a tsintsiyar hanunshi."

Turo baki tayi ta juya tayi hanyar shiga gida," islo," tace tana mai jin haushin sunan da ya qira ta dashi.

Har ta shige gida yana tsaye yana kallonta yana murmushi.

Gidansu da suka sauqa ya shiga ya tarar da Daddy yana shirin fita yayi alwala zaije masallaci.

"Sannu daddy."

"Yauwa Habibullah, kun dawo? ina yar tawa ?"

"Ta shiga gida Daddy, barin yi alwalar mu tafi tare daddy.....

*Aunty Ruqayyat ce .*🥀

*08161594233.*
[7/31, 10:39 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers.*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*15-20*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*B*ayan sallar azahar ta fito da yar littafinta 20 leaves da pen a hanu.
Sallama tayi a kofarsu taji shiru, cikin gidan dake manne kusa dasu ta shiga da sallamarta.

Kafin ta shiga ciki ta tsinkayo muryarshi yana hira da ɗan gidan cikin ɗakin bukkarshi.

Bakin kofar ta tsaya ta doka sallama, suna fitowa ta ɗaga littafin tana nuna mishi.
"Habibi karatu zamuyi."

"Ok."
Yace yayi hanyar waje ta bishi a baya.

Tabarma ya shimfiɗa musu qasan bishiyar da suke zama da daddynshi.

Da alphabets suka fara yaga ta iya, sai suka koma two letter words, sun dau lokaci suna karatun kafin ya rufe littafin yace su koma koyon fulatanci.

"Dame za'a fara?"
Ta tambayeshi.

"Me ma kika cewa yar tsakon nan ɗazu."

"Miyetti?"

"Eh, shi "Mi yeti ko?"

"Miyetti zaka ce."

"Miyeti."

"Mi..ye..tti nace, kaga aradu idan kayi wasa zaneka zanyi kar kaga ka fini girma, malaminmu yace ba a girma wa karatu"

"To miyetti."
Yace yana dariyar maganar ta, dan har wani waige waige takeyi ita nan neman bulala takeyi.

"Yauwa sake faɗa."

"Miyetti."

"Again."

Ci gaba yayi da faɗa ita ko ta kifa kanta kan cinyoyinta , sai can jimawa ta ɗago tace "Sau ɗaya kayi ka qara."

"Ke na gaji."

Zaro mishi ido tayi "Haka ake karatun, mufa idan aka ce mu qara qarawa mukeyi."

"To ni ba ku bane, mu ci gaba da wani kuma, yawwa me ma naji kike cewa tunkiyar can ɗazu?."

Saida ta ɗanyi jimm kafin tace "Oh, a tappaka?"

"Eh, me hakan yake nufi?"

"Ina nufin bata daku bane."

"To kace a tappakan mu muji."

Haka yayi ta mata tambayoyi tana amsa mishi daga bisani ta buɗe littafin tace yayi shiru zata yi

kiran suna.

Shirun yayi yana kallonta ta qarashi rubuce rubucenta can ta ɗago tace "Fatima Barkinďo."

Da kanta tace "Present."

Sai tace "Habibi Barkinďo."

Jin yayi shiru tace "Aradu idan bakace present ba aspen zan sa maka."

"Present."
Yace yana ci gaba kallon shirmen da take zanawa a book ɗínta.

Can tace "Halima Isuhu."

"idan  ba tazo ba aspen zaka ce min."

"Malamata tsaya in ɗan miki gyara kaɗan, ba aspen ake cewa ba absent ake cewa."

"Absel?"
Ta faɗa cikin nitsuwa dan so take ta faɗa kamar yanda taji ya faɗa.

Gyara mata ya rika yi har ta faɗa dadai.

Suna wajen har daddy da baffa suka dawo suka samesu, suka zauna a haka aka ci gaba da karatun har la'asar tayi.

Innarta na shiga sallar isha i ta kwashi takalman ta a hanu ta sanɗe ta fita.

Saida ta ɗan yi nisa da gida ta zuba takalmanta a kasa ta sanya, tana magana ita ɗaya " yasin yau sai na ci hana baba tashi, kuma dafa tallenma dani za a ci, haka kawai ayi ta cin daɗi bana ci.

Haka tayi ta surutanta har ta isa dandali.
Ba a cika sosai ba amma mutane sun fara taruwa.
Hankali kwance ta saki jiki suna ta zuba hira da kawayenta suna ta ciye ciye.

Can ta hango baffanta yana zuwa wajen yana ta dube dube.
Ta tabbatar da cewa ita yake nema.

Wuff ta mike ta shige cikin mutane ta samu ta bar wajen ba tare da ya ganta ba.

Gida ta nufa a guje tana suɗe hanu sbd romon dafa tallen da bai gama fita daga hanun ba.

A kofar gidan ta tsaya tana maida numfashi.
A hankali ta leqa ta hango innarta zaune tsakar gida kan kujera yar tsuguno ta rabka tagumi, fiskar nan q murtuke.

"Yau kuma muguntan sun motsa."
Ta faɗa a hankali tare da kaucewa daga gurin.

Jikin zanan gidan taje ta jinginu daga gefe, tana kallon duk masu wucewa.

Ta jima tsaye a gun dan duk lokacin da ta leqa tana hango innarta bata bar gurin da take zaune ba.

Baffanta ne yazo ya wuce cikin sauri hankalinshi tashe, tana jin yana faɗawa innarta bai ganta ba kuma ance bata je dandali ba.

Tana kallo innar ta fita ta shiga makotarsu, shi kuma baffa ya shiga gurinsu baba alhaji yana cewa bari ya duba ko ta shiga wajensu.

Cikin sauri ta shige cikin gidan ta nufi ɗakin da take kwana.
Adakar da suke zuba kayan sawarsu "Irin akwatin karfe babba na mutanen da ɗinnan.
Ta buɗe sauri sauri ta fitar da kayan ciki ta zuba ta bayan adakar, ta shige ciki taja kofar ta rufe ta bar ɗan guri kaɗan yanda iska zai rika shigo mata.

Tana ciki ta jiyo muryar yayunta mata biyu da suke qure sun shigo tare da innar suna ta jajanta al'amarin.

D'akinta suka shiga har da leka karkashin đan karamin gadon qarfen dake cikin ďakin.

"Kai, na gaji da yawo aradun alla, yanzu dan Allah ina yarinyar nan ta shiga tun ďazu."
Babbar yayarta ta fada tana fifita da gyalen da ta yafa.

"Allah dai ya bayyanar mana da ita cikin koshin lafiya."
Cewar ďayar tana kwance goyon ta.

Motsi taji a bayanta yasa ta saurin waigawa, bata ga komai ba, hakan yasa ta haska tocin dake rike a hanunta.
Babu abunda ta gani, yasa ta gyara zama suka ci gaba da jajantawa suna addua.

Can kuma suka sake jin motsi, ďayar tayi saurin haska tocin.

Ta gurin akwatin suka ji alamar motsin hakan yasa duk suka nufi wajen suna dubawa.

Motsi sosai tayi cikin akwatin wanda yasa su kwalla qara dukansu biyu suna rige rigen fita daga ɗakin.

Ihunsu ya janyo hankalin su baffa da su baba alhaji da ke kofar gida suma suna maganar yanda zasu bullowa al'amarin.

Dukansu suka ɗuru cikin gidan a lokacin da inna ta taresu take tambayarsu abunda ya sasu ihu.

Dakyar suka nitsu suka faɗa mata motsi sukeji a ɗakin Bintu.

Da sauri baffa ya shiga ɗakin  Habibullah na take mishi baya, dan ba karamin tashin hankali ya shiga ba da suka nemeta basu ganta ba.

Gurin adakan suka isa baffa yana haska tocila, tsit suka ji daga baya kuma suka kuma jin motsin.

Cikin dakewa baffa ya bud'e akwatin yayi saurin ja da baya.

"Dan kwalinta ne ya fara bayyana, hakan yasa Habibullah, leka akwatin.

Zuru zuru ya  ganta ciki tana ta raba idanu gata tayi sharkab da zufa.

"Islam."
Ya faɗa cike da mamaki .
Kasancewar basu san sunan ba yasa baffa ya matso sosai yana tambayar "Menene aciki?"

Abulle (zainabu) da Muna (Maimuna) yayunta  suka matso suma dan suga menene yake cewa islam ɗin.
Itako Inna tana daga bakin kofa.

"Bintu."
Suka haɗa baki wajen faɗa.

Dakyar ta mike ta fita ta fara murza idanu.

"Me ya shigar dake cikin nan."
Baffa ya tambaya cike da mamakinta.

"Bacci nayi Baffa."

"Bacci?"

Suka haɗa baki wajen faɗa.

Fizgota innarta tayi cikin jin haushi tana cewa "Babu wani baccin da tayi fakon idonmu tayi ta shigo ni na tabbata wani gurin taje."
Ta karasa tana kai mata duka.

Ihu mai qarfi ta qwala tana kiran innarta zata kasheta.

Cikin azama Habibullah ya jawota ya maida ita bayanshi yana cewa "Inna kiyi haquri bazata sake ba."

"Habibu da ka barta ta daku watakila ta yi hankali."

"Baffa kuyi haquri."
Wuff ta fice da gudu ta tafi gurin baba alhajin da ke tsaye daga hanyar fita.

Cikin muryar kuka tace " Babana daga bacci ya kwasheni cikin adaka shine fa innata ta fara dukana."

"To bintun baba me ya kaiki cikin adaka har kiyi bacci, duk kin ɗagawa mutane hankali."

"Baba kace kada ta dukeni bazan sake shiga ba."

"Baza ta dukeki ba ai, ya wuce."
Ya faɗa yana fita daga cikin gidan.
Shi ma Habibullah fita yayi har lokacin baibar mamakin abunda islam ta yi ba.

Suna fita yace "Daddy anya yarinyar nan lafiyarta lau kuwa, kaga inda ta shiga ta rufe kanta, ni fa ta bani tsoro."

"Lafiyarta lau Habibullah ita kuma kalar tata yarintar kenan."

Jinjina kanshi yayi yace "Nata yarintar ya bambanta da ta sauran yara."

Dariya daddy yayi yace "Kar ka sha mamaki a samu wacce ta fita ma."

Tana ganin sun fita ta faki idon innarta ta shige ɗakinta da gudu ta rufe kofar gararam.

"Ke buɗemu mu tafi gida fitinanniyar yarinya."

A tsorace ta kallesu "Me ya kawo da dare nnan nenne abulle."

Duka ta kai mata ta goce "da kika tasomu kika ɗaga mana hankali dole kice me ya kawo mu ai."

"Ku kuka so meye abin ɗaga hankali, kunsan ni bintu bazan b'ata a cikin garinnan ba ai."

"Sannu bintu min yetti."
Cewar Muna.

Bata kulasu ba ta ɗale gadon karfenta ta kwanta tana cewa "Idan kun fita ku rufe min kofa."

Innarsu taji ta shigo tana cewa "Kinyi sallah ne da kike kwanciya?"

Wuff ta mike ta kama gefen zanin abulle, "Nenne abulle binki zanyi, aradu inna dukana zata yi kema kin san halinta."

Tana ganin innarta ta nufota ta fita a guje tayi kofar gida tana kiran "Nenne abulle kuzo mu tafi."

Nacewa tayi saida tabi abulle gidanta ta kwana.

*Aunty Ruqayya ce.*🥀
[7/31, 10:41 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBAGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*20-25*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*D*a asubah aka tasheta tayi sallah ta tafi karatun allo.
Tana dawowa ta bata abun kari, daga nan ta shiga wanka.

Wajen shafa mai, ta fara bincike kwandon kayan shafe shafe, har tayi karo da kwalban maganin

mura na yara. (Coflin syrup.)

D'agawa tayi tana kallo a ranta take tunanin ko menene cikin kwalbar.

Can dai ta buďe kwalbar ta ďanďana, aiko taji zaki zaki.
Bulbuleshi tayi a bakinta ta shanye kaf kafin ta karasa shafa man, tare da shafa jan pankeke a fiskarta ta rangaďa kwalli a idanunta.

Yayarta abulle ce ta shigo tana ce mata tayi sauri taje gida tasa uniform ta tafi makaranta.

Cikin sauri ta kammala shirinta ta fita daga gidan.

Ta ďanyi nisa da tafiya ta fara jin idanunta suna son rufewa ga wani ďan banzan kasala da ya ziyarceta.

Tafiya ta cigaba da yi, har ta kusa isa gida ta fara layi.
Jiri jiri bacci bacci, ta rasa wannene takamamme yake damunta.

Jikin wani ďakin O, ta matsa ta baya ta dafa ginin tana zamewa kaďan kaďan har ta zauna.
Ganin zaman bai mata daďi ba kawai sai ta kwanta a wajen, take kuma idanunta suka rufe sai bacci.

Shiru Shiru innarta bata ga ta shigo ba ta fara magana, jin haka yasa baffanta fita ya aiki wani yaro yaje gidan abulle ya qira bintu.

Cikin dimbin mamaki da kullewar kai abulle ta shaidawa yaro cewa Bintu ta jima da barin gidanta.

Yauma kamar jiya haka sukayi ta nemanta.

Fitowa Habibullah yayi yana jiran fitowarta ya raka ta makaranta kamar jiya sai ya tarar da yauma nemanta akeyi.

Har da shi aka ďunguma aka tafi nemanta, duk gidan kawayenta sai da aka bi amma babu labarinta, gidan yayarta muna ma haka suka je basu sameta ba.

Har kogin kauyen suka je basu sameta ba.

Ba qaramin tashin hankali suka shiga ba, baffanta sai surutai yakeyi.
"Anya yarinyar nan ba aljanu gareta ba habibu, jiya ma fa kaga inda ta shiga kuma tace bacci takeyi a ciki, ko su suka sakata ciki."
Ya faďa cike da alhini.

Habibullah dai cewa yayi "Allah ya bayyana mana ita ya kare ta a duk inda take."

"amin, baffa ya faɗa cikin jimami.

Maiwada yaron da suka je kogin tare da shi, dake gaba dasu yake tafiya shi ya fara hangota kwance.
Da gudu ya qarasa gurin ya sunkuya yana kallonta dan son ya tabbatar da ita ɗince.

A guje ya koma baya gurin su baffa.

"Baffa gata can kwance bayan ɗakin Buba."

Da sassarfa suka qarasa wajen suka sameta a yashe tana sharar baccinta hankali kwance.

"Bintu."
Baffanta ya faɗa kamar zaiyi kuka yana jijjigata.
Maida kallonshi yayi kan Habibullah yace "Kaga inda suka kawo min ita ko Habibullahi."

Shiru Habibullah yayi yana kallonta dan kam kanshi ya kulle sosai, tunanin abunda ya kawota gurin ta kwanta yakeyi.

Hanu Baffa yasa ya ɗauketa Habibullah yayi saurin karb'anta daga hanunshi ya sab'ata kan kafaɗarshi.

Har suka isa gida tana sake kamar gawa.
Tun kafin su qarasa baffa yake kwalawa inna kira "Shatu fito mana da tabarma."

Tabarmar ta fita ta shimfiɗe sai gasu sun shigo da bintu a jiki a sake.
A hankali Habibullah ya kwantar da ita yana qare wa fiskarta kallo.

"Me ya sameta?"
Inna ta tambaya cikin tashin hankali.

Bayani baffa yayi mata yanda suka sameta a yashe, ta shiga salati da salallami.

Shi kuwa ya qara da "Shi yasa na ce miki bana son kina yawan dukan min bintu, kinga ashe aljanu gareta, kinga jiya inda suka turata yau kuma kan hanya suka sata bacci."

Zama inna tayi kusa da bintu ta ɗauki kanta ta ɗaura bisa cinyarta tana kiran sunanta a hankali.

Sun jima suna zaune a gun baffa da Habibullah sai tofeta sukeyi da addu'o'i ita ko inna sai girgizata takeyi cikin damuwa.

Suna cikin haka abulle ta shigo dan jin ko an ga bintun, nan kuma ta tarar da halin da ake ciki.

Cikin tashin hankali ta zauna itama kusa da innarta tana kallon bintu cike da alhini.

Cikin son yin kuka tace "Hande en woni" (Yau mun bonu.)
Inna a ina aka ganta me ya sameta?"

Baffa ne ya amshe zancen ya sanar da ita inda suka sameta da yanda suka sameta ya qara da cewa "Yarinyar nan ba ita kaɗai bace abulle, yauwa ɗauko min magani cikin bakin buhu a karkashin gadona yana kulle cikin bakin leda.

Da sauri ta tashi ta shiga ta ɗauko.
Hayaki aka gumbuɗa mata kusa da ita amma ko gezau sai su da suke ta sakin atishawa.

Can tunani ya faɗowa abulle ta zo zata bawa yaronta maganin mura bata samu maganin ba sai emptyn kwalba, kuma tayi tunani ko bintu ta zubar ko ta sha.
Snn kuma ta tuna mijinta yace kada ta bawa yaron overdose dan zai iya bugar dashi.
A ranta tace bintu ta sha maganin kenan.

"Inna ina tunaninfa maganin muran iro, Bintu tasha dan na duba ɗazu ban gani ba kuma babanshi yace in ansha da yawa yana bugarwa."

Tabbas hankalin inna yafi kama maganar abulle dan ita sam bata yarda cewa bintu aljanu gareta ba, ta daiyi shiru ne kawai dan kada tayi mishi musu.

Shima Habibullah Hankakinshi yafi kama maganar abulle sbd haka ficewa yayi ba tare da ya musu magana ba.
Saida ta biya ya sanar da daddynshi halin da ake ciki snn ya tafi ya sayo peak milk.

Dawowarshi ya tarar da su inna suna ta ɗura mata manja.
Saida ya shiga cikinta sosai snn suka kyaleta.

Ba da jimawa ba ta fara sheka amai ba kakkautawa da kyar ya lafa mata.

Komawa tayi ta kwanta tana lumshe ido, shiko baffa sai sannu yake mata kamar ya karb'a mata abunda take ji ya dawo kanshi.

Ta jima tana kwance kafin daga bisani ta tashi tana magana a harɗe " Inna bani kayana zan tafi makaranta."

"Yi haquri bintu yau kam ki haqura da zuwa makarantar."
Baffa ya bata amsa.

Tashi Habibullah yayi ya ɗauko cup cikin kwando kwanuka da aka wanke aka kikkife.
Peak milk ɗin ya b'ula ya zuba mata a ciki ya ce ta tashi ta sha.

Tashi tayi tana yamutsa fiska ta ɗauki kofin ta kafa a bakinta .
saida ta shanye tass ta ajiye kofin tana tanɗe baki.
"Qara min Habibi."

Haushi ne ya kama inna ta tashi ta bar wajen.
Saida ta shanye gwangwanin tass snn ta kalli baffanta " Baffa en bali jam."
Gaisuwa.
"Jam Bintu am."
Ya faɗa yana shafa kanta.

"Habibi ina kwana."

"Lafiya ya jiki?"
"Ni kam kar ka min fatan ciwo lafiyana kalau, ina baba alhajina?"

Shiru ya mata yana kallon yanda baffa yake binta da kallo cikin tausayawa, lallai ya tabbata baffa ba karamin so yake yiwa bintu ba, shi yasa itama take sonshi sosai.

Yayyafin da aka fara ne yasa su watsewa gaba ɗayansu, gudu gudu abulle ta koma gidanta itako bintu ta ɗauki dayan gwangwanin madaran da Habibullah ya ajiye mata kafin ya fita ta shige ɗakinta dashi ta ɗale kan ɗan gadon karfenta tana qarewa gwangwanin kallo...

»»«»»» «»»«»»«

Kasancewar yau alhamis ba ta je karatu ba, bayan sun kare karatunsu  tace mishi suje yaga kogin garinsu.

"Je ki tambayi inna ."
Yace mata.

Da gudu ta fito tana cewa "Mu tafi Habibi ta yarda."

Kogin suka nufa tana ta bashi labari har suka isa suka zauna kan yashin bakin kogin.

Tsintan duwatsu tayi ta tona rami daga gefe ta fara yar carafke.

Shi kuma ruwan dake gudu ya zubawa ido, can ya tsini kananan duwatsu yana jefawa cikin ruwa.

Bunjum, yaji ta faɗa cikin ruwa.

Ďagowa yayi yana kallon ta inda yaji karar faďawan, ya jima yana kallon wajen bai ganta ba, can ya hango ta nesa da shi ta fiddo kanta daga cikin ruwan tana wasa da jannayenta kan ruwa.
Can ta kuma nitsawa tana ta wutsil wutsil da kafafunta a guri ďaya tamkar kifi.
Daga baya kuma ta fara iyo cikin ruwan sauri sauri har ta iso kusa dashi kafin ta ďago kanta tana share fiskarta.

"Zo muyi bule Habibi."
Bai tankata ba kuma bai daina kallonta ba.
"Matsoraci kawai kar kazo mana."
Yaji ta faďa kafin ta kuma faďawa cikin ruwa.
Shi kuma ya maida hankalinshi ga mutanen da suke ta harkokinsu a kogin, wasu wanki kaya, wasu wanka, wasi yaran kuma wasanninsu kawai suke kamar yadda bintu takeyi, har da rige rige sukeyi cikin ruwan.

Saida ta gaji da bulen ta mike kayan jikinta sharkaff sun gama jikewa "Habibi bari na amso maka mangoro masu zaki a gonar baffa Iliya.

Kafin yayi magana har ta fara tafiya.
Da sauri ya tashi ya naďe kafar wandonshi yabi bayanta yana kiranta.

"Ka jirani ina zuwa."
Ta faďa cikin ďaga murya.

Bai fasa binta ba har suka haye kogin.

Cikin gonakin mangoron suka shiga, kafin ya karasa isowa har ta haye saman bishiyar mangoro.

"Sauko Islam."
Yace a tsorace.

"Ka cafke idan na jefo."

Jefo manyan mangoro ta fara yi tana cewa "Ka tare kar su fashe."

Da yawa ta tsinko tana jefowa, kanshi ďage sama yana kallon ikon Allah.

Yana kallonta ta fara bin reshe reshe tamkar biri tana saukowa.
Ta iso reshen karshe ta rike tana lilo.

Matsawa kusa da ita yayi yana mika hanu zai kamota.

"Ka matsa kar in faɗo a kanka."

Kafin yayi magana ta diro da karfi ta faɗo kasa.....

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 10:59 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal.*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*25-30*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Z*aro idanu yayi yana kallonta shi duk a tunaninshi ko taji ciwo.
Sai ganinta yayi ta mike tana kakkab'e jikinta, tana turo baki.

"Kai ina ta ce maka ka tare ka tare saida ka barsu suka faɗo baka tare ba, idan suka fashe aradu sai ka biyani."

Shi dai baice mata komai ba saima tunanin da ya fara yi kan maganar baffa da yace tana da aljanu.

Bakar leda mai ɗan girma ta fitar daga cikin zaninta ta warware ledar ta fara ɗura mangoron a ciki.

Kasan bishiya ya samu ya zauna yana bin bishiyoyin mangoro da ke gonar kallo.

"Habibiii."
Yaji ta kira shi da qarfi.

D'agowar da zaiyi sai ganinta yayi a bayan motar akori kura.

"Islam!."
Ya faɗa da karfi.

"Na tafi wuro magaji sai na dawo."
Ta faɗa tana waving ɗinshi.

Hannayenshi duka biyu ya ɗora a kanshi yana faɗin inna lillahi wa inna ilaihi ra ji uun.
Yana kuma bin motar da kallo har ta b'acewa ganinshi.

A kiɗime ya dawo bakin hanya suka haɗu da wani matashi yana tsaye yana b'abb'a ka dariya tare da kallon hanyar da motar su bintu ya bi, da alama wani abun dariyar tayi mishi.

"Dan Allah ɗan uwa ina yarinyar can ta nufa?"
Ya tambayi matashin kamar zaiyi kuka.

"Bintu, bintu, indai bintu ce anjima kaɗan zaka ganta ta dawo."

Ajiya zuciya ya sauqe ya koma jikin wata bishiya ya zauna ya dafe kai.
Addu a yakeyi Allah yasa ta dawo da wuri.

Yana zauna anan la asar ta sameshi yaje yayi sallah yaci gaba da jiranta.

Motar na isa garin magaji ta dira ta sauqa.
A guje ta shiga gidan kanwar mamanta tana kiran "Inna Dija nazo."

"Oyoyo Bintun Inna."
Innar ta faɗa daga cikin madafi.

Madafin ta nufa sukayi kicibis da inna tana fitowa daga madafi.

"Inna jam b'andu."
"Jam bintu yaya innarki."

"Lafiyarta qalau tace in gaisheki."

"Inna ina Haulatu?"

"Tana bacci."

Da gudu ta shiga ɗakin inna dije tana cewa "Ina ta tunaninta inna dije."

Jijjiga yarinyar ta farayi har saida taga ta buɗe ido.

Ďagata tayi ta jefa ta ta cab'e tana mata waqa (Haulatun Inna Dije na ta girma."

Tsakar gida ta fito da ita, yarinya sai binta takeyi da kallo.

"Ina Altine Inna."

"Tana gidan su Dijatu."
Da gudu ta fita rike da yarinyar inna tana " Bintu kada ki kada min ita."

Tare suka dawo da altine.
Suna shiga tace inna kin gama girki ne?"

"Bintu miya na gama saura tuwo."

"Miyan meye kika dafa."

"Karkashi."

"Yauwa inna zubo min zan sha shi haka, innata tace kar na jima."

Zubo mata inna dije tayi ta zauna ta na sha tana lasawa Haulatu a baki.

Tana gamawa ta tashi ta wanke hanunta.

Daga haulatu takeyi tana dariya itama yarinyar tana babbaka dariya.
Can tace.
"Altine bari in jefo miki ita ki cafe."

Da gudu inna ta fito daga ďakinta, ko kafin ta iso har bintu ta jefa wa altine ita.

Wani irin qara yarinyar ta tsanyara sbd zafin faďuwar da tayi ta dan altine bata samu ta cafe ta ba.

Da sauri bintu ta je zata ďauketa inna ta rigata ta dauketa ta sa mata nono a baki.
Dakyar ta samu tayi shiru.

"Maza bintu koma gida kada dare yayi miki a hanya."

Ta faďa tana mika mata naira ďari.
"Ki gaida innarki."

Hanun Haulatu ta rike, "Haulatu na kiyi hakuri, Altine wawiyace bata iya cafewa ba, baza mu

sake wasan da ita ba kinji."

"Jeki kedai Bintu ki gaisheda baffanki da innarki."

"To." tace ta fita tana tsalle tsalle.

Wani shago ta shiga mai ɗan girma, ta sayi babyn roba ÿar karama, da biscuit da sha ka hura.

Cikin zaninta ta b'oye ta nufi gurin motocin da tasan zasu koma qauyensu.

Daya ta tarar an loda buhuhuna, zata tashi, batayi wata wata ba ta ɗale bayan motar ta kame ta b'are biscuit ɗinta suna tafiya tana ci tana kalle kalle.

Kasancewar sun iso bakin kogin motar ta rage gudu.

Ganin bintu da yayi a bayan mota ya sashi mikewa tsaye da sauri.

Dirowa tayi ta nufo inda yake.
"Habibi ina mangoro na?"

Ta fara ce mishi.

"Ban sani ba dama kin bani ajiya ne?"

Turo bakinta tayi ta nufi gurin da tabar ledar mangoron
Wayam ta gani babu komai.

Wangale bakinta tayi zatayi kuka ta hango baba iliya da yaronshi suna zagaye gonar.

Da gudu ta isa wajensu, tana haki tace "Sannu baba ina wuni."

"Lafiya bintu yaya gidannaku?"

Langab'e kanta tayi ta marairaice murya tace "Baba baka ga mangoron da na ajiye cikin bakar leda acan ba?"

"Dama mangoron naki ne?"

Washe baki tayi tace "Eh nawane baba."

"To wa ya baki izinin cirewa."

"Um.am, baba baki mukayi shine nace bari in ciran musu mangwaronka masu zaki susha suyi

santi su bada labari a garinsu.

D'auko ledar yayi ya mika mata yace "Maza koma gida , kinga garin a haďe yake, kada ruwan sama ya sameki a hanya."

"To nagode."
Tace tare da barin wajen da sauri.

"Habibi mu tafi."
Tace mishi ta ci gaba da tafiya ledar mangwaronta rike a hanunta bata kuma damu da kallon expression da fiskarshi ta nuna ba.

Har suka haye kogin babu wanda yacewa wani qala.
Sunkuyawa yayi wa warware nad'in da yayiwa qafar wandonshi.
Ya ďago da niyar ya ci gaba da tafiya sai ya ganta tsaye kusa dashi tana kallonshi.

Warware babyn roba da sha ka huran da ta siya tayi daga bakin zaninta tana nuna mishi.
"Habibi, kaga babyna da na siya zanyi wasa, karfa ka faďawa innata dan kwacewa zata yi ta hanani wasa da ita.
Ga sha ka huranka da na kawo maka tsaraba, kar kuma kasa kwaďayinka akan biskin ďina dan na cinye duka ban rage maka ba aradu."

Kallonshi tayi jin bai amsa mata ba kuma bai karb'i sha ka huran da take bashi ba.

"Me ye, yaya da kallon?"

"Ke zan tambaya meye kam ai."
Ya faďa yana banka mata harara.

Haushi hararan ya bata.
Ta takarkare ta gyara tsayuwarta harda rike qugu.

"Mele da maleqata ya mele maka jan ido ka kasa ganin habbakar da rana da farin wata da tauraro guda bakwai.
Kaji min Habibinnan fa ni ban ďurkite ka ba (Harara.) kai da ka bar min mangora a tsakiyar gona har mai shi ya gani ya ďauka kai zaka ďurkite ni, kaji min fa."

Ga abin dariya ga abin haushi ya rasa ma wanne zaiyi ďaya sai kawai ya kama kunnenta ya murďe ""Ke wani irin rashin ji ne yake damunki, yanzu da kika shiga motar mutane suka tafi dake da sun sace ki fa."

"Wayyo Baffana."
Ta faďa tana rike hanunshi dake rike da kunnen.

Sakin kunnen yayi ya fara tafiya ya jinta tana magana.

"Motar kawujin ne zaka ce zasu saceni, mukam garinmu ba a satan mutane saidai in a garinku, kar ka mana fata umhum, kuma mun b'ata nayi fushi da kai kar ka sake yai min magana, kuma in ka sake ce min islam wuta bal bal, bullukutun bakar mutuwa."

Shi dai gaba yayi ya barta tana ta soki burutsunta, Alla alla yakeyi su koma gida lafiya kar ta b'allo mishi wata damuwar kuma.

Ganin ya mata nisa ta ruga da gudu ta kamoshi amma ba magana bakinnan a ture, ita a dole tana fushi.

Wake wakenta ta fara rerowa da fulatanci ta yi wannan ta sake ta kama wancan.

Wasu gun gun shanukai ne suka tunkarosu, yana gani ya koma gefe can ya fara bin cikin ciyayi. Itako hijabinta ta cire ta saka ledar mangoronta a ciki ta ďaure  tagoya mangoron a baya.

Cikin shanukan ta shiga tana wakewakenta tana tab'a duka wanda tabi kusa dashi.
Saida suka gama wucewa kafin ya fito kan hanya.

Dariya ta tuntsire dashi tana nuna shi "Habibi ase kai kulďo ne (Matsoraci ) ase haka kake da kulol (Tsoro.)

Kallon yanda ta dage take dariya har da sunkuyawa yayi ya kalli sama yanda hadari yake kara haďuwa yace.

"Ke, ki wuce mu tafi kada ruwa ya tare mu anan."

Haka kawai sai taji ba dadi da ya ce mata ke.
"Ni ba sunana ke ba."

"Ni bansan wani sunanki ba to kuma kince in na kira ki islam wuta bal bal.....

Tun bai kare maganar ba tace "To kace islam ďin na yafe ka."

"Ni kam mu tafi kada ki jaza min mura."

kafin su isa ko ruwa ya sako, gudu ya fara, ya juyo sai ya ganta ta ware hannayenta ta rufe ido tana tsaye ruwa na dukanta, sai dariya takeyi da alama nishaďi ruwan yake sakata.

Dawowa yayi kusa da ita zai mata buďa mata wuta dan tayi sauri su tafi , sai kuma ya tsaya qare mata kallo.

Dariyar da takeyi ya bayyanar da jerarrun fararen haqoranta, dogayen gashin idanunta suka jike da ruwa suka qarayin baki sidiq, sai cikakken bakin gashin girarta da ya kwanta lub.  ga lotsawar dimple ɗinta wanda ya qara wa fiskarta kyau.
Sai yau zai iya cewa ya tsaya ya kalleta da kyau, lallai ya yarda da maganar daddynshi da yake ce mata itama kyakkyawace.

Ware idanunta tayi a kanshi sai kuma ta hau share fiskarta da ruwa yake zuba akai.
Hanunshi tayi tsalle ta cafke tana lilo dashi, "Kai Habibi ya kaji daɗin ruwannan."

Kawar da kanshi yayi daga kallonta "Sake min hanu ba kin ce mun b'ata ba kada in sake yi miki magana."

Sake shi tayi ta sauri ta ɗaure fiska, "Ai nima dan na manta ne."

Waige waige ya farayi yana duba kasa.
"Me kake nema?"

"Bulala."

"Me zakayi?"

"Tsabgeki zanyi dan naga taurin kanki yayi yawa, KUNNEN K'ASHI gareki."

"Banda duka kam Habibi kaji, mu tafi bazan sake maka taurin kai ba.
 Inji baffa na yace ni 'yar albarka ne ko?"

Shiru ya mata yana jan hanunta suna tafiya sauri sauri.

"Kaga fa ban isa YUSA bafa gun inna kulu, a wuro magaji kawai na tsaya gurin inna dije.

Kallonta yayi yace wani yusan kuma bayan wannan.

"Yusan biyu ne fa, akwai yusa, A, Hab'e ("Arna ) su suka fi yawa a gurin, sai ka wuce wuro magaji zaka je wajen, idan kana zuwa daga jalingo kuma sai ka wuce wajen zaka isa garin magaji .
nan kuma YUSA B. ne shi ake kira Yusan fulani.

"Wonderfull."
Taji yace.

"Hhhh Habibi ai ful da ful kam e ton wuro magaji. Nufinta ( wonderful yana garin magaji.)

"Me kenan kika ce?"

Fassara mishi tayi har da daddagewanta.

"Wonderful nace ba ful da ful ba."
Ya fada yana dariya.

"Oho, woldaful ai na iya ko?"

"Um, kawai yace mata suka ci gaba da tafiya, kafin su karasa ruwa ya gama jika su sharkab.

Koda ta shiga gida inna tana mata faɗa sai cewa tayi gurin inna dije taje kuma tace a gaisheta, tana faɗa tana tub'e kayan jikinta ta saura da pant, har zata shiga sai ta dawo ta ɗauki ledar mangoronta ta shiga dashi.

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 10:59 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*30-35*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*D*a daddare, tare suka shiga da baffanta gurinsu baba alhaji tana rike da ledar mangoro da hanun hagu, hanun baffanta da hasnun dama.

Suna isa ta gaida babanta ta ciro manyan mangoro nunannu guda uku ta ajiye mishi, tace "Baba alhaji ga tsaraba."

"Ina kikaje."

"Gona muka je ɗazu da wannan."
Ta faɗa tare da nuna Habibullah.

Sauran biyu na cikin ledan ta mikawa daddyn tace "ka bashi idan na fita."

Dariya daddy yayi yace "Ba gashi kusa dake ba me yasa baza ki bashi ba?"

"Mun b'ata bamu magana baba, mangoron ma na bashi ne dan kar yace tare mukaje yana gani na cire ban bashi ba, Allah ya so shi ma ɗaya ne kawai ya fashe da ko ɗaya bazan bashi ba yasin."

"Rike mangoron ki bana so, ai nima bance ki bani ba."

Matsowa tayi kusa da shi "Yi haquri habibi na yafe maka kasha kaji."

"D'auki kayanki nace bazan sha ba."

"To a andi Allah a waɗa munyal mi metata."

"Banjiki ba ai."

"Nace in kasan Allah kayi haquri bazan sake ba."

"Ba zaki sake me ba?"

"Taurin kai."

"To kaji , tace baza ta sake ba."
Cewar daddy.

"Yauwa kaji babana ma ya faɗa maka, karb'a kasha kaji, da zaki aradu.

Karb'an ledar mangoron yayi daga hanunta yana cewa "Sai ki kawo min ruwa na wanke kafin nasha.

»»»»»»« »»»»»

Sabo sukayi sosai har ya kasance yanzu cikin gidansu bintun suke karatu.

Yau ta kama asabar kuma aranar zasu koma jalingo.
Da safe sukayi karatu  kan tabarma, a cikin gidan su bintun.
Innako tana ta kai kawo tana ayyukan gida.

Saida suka kare karatu yace mata "Islam yau zamu koma gida."

Waro ido tayi tace  "Kace aradu."

"Aradu."
Yace yana dariya.

"Kace yasin."

"Ke bana son shirmen ki nnan, meye wani aradu, da yasin kuma."

"Rantsuwa ne mana."

"Ana rantsuwa da wani abu bayan Allah ne banda shirmenki."

"To meye aradu da yasin ɗin."

"Kin san tsawa da akeyi idan ana ruwan sama ko idan za ayi?"

"Na sani ba wnn giriri ɗin ba?"

"Shi ɗin dai, to shine aradu, idan kina yawan ambatar shi kuma hmm ni dai babu ruwana."

"To me zai faru?"
Ta tambaya tana watsa hannayenta.

"Ni dai bazan faɗa ba, ki daina faɗa kawai."

"Yasin fa."

"Yasin sura ne cikin al -qura'ni mai girma."

"Kace aradu yasin ba sunan Allah bane?"

Zaro idanunshi yayi "Baza ki daina ba ko, ba ruwana fa."

"Na daina to yasin bazan kuma ba."

Yar karamar tsaki yayi murmushi yana escaping lips ɗinshi.

"Islam zan yi missing ɗinki, ke fa?"

"Na san maka shi?"

"Me ɗin?"

"Misil ɗin."

"Missing nace miki."

"To meye shi ɗin ban sanshi ba."

"Zakiyi kewata idan na tafi?"

"Kewa ? Meye shi?"

"Islam."

"Na'am."

"Ba zakiyi tunani na ba idan na tafi?"

"Tunani kai, Habibi har da mafarki ma."

Murmushi yayi yace "To shi nake nufi, idan na tafi zanyi ta tunaninki."

"Yeah, Habibi, kayi ta tunani kar ka manta ni fa."
Ta faɗa tana girgiza mishi yatsar ta manuniya.

"Bazan manta ki ba islam, nima kada ki manta ni kinji."

"Haha, Habibi, bazan manta ka ba ai, kaga kullum sai na tuna dogon hancinkannan, da wannan tayani kyaun irin nawa, zan rika tuna fiskarka, da dariyarka, da ɗaure fiskar nan da kakeyi, da tafiyanka, da sa hanu cikin aljihunka, kai kai na manta har da tsoron shanunka hhhh."
Ta karishe da dariya.

Dariyar shima yayi yace "Islam idan na  rokeki wani abu zaki yi min."

"Zanyi."
Ta bashi amsa cikin saurin baki.

"Dan Allah ki daina b'atawa inna rai, ki daina zuwa dandali, ko ba dan dali bama ki daina fita yawo idan ba aikanki tayi ba, ki daina wasa idan an tashi karatu, ki daina biye biyen gidan mutane, kuma ki rika karatu sosaifa."

"Kai Habibi ka rage mana yayi yawa."

B'ata rai yayi "Babu wanda zan rage a ciki idan bakiyi niyyan bari bane ki faɗa tun yanzu."

Marairaicewa tayi tana kallonshi "Ni dama dan kar kazo ace maka nayi wani abunne kace banji maganar ka ba shi yasa."

"Bakiyi niyar gyarawa ba kenan."

"Nayi zan gyara."

"Yauwa my islam, I love U."

"Taɗari, aradu ba don yau zaku tafi ba da sai na rama zaginnan, haka kawai dan zaku tafi sai ka antaya min zagi, haka ranar ma naji ka ka faɗa kyaleka kawai nayi aradu, ka jima kana zagina da turanci ina haquri, idan ba zagi ba me yasa da na tambayeka abunda ka fada kaki fassara min kamar sauran?."

"Rama zaginki  islam."

"Ni dai na yafe."

"Ni kuma ban yafe ba sai kin rama."

"A lob yu ma Habibi kai ma kaji inda daďi."

"Yauwa kinga mun tashi one one kenan babu wanda ya kwari wani ."

"Habibi ."

"Na'am Islam."

"Yaushe zaku sake zuwa?"

Zamu zo ai, ko zaki bimu ne?

Washe baki tayi sai kuma ta ďaure fiska.
"Kana ji ba, Habibi, da ba don baffa na ba da binku zanyi ko dan na huta da dukan da innata takeyi min, kaga yayana mudassiru da ya koma gidan kawunmu a jalingo ya huta da duka ai."

"To muje kema kiyi karatu a can mana."

"Taďari, in tafi in bar Baffa na, aradu na fi sonshi a kan kowa ma, bazan biku ba yasin."

Kallo inda inna take yayi, ta kawar da kanta tana harkokinta tamkar bata jinsu.

Kusa da ita yaje ya tsuguna ya mata sallama kafin suka fice tare da Islam.

Gurin Baba alhaji suka je suka sameshi tare da mutane , daganan suka wuce gidajen relatives ďinshi ya musu  sallama suka dawo.

Saida taga tafiyarsu kafin ta shiga gida tana sharar kwalla.

Daga ranar kuma kayan da baba alhaji ya kawo mata tsaraba su suka zama kayan sawarta, sai innar tayi da gaske take sa wasu.
Hirar Habibi kuma duk inda ta zauna sai ansan labarinshi.

Kusan kullum sai yakira baffanta sun gaisa ya kuma ce a bata wayar su gaisa, tun tana tafka mishi qauyanci a wayar yayi ta dariya har ta saba, a hakan kuma yake kara mata karatu.

A b'angaren Habibullah ma haka abun yake , kullum sai sun sha labarinta a gida, daddy ma har qara basu labarin wasu daga cikin shirmenta yakeyi suyi ta dariya.

Yayarshi Nafeesat dake zaune da mijinta da 'ya'yanta biyu a Owoniyi quarters duk da ba tare suke ba, amma tasan labarin Islam.
Wani lokacin idan yaje gidanta har gaisawa sukeyi da ita ta waya.

Saida suka kara watanni uku kafin suka kuma zuwa YUSA.
Wnn karo Islam (Bintu) tasha tsaraba fiye da yanda ta saba samu daga guri baba alhaji, murna kuwa kamar ta goya Habibi takeyi, labari na kirki, shirme har da na wofi duk ya shasu.

Wnn karo kwana uku sukayi suka koma.

Daga baya ya zamanto ko daddy baice zai je ba Habibullah yana zuwa ya wuni ko ya kwana, wani lokacin tare da yar shi Nafeesat suke zuwa su zaga dangi.

BAYAN SHEKARA BIYU.

Cikin tashin hankali daddy ya fito yake kwalawa Habibullah kira.
A tsorace ya fito yana amsawa, tare tambayar daddyn ko lafiya dan ya ganshi duk a hargitse.

"Yi maza ka shirya yanzu zamu tafi Yusa, Baban yarinyar nan ya rasu."

"Wace yarinya daddy."
Ya tambaya gaban shi na faďuwa.

"Bintu, yanzu Malam Husaini ya kira ni ya sanar dani rasuwan."

"Inna lillahi wa inna ilaihi rraa jiuun."
Ya furta yana juya kai cikin alhini.

"Jeka Habibullah, kwana uku zamuyi sai anyi uku zamu dawo."

Da sassarfa ya shiga ɗakin ya fara shiri.
Haɗa kayanshi yakeyi amma tunaninshi na ga islam, wani hali take ciki yanzu? Ko me take ji cikin zuciyarta, ya tayi da ya rasu."
Har ya kare shiri tunanin da yakeyi kenan.

Lokacin da suka isa sun tarar an kaishi,sai jama a suka tarar cike a kofar gida, mata kuma sai ɗuruwa cikin gidan suke, wasu daga kauyukan da suke makwabtaka dasu ma suke zuwa.

Nan suke jin cewa lafiya aka rabu dashi jiya da dare ya shiga gida bayan sunyi sallar isha' i dashi kafin asubah Allah ya amshi kayanshi.

Hankalinshi ne ya gaza kwanciya dan baiyi tunanin zai iya jira zuwa  anjima su shiga ciki  kamar yadda daddy ya ce ba.

Can dai ya tab'o Ila wanda suke kusan sa 'o' i dashi dama shine abokin hiran in yazo garin duk lokacin da islam taje makaranta.

"Mu shiga ciki Ila ina so inga Islam."

*Aunty Ruqayya ce*🥀
[7/31, 11:00 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*35-40*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*S*higa sukayi sukabi duk inda matan suke tare suka gaishesu.
Har cikin ɗakin inna suka shiga suka sameta suka gaisheta.
Ilan ne ya tambayi inda Bintu take.

Kwance suka sameta cikin ɗakin baffanta, yayarta Abulle zaune kusa da ita.
Rungume take da rigar baffan a jikin ta ta kudundune jikinta gu ɗaya.

Gaisuwar da yayi wa abulle ce ya sa ta tashi da sauri tana kallonshi, shima ɗin kallonta yakeyi cikin tausayawa , fiskarnan tayi jazir, idanun duk sun kumbura, da ka ganta kasan ba qaramin kuka ta sha ba.

Tausayinta ne ya daɗa kama shi, tunawa yakeyi da lokacin da take ce mishi tafi son baffanta kan kowa, ganin baffan yakeyi yanda yake tasata gaba yayi ta kallonta cikin nuna tsantsar soyayyar da yake mata, irin kulawar da yake bata, da yanda idan tayi laifi ko ya mata fada sai ya koma lallashi, gashi yau mai rabawa ta raba, mutuwa ta ratsa tsakanin bintu da baffanta,Lallai Allah ba ya bari wani dan wani yaji daɗi.
Allah yaji kan baffa yasa ya huta.
Baisan sanda kwalla suka fara kwaranyo mishi a fiska ba.

Fashewa ta yi da kuka ta rarrafo ta zo ta ɗora kanta jikinshi "Habibi baffa ya tafi ya barni, sun ɗaukeshi sun tafi dashi sun binne shi cikin qasa, jiya da daddare fa yace min zai je Yusa A ya nema min makarantar gaba da primary, amma yau ya tashi ya mutu ya tafi ya barni."

Sai ta kuma fashewa da kuka har kamar zata shiɗe.
Ba shi kadai ba Abulle da Ila ma duk tayata kukan sukeyi , dan dukansu shaida ne a kan irin shaquwar dake tsakanin bintu da baffan.

Babbuga bayanta yakeyi kaɗan kaɗan yana share hawaye.
Dakyar murya a shaqe ya iya ce "Hakuri zamuyi Bintu, Allah da ya ɗauke shi ya fi mu sonshi, kowa kuma lokacin shi yake jira, baffa kam saidai mu bi shi da addu'a, Allah yaji qanshi ya sa aljanna ce makomarshi, Allah ya kyautata makwancinshi."

"Amin."
Duka suka amsa banda bintu dake ta shessheka.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Har akayi uku jinyar Bintu da lallashinta ake dan duk lokacin da abun ya fađo mata sai ta birkice musu.

Sosai baba Alhaji ma yake kokarin ganin ya kwantar mata da hankali.

A lokacin da zasu koma Habibullah ya shiga cikin gidan domin sallamarsu.

Lokacin jama a sun watse sai yan uwan inna da na baffa, mata uku, yayarshi đaya da kannenshi mata biyu.

Dukansu suna cikin đaki sai Bintu dake takure jikin zana tana ta sharb'an kuka, Abulle tana gindin murhu tayi jugum, sai Muna da ke wajen wanke wanke, dukansu kallo đaya zaka musu kasan suna cikin tashin hankali.

Kusa da bintu ya matsa ya sunkuya, "Mene ne kuma Islam?"

Cikin kuka tace "Ba goggo Rabi ce tace zata tafi dani ba, kuma zata bawa yaronta yunusa ni ya aura, kuma tace bazan sake karatu ba.

Shiru yayi zcyrshi na bugawa, can kamar an mintsine shi ya mike ya fita cikin sauri.

Cikin tashin hankali yake fađa mishi abunda Islam ta fađa mishi ya qare da "Yanzu daddy haka zamu barta ta tafi da ita watakila taje tayi ta bata wahala, tunda ta tab'a ce min matar bata son innarta bata sonsu, duk lokacin da tazo sai tasa innarta kuka.

Shiru daddy yayi yana nazarin maganar Habibullah.
"To ya zamuyi Habibullah, watakila haka Allah ya tsara mata rayuwarta."

Kamar zaiyi kuka yace "Daddy dan Allah kayi wani abu akai, ka roki baffanayentannan su bamu ita mu tafi da ita tayi karatu a can."

"Habibullah su fa basu barin yaransu suyi karatu sosai, kaga itama zaiyi wuya su barta ,gashi ma kaji har sun fara maganar yi mata aure daga yanzu."

"Daddy yarinyar nan baza ta wuce 12 yrs bafa, idan akayi mata aure zata cutu."

"Hakane Habibullah, amma ai kaga su haka sukeyi, baka ga yayunta ma ba,ba wani girma ne dasu ba, amma kaga har da yaransu."

Guri đaya ya kafawa ido Kamar mai tunani yayi, cikin sauri ya đago ya kalli daddyn.
"Daddy to a đaura auren dani, kaga sai mu tafi da ita kawai tayi karatunta a can."

Shiru daddy yayi a ranshi yana cewa "Tarihi zai maimaita kansa kenan."

A fili kuma sai yace "To idan akayi airen yaya zaka yi da ita, dan nasan tausaya mata kakeyi.

"Daddy har da sonta ma inayi, ka nema min auren kawai."
Ya faɗa cikin rawar baki.

Ajiyar zuciya daddy ya sauqe yana tunanin ya samu wata dama da zai tankwara Habibullah ya tafi karatu, ga kuma ladan taimako.

"Habibullah, zan nema maka auren Bintu, amma da sharaɗi ."

Da sauri yace "Faɗi sharaɗin daddy komai wahalarshi zan bi."

"Ba wani mai wahala bane, sharaɗin shine zaka  tafi makaranta kamar yanda na buqata tun farko."

"Daddy!
Yafaɗa yana zaro ido.

"A a ba dole bana Habibullah, idan baka so shi kenan sai a haqura kawai a aurar da ita ga wani."

Da sauri yace na yarda Daddy zan tafi makarantar.

"Ma sha Allah, Allah ya tabbatar da alkhairi."
Yace kafin ya bar wajen ya tafi gurin iyayen bintu maza.

Bai wani sha wahala sosai ba suka amince mishi dan dama sun sanshi suna sane da mutunci da alkhairin da yake yiwa ɗan uwansu, shi yasa suke mutunta shi.

Cikin gidan suka shiga dan sanar da mahaifiyar yarinya da sauran yanuwa.

Dukansu sun ji daɗin maganar banda goggo Rabi da goggo Rahi.

Shi yasa da suka fita suka hau zagin inna kan cewa ta nuna tafi son bare akan su dan taga yana da kuɗi, shi yasa ta mallake musu ɗan uwansu ta hanashi qara aure  dan idan ya mutu ta gaji shanukanshi, gata ba haihuwar kirki takeyi ba, shekaru goma sha tara da aure 'ya 'ya huɗu kacal."
Zagi dai kala kala, su kam sai kuka sukeyi, suna tuna baffansu.

Ɗaga tafiyar sukayi.
Washe gari aka ɗaura auren *Habibullah Muhammad Bello*
Tare da.

*Faďimatu Barkinďo*

Akan sadaki dubu Ishirin.
Habibullah kam ya rasa wani yanayi yake ciki, dan farin ciki yanayi saidai ya rasa gane abunda yake faďar mishi da gaba, daga baya ya alakanta hakan da zuwan auren a bazata ne ya sa yake jin hakan.

Makwabta da suka ji labari sai shigowa yima inna barka sukeyi.

Shirye shiryen tafiya akeyi ,inda aka sa goggo Rabi da inna Dije zasu bisu a cikin mata, su ko maza baffanta wan babanta ne zai je.

Neman bintu akeyi ta fito tayi wanka su tafi abin mamaki aka neme ta aka rasa.

Nemanta aka shigayi gida gida sbd tunanin ko bata so ta rabu da innarta ne yasa ta gudu ta b'uya.

Gidajen qawayenta duka saida akaje amma suka ce bata shigo ba.

Yayunta gidajensu suka koma suka duba, Abulle har da leka kasan qado dan ta san ba abin mamaki bane Bintu ta makale a wajen,nan ma shiru.

Habibullah har gonar mangoro da suka je da ita ranannan saida ya je yayi ta duba saman bishiyoyi, amma babu ko alamunta.

Lokaci guda labari ya karaďe kauyen cewa Bintun Marigayi Mal. Barkiñďo ta b'ata, abunka da kauye tuni aka hau shigowa gidan dan tabbatarwa.

Wasa wasa har yamma ana abu ďaya babu labarin bintu.

ŤIRQASHI.
Wai ina Bintu ta shiga ne?"

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:01 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*40-45*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*HIP....HIP.....HIP*

*HURRAY*
🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂
*Just chill it's ur birthday*
🍰🍰🍰🍰🍰🍰🍰🍰
*HAYATU BABA ZUBAIR*

*Admin of Admins, Cool nvls & Make up and kitchen*
*Wishing u many more blessed years ahead.*
🍰🍰🍰🍰🍰🍰
*This page is specially dedicated to u*
*Happy Birthday*
🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂🎂

*M*utuwa kam ya dawo musu sabo dan tuni aka fara koke cikin gidan.
Shima kanshi daddy ji yake kamar yayi kukan, idan ya tuna yau kwana uku da rasuwar bawan Allah, 'yar shi kuma ta b'ata, inna ke bashi tausayi dan yasan babu wanda zai kaita shiga damuwa.

Gefe đaya kuma ga Habibullah da ya zamo tamkar marar lafiya yayi yawon neman Bintu har ya gaji.

Tafiyar da ba'a yishi ba kenan a ranar.

Washe gari, ďaukan mudassiru yayan Bintu yayi yace suje garin magaji gidan inna Dije ko can ta tafi.
Daga gurin sukayi ta bin gidajen 'yan uwan Bintu da suka san zata iya zuwa.

Daga baya suka fara shiga qauyukan da ke kewaye da Yusa, inda suka san zata iya shiga.
Har Jambutu, kauyen da goggon Bintu take aure saida suka je, duka dai shiru ba labari.

Har akayi bakwai Bintu bata dawo ba, ba kuma labarinta, inna tun  tana haquri tana nuna kawaici har ta gaza , duk lokacin da ta kalli ɗakin bintu ko wani a bu na bintu sai tayi kuka.
Haka kuma duk shigowan da Habibullah zaiyi cikin gidan sai ta fashe da kuka.

Faɗin irin damuwa da Habibullah ya shiga b'ata lokacine dan har gizo Bintu take mishi.

Ko da yaushe fiskarta yake gani ko tana dariya, ko ta cuno baki yanda ta saba yi mishi.
Wani lokaci kuma har jin muryarta yakeyi cikin kunnuwanshi tana yi mishi magana.

Babu abunda yake ɗaga mishi hankali idan ya tuna ranar da take ce mishi zata bi baffanta, tana so ta je ta ganshi.
Tsoro ne yake shiganshi idan ya tuna da hakan.

Lokacin da tunanin ya fara faɗo mishi saida ya nemi Ilu suka tafi makabartar da aka binne baffa, a tunaninshi ko zai ganta a wajen.

Duk wani gurin da ya tab'a bi da bintu idan yaje sai ya tsaya yayi ta tuna shirmen da ta tab'a tafka mishi a wajen.

Yakan tuna yanda take kama hanunshi ta ɗangale tana lilo.
Duk lokacin da tunani ya faɗo mishi sai ya bi hanunshi da kallo , wani lokacin har yayi ta rike hanun, yana jin kewarta na ratsa shi.

Bayan bakwai sauran mutane suka watse, sosai sukayi ta kukan rashin baffa da na bintu, a ranar goggonayenta da pendonayenta duk suka koma gidajensu.

Mudassiru kawai aka bari da inna dan ya rika ɗebe mata kewa.

Dakyar  Habibullah yarda ya bi daddy ya suka koma da zummar zasu dawo ba da jimawa ba.

Lokacin da suka sanar da mummyn Habibullah ba karamin mamaki tasha ba na auren bazata da akayi mishi, saidai b'atar da akace yarinyar tayi ne yasa bata nuna hakan ba, sai addu'ar da tayi na Allah ya bayyanata.

Masallatai da makarantun Allo daddy yake zuwa ya nemi taimako addu'a Allah ya baiyan bintu , ya kareta a duk inda take.
Saukar Qur'ani yasa ake tayi mata da sadaqa.
Kayan abinci kuwa sosai daddy ya haɗa ya bawa driver aka kaiwa Inna.

Suma can qauyen basu cire tsammani ba, kullum cikin nemanta suke, kowa mamakin b'acewarta yakeyi lokaci guda babu labari, kuma babu wanda ma yace ya ga lokacin da ta fita.

Sati biyu suka qara suka koma, wnn karo har da Mummy da Nafeesa, suka je sukayi ta'aziya tare da jajen b'atan Bintu.

Wuni guda sukayi suka koma.

*1 month later.*

Zuwa wnn lkc Habibullah yaje Yusa yafi a kirga, ya shiga qauyukan da bai tab'a tsammanin zai shiga ba akan Bintu.
Duk da har yanzu bai cire rai da ganinta ba wata rana amma fa ya karaya.
Addu'a kuwa yi yake ba dare ba rana.
Ya zama wani sukuku dashi.
Tun Mummy na mishi fađa har ta gashi ta zuba mishi ido sbd damuwar da ya sa kanshi.

Ko fita yayi idan yaga yarinya kamar bintu sai ya tsaya ya kalli fiskarta, gani yake babu mamaki ya ganta a cikin jalingo ,tunda tace a kwai gidan kawunta a nan.

Computer business center da ya kallafawa rai, yake hana shi karatu, ko yaushe yana wajen ma yanzu ya daina zuwa, ya bar wasu suna kula da wajen.

A da bashi da burin da ya wuce kullunlm ya ganshi yana sarrafa computer, dalilin haka daddyn shi ya buđe mishi wnn gurin, amma daga baya shi kanshi daddyn saida buđewan ya dameshi, sbd yanda ya makalewa gurin ko yaushe yana gurin, baya yarda ko da wasa wani abu ya nisanta shi da gurin, hakan ya sa yaki tsayawa yayi karatu mai zurfi dan a cewarshi abarshi da ilimin computer da yake dashi ma ya isheshi.
Dan bayan ya kammala sec. Sch, certificate yayi a computer, daga nan kuma daddynshi ya buđe mishi business center, har training na wasu sukeyi a gurin.
Saidai a yanzu baya sha'awar ko zuwa wajen computer centern har mamaki daddynshi yakeyi, ashe akwai abinda zai iya đauke hankalin Habibullah daga computer.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Kwance yake kan cushion hanunshi rike da wayarshi yana kallon hotunan da yayi wa bintu a qauye, wasu hotunan ma idan ka gansu sai kayi dariya sbd styles đin da tayi wajen đaukansu.

Wasu kuma kwalliyar da ta cab'awa fiskarta ne zai baka dariya.

Sosai hotunan suka fito kamar a kirata ta amsa.

Kare kallonsu yayi ya koma kan videos.

Muryarta tar tar yake fitowa gata ta fito rass kamar ya janyo daga cikin wayar ya ganta a zahiri.

Kan wani videon da ya mata ya tsaya yana kallo, shine first vedion da ya fara ɗaukanta.
Sanye take da zani da riga na atamfa, ta ɗaura ɗankwali irin ɗaurin asetta ɗinnan, hijabinta kuma ta cire tayi ɗamara dashi.

Waka take rerawa da fulatanci tana rawa, a dole ita tana koya mishi rawa.

D'aukanta yakeyi yana dariya ba tare da ta fahimci abunda yakeyi ba.
Saida ta qare tazo kusa dashi tana maida numfashi take ce mishi ya tashi ya gwada rawan taga ko ya iya.

"Zo ki gani."
Yace mata yana nuna mata wayar.

Zaro idanunta tayi lokacin da ta ganta cikin wayarshi tana tikar rawa, ga kuma muryar ta dake fitowa rass daga cikin wayar.

Baya ta koma da sauri.
"Habibi wani irin madubi ne wnn?"

Ta tambaya tana nuna wayar.

Jin baiyi magana ba ta matso kusa dashi tana leka wayar, still ita ɗin ta gani cikin wayar.

"Amma Habibi mayu ne suka ɗauki kamannina suka shiga cikin wnn abin ko?"
A ina ka sameshi, wa ya baka?"
Ta tambaya da ganinta a tsorace take."

"Waya ce fa islam ba madubi bane."

Matsawa baya tayi tana hararar shi tace "Mannawa kanka hauka, an ce maka ban san waya bane, baffa nama yana da waya fa, wnn qaton abun maitan ne zaka ce min waya?"

"Zo ki gani mana, da gaske waya ce."

Ta bayan shi ta dawo ta tsaya ya sake kunna mata tana gani.

tsalle tayi ta dire.
"Aradun alla, Habibi wnn maitane, yasin nafi qarfinku namana da ɗaci baza ku iya ci ba.
Ta karishe tana cije harshenta .

Dariyar shirmenta yakeyi bai ankara ba ta wafce wayar sai jinta yayi tace "Bismillahi, wa

makarun makaran kubbara."
Wai ita a dole tayi addu'ar mayu.

"Jefawa zan yi a kogi su tafi can suje suci kansu Bintun baffa tafi qarfinsu."

Tana faɗin haka ta ruga a guje ta nufi hanyar kogi.
Ganin da gaske takeyi ya rufa mata baya yana kiranta, haka suka rika gudu.
Sai ya kai hanu zai kamota ta zille , haka sukayi ta zagaye tana ce mishi ya barta ta jefa mayu cikin ruwa.

Dakyar ya samu ya cafkota suka zube a wurin dukansu suna maida numfashi.

Karb'an wayan zai yi ta maidata ɗaya hanu ta b'oye a bayanta, ya sake ta sake maidawa ɗaya hanun."

"Islam ina tausaya miki ne fa, idan karfi zan gwada miki kinsan wayarnan baza tayi second goma a hanunki bako?"

"Kafin ka gwada min karfin bari kaga, da karfinta tayi tsalle.....

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:02 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*45-50*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*J*ifa zatayi da wayar ya yi saurin cafkewa "Ke Islam kina da hankali kuwa?"

"Garau aradu, zan koya musu hankaline, kaima ɗin yanzu ban yarda da kai ba tunda kakeson zama dasu.

"Su wa kenan?"

"Mayun mana."

"kina nufin nima mayenne kenan?"

"Eh, mana kasan ni bana tsoron mayu . Idan nace wa makarun makaran kubbara babu abinda suka isa su min."

"ashe ke zan fara cinyewa kenan."

"Ni, Bintu, yasin nafi qarfin maitanka."
Tana gama faɗa ta sake cije harshenta, ta shiga kwance hijabinta daga ɗamaran da tayi dashi.

Dariya abunnata yake bashi, wai ita a dole ta cije harshenta kada mayu su kamata.

Har ta juya zata tafi, ta fasa ta dawo da baya tana cewa "Aradu bazan cuci Baba alhaji ba, sai na nuna mishi wnn abun mayun yasan abunda kake aikatawa."

D'aga hanunshi mai wayar yayi sama yace "Zo ki karb'a ki kai mishi."

Tsalle takeyi da iya karfinta ita sai ta kwace wayar shi kuma yana mata dariya.

Cire wayar yaji anyi daga hanunshi da gaske, hakan ya dawo dashi daga tunanin da ya lula.

Tashi yayi zaune ya maida kallonshi kanta.
"Sister yaushe kika shigo?"

Shafo hawayen da ya gangara daga idonshi zuwa kunnenshi tayi, bayan ta kalli abunda yake kallo a cikin wayar.

"Habib ashe haka kake? Kana namiji kana yin abu kamar mace, baza kayi haquri ka fawwalawa ubangiji al'amarinshi ba.
Kada ka manta da saninshi komai ke faruwa, shine masanin gaibu, abunda kakeyi bashi zai bayyanata ba, kasawa zcyrka hakuri da dangana, In Allah ya yarda zai bayyanata , mu dai fatanmu Allah yasa tana hanu mai kyau."

"sister baza ki gane bane, ce min tayi fa zata bi baffanta, tsoro nakeji wani lokaci zcyta na raya

min watakila bata raye.  Idan kuma tana rayen akwai abun da nake tsoro ne."

Saida ya ɗan ja fasali yaci gaba da magana.
"Sister, islam tana da wani habit wanda yake bani tsoro, yarinyar nan da kike gani kina tare da ita baza ki ankara ba sai ki hangeta kan machine ko cikin mota, bata da tsoro sam, a hakan sai ta bisu taje wani qauye ta dawo, ina gudun ta faɗa motar mugaye su cutar da ita, yanzu Allah ne kaɗai ya sani ko tana raye ko bata raye."
Ya qarasa maganar cikin karaya.

"Hakuri zakayi Habib muna nan muna addu'a Allah ya bayyanata, dan Allah ka rika cin abinci ko zaka yi kyan gani, rayuwa baza ta tafi a haka ba."

"Na gode sister, ina yaran?"

"Suna wajen mummy, dama na shigo in duba ka ne na tarar da kai kwance kana kuka kana murmushi."
Ta karishw maganar tana murmushin yake, dan sosai damuwar ɗan uwanta yake damunta.

Tare suka shiga wajen mummy suka haɗu da yaran akayi ta chapter, sai bayan isha'i ta koma gida.

Sosai suke kokarin ganin ya kwantar da hankalinshi, daga daddy Mummy har Nafeesa, shi kanshi addu a yakeyi Allah ya kawo mishi sauqi a cikin lamarinshi.
Dan shi kanshi bazai iya cewa ga takamammen abunda yakeji game da ita ba, kawai dai yasan yana azabtuwa da rashinta.

Akai akai suke zuwa yusa, kuma har yanzu basu bar nema ba kamar yanda dangin  Bintu ta gefen uwa da uba basu daina nemanta ba.
Kayan abinci kuma ko wani zuwansu sai sun loda ma inna har itama tana bawa makwabtanta.

Duk da yana kokarin hana kanshi damuwa tunaninta nanan cikin ranshi, ranaku ɗaɗɗaya ne kuma zai kwanta baiyi mafarkinta ba.

A kwana a tashi ba wuya, b'atan bintu ya kai wata biyar yanzu.

Yanzu haka sunje qauyenne kamar yanda suka saba, saidai da drivernsu suka je sbd shiga kauyukan da sukeyi idan sunzo yasa daddy ya bada shawarar su dinga zuwa da driver.

Gurin bishiyoyin yazawan da take maitan hawa a ko da yaushe yaje ya tsaya, hanunshi soke cikin aljihunshi.
Kallon bishiyoyin yakeyi ɗaya bayan ɗaya.
Gani yake kamar zai hangota saman ɗaya daga cikin bishiyoyin.
Ya jima yana tsaye a gurin har ya gaji dan kanshi ya kamo hanya ya dawo gida

Kasan bishiyan mangoro da suke zama nanma ya tsaya yana tunanin abubuwan da suka wuce, wnn karon tunanin ba nata ita kaɗai ba har da na Baffanta.
"Indo da Hure ne suka fito daga gidan inna suna sharar kwalla ya bisu da ido. Dan suma duk lokacin da suka shiga wajen inna sai sun fito da kuka.

Binsu yayi da kallo har sun ɗanyi nisa sai ya bi bayansu da sauri, sunayensu ne bai rike ba sbd haka sai ya ɗaga murya yace "Sannunku."
Tare suka juya suka kalleshi, indo ce tayi karfin halin ce mishi

"Sannu Habibi."
Wani iri yaji dan ya jima ba a kirashi da sunan ba sai yau.
Murya a shaqe ta gaisheshi itama Hure ta gaisheshi
Rasa abunda zai ce musu yayi kawai sai yace musu ya gode su gaisheda mutanen gida.

Yana tsaye yana kallonsu har suka b'acewa ganinshi,
Sabuwar damuwa ne da tunani suka shige shi hakan yasa shi kasa barin gurin

Yana nan tsaye har Ila ya zo ya tadda shi.
"Habibu yaya ka tsaya anan kai kaɗai."

Cikin sanyin jiki ya kalleshi na ɗan lokaci kafin yace "Ila, anya Islam tana raye kuwa?"

"Haka muke fata Habibu, zo mu shiga   ciki."
Ya faɗa da niyar basar da zancen.

D'akinsu na cikin gidansu da daddy ya shiga shi kuma Ila ya shiga gidansu da niyar yin wanka.

"Islam, ina kika shiga?
me yasa kika tafi?
Ina kike yanzu?
Yaushe zaki dawo garemu?
Dani da inna muna muna buqatarki Islam ki tausaya mana ki fito.
Bana fatar ya zamo kin bi baffanki da gaske kamar yadda kike faɗa.
Allah yasa kina raye islam.
Allah ya bayyana mana ke cikin koshin lafiya."

Surutan da yake tayi kenan shi kaɗai wanda sha a tunaninshi zancan zuci yakeyi, saida yaji drivernsu ya amsa da amin kafin yasan cewa a bayyane yayi maganar.

A sanyaye ya tashi ya shiga wanka.
Yana fitowa yayi arba da Ila dake zaune yana jiranshi.
Kafin yayi magana Ila yace .

"Habibu nazo da wata shawara."

Kusa dashi ya isa ya zauna yana kallonshi "Wace irin shawara Ila?"

"Akwai wani qauye dake ta cikin kunini yana gaba kaɗan da kuni gurin da muka je kwanaki, duk da dai zaiyi wuya ace ta shiga wajen dan qauyen yana ciki sosai ne, ko za mu gwada dubata a wajen."

Cikin zafin nama ya mike, tashi muje Ila, daga can ma zamu tambaya idan akwai wani ta ciki duk zamu shiga.

"Amma da ka bari sai gobe muyi sammako Habibu dan qauyen yayi ciki sosai, nima kaina ba sosai nasan qauyen ba, sau ɗaya na tab'a raka wani abokina yakai aika.

"Muje kawai idan ya kama kwana ma zamuyi a wajen. Ko a cikin mota sai mu kwanta idan yaso goben muci gaba da nemanta.

Hakan ko akayi suka kama hanya, Driver da Ila a gaba dan ya nuna mishi hanya , shi kuwa Habibullah yana baya, sai kallen kallen hanya yakeyi ko Allah zaisa ya hango ta.

Quarter pass four suka shiga cikin qauyen, basu b'ata lokaci ba wajen fara cigiya tun daga farkon qauyen.
Har suka shiga ciki, saidai duk tambayar da sukayi sai a ce musu ba a san wata mai suna bintu ba.

Daga baya gidaje biyu aka kaisu aka nuna musu wasu masu suna bintun amma sai suka ga ba ita bace.
Sun kare duk kwatancensu sai a ce musu ba a ganeta ba.

Tambaya sukayi aka nuna musu wani qauye kusa dasu, nanma suka shiga kusan magriba.

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:04 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*50-55*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*D*rivernsu ne ya tsaya ya fita yaje yin fitsari. Ila zaune a gaban mota yana jiran dawowarshi.

Shi kuwa Habibullah fitowa yayi ya jinginu da jikin motar ya harɗe hannayenshi yana bin ko ina da kallo.

Kamar a cikin mafarki ya hango mai kama da Bintu ɗauke da kirare a kanta.
Sanye take da wasu koɗaɗɗun kaya ta ɗaure itacen da hijabinta.
Saidai wnn baqa ce, kuma tayi rama da yawa.
Tafe take tare da wata yarinya kusan kansu ɗaya, itama kiraren ne a kanta, saidai da alama masifa mai kama da Bintun take suburbuɗawa ɗayar.

Goge idanunshi da yaji kamar suna mishi dishi dishi yayi , ya runtse ya kuma buɗe su.
Suna daɗa matsowa kamannin bintu yana bayyana a jikin yarinyar.

Runtse idanunshi ya kuma yi ya buɗe, ya sake goge su a karo na uku.

Tabbas wnn muryar bintu  yakeji take zuba surutu da tsattsamar fulatancinta.

Kamar ance ta ɗago kai, tana ɗagawa taga wanda bata zata a yanzu ba yana tsaye ya kafe ta da ido, ko a bacci aka tashe ta ko cikin magagi babu abinda zai hana in ta ganshi ta ganeshi.

Cakk ta tsaya tana kallonshi kamar yadda shima yake kallonta. Ko maganar da abokiyar tafiyarta take mata bata jinshi.

Gizo take min ko mafarkin da na saba ne.
Ya faɗa cikin ranshi.

Jifa tayi da kiraren da ke kanta ta nufe shi da gudu.

"Habibiii."
Ta faɗa daidai lokacin da ta rukunkumeshi.

Marin fiskarshi yayi da kyau yana jin kamar ba a gaske bane.
Fiskarta ya ɗago ya kalleta da kyau kafin ya rungumeta sosai kamar zai maida ta ciki.

Bai ankaraba sai jin hawaye yayi suna sintiri kan fiskarshi.

"Habibi, wa ya faɗa muku ina nan?"
Ta fada cikin kuka.

Share fiskarshi yayi kafin ya ɗago fiskarta yana share mata hawaye.

Cikin wani irin murya yace "Islam, ashe zan ganki?"

Ila da tun da ta iso gun ya fito daga motar yake kallon ikon Allah yayi saurin cewa "Alhamdulillahi, Habibu ku shiga muje kawai."

"Ma sha Allah, driver ma ya faɗa cikin farin ciki dan tunda ya iso ya gansu rungume da juna ya gane itace suke nema.

"Bintu to njata?"
(Bintu ina zaki je?")

Suka tsinkayo muryar abokiyar tafiyarta tana fada lokacin da taga zata shige cikin mota.

"Yauwa tsaya Habibi ku jirani ina zuwa."

Tace tana fasa shiga.

"Jira a ina? Common get into d car."
Cewar Habibullah ya na maida ita.

"Yauwa ka tunamin zamu ci gaba da karatunmu ko Habibi."
Ta fada tana shigewa fikin motar.

Shiga tayi ta zauna kafin tayi kwafa "Da ka barni na je na sameta ai ta faɗi yaren garinsu."
Sai ta qara da cewa.

"Yaya Ila ko waɗi on yeccai yam on warai heb'a mi tappa Fa'i ɗo ba mo wujji mota."

(Yaya Ila ya baku faɗa min zaku zo ba samun in daddaki Fa'innan kamar wacce saci mota."

Dariya Ila yayi yana tambayar ta me tayi mata, lokacin har sun fara tafiya sun bar yarinya sake da baki , saida taga sunyi nisa ta ruga da gudu tayi cikin gida tana ihun an sace bintu.

"Hmm, Nafikijo on "
(Munafukace.)

Ta bawa Ila amsa. Kafin ta ci gaba da cewa "Yaya Ila ina su inna ta  su yakumbo, (Mamanshi)
Su Nenne Abulle adda Muna."
Sai jera mishi sunayen mutane take tayi.
Shi ki yana ta amsa mata sunanan cikin tsan tsan farin cikin sa'ar samunta da sukayi.

Tallabe hab'a yayi yana kallonta , a ranshi yana tuna babu a bunda ya ragu a halinta na surutu.

Kallonshi tayi taga yanda ya kafe ta da ido ta rufe fiska tana dariya.

Hannayen duka biyu ya rike yana kallonta .
"Islam me ya kawo ki nan ?
Ya kika yi kika zo?."

Juya idanunta tayi tace "Ance maka ni na kawo kaina  ne, nima kawo ni akayi."

Wa ya kawoki?"

"Ba goggo na bane tasa yaronta ya kawoni."

Cikin mamaki yace "Wace goggon ?"

"Goggo Rabi mana."

"Ila, ba da matar nan akayi ta neman islam ba, kusan ma tafi kowa nuna damuwa a wajen, kana ji kuma wai ita ta ɗauketa."

"Nima kam abun ya bani mamaki Habibu."

"Hmm, lallai sanin zcyr  mutum sai Allah, to nan ɗin gurin wa ta kawoki?"

"Ba fa ita ta kawoni ba , yaya yunusa tasa ya kawoni gidan wata mata Innawuro, wai kawartace, tunda nazo gidan tace ni zan rika dafa musu abinci , da nace mata ban iya ba, tace haka zan koya wai idan nayi aure wa zai dafa min, har da shara da wanke wanke ɗiban ruwa, da ɗebo itace duka inayi, kuma kasan waye mijin?"

"Um, um."

"Ka sani mana Habibi, ba ranar na faɗa maka ba, yaya yunusa ne fa, shima yana zuwa wai gurina yake zuwa, yana kawo min kayan kwalliya da man shafawa har da turare, ka san me

kuma?  Innawuro bata barina nayi kwalliyan sai yaya Yunusa yazo wajena sai inyi wanka inyi kwalliya ta fesa min turare mai kamshi ."

Haushi ne da takaici suka hađu suka mamayeshi, idan ba jahilci ba tana sane da aurenshi a kanta take turo đanta zuwa zance wajenta.

"Wai ma idan yazo wajenkin me yake ce miki."

"Kaga idan yazo, gaisheni yakeyi, sai yace goggona tana gaisheni, kuma sai yace min, innata ma tana gaisheni. Wai tace inyi haquri wasu mutanene suke so su sace ni shi yasa aka kawoni nan aka b'oyeni, idan sun gaji da nema na sun daina zuwa za a maida ni sai muyi aurenmu, na haifa mishi kyawawan yara kamar ni."

"Shut up."
Yace a tsawace saida ta razana.

Hakan kuma bai hanata cewa "Kaima shatap."
Qasa2 ba.

"Wai haka idan yazo kike zuba mishi surutu."
Ya tambaya yana tsattsareta da ido.

Kawar da kanta tayi tace "Amma dai kaima Habibinnan, an ce maka bani da kunya ne, ance maka idan ana zance ana kallon juna ne? Haka nakeyi , kalla ka gani."

Juya baya tayi ta bashi Qeya taja đankwalinta tana rufe fiska, tace "Haka akeyi, idan mutum yace yana sonka sai kayi ta b'oye fiska, idan banyi haka ba ai sai a ce bani da kunya, kuma ma wa yake yiwa mijin da zai aura rash.. ."

"Ke ya isheni haka."
Ya dakatar da ita cikin b'acin rai.

Ila da driver sai dariyarsu sukeyi, shi yake tambaya idan ta bashi amsa kuma yaji haushi.

Zumb'ura bakinta tayi ta maida kallonta waje, tana ta kunkuni.

Shiko banda tafasa babu abinda zcyarshi keyi, fađi yake a cikin ranshi lallai matar nan bata da hankali, a tsammaninta zai gaji da neman Islam ne ya haqura kenan ta aurawa đanta .

'yar qaramar tsaki yaja ya kuma cewa "To waima tayaya kika fita daga gidan har kika tafi babu wanda ya ganki?"

Banza ta mishi tamkar ba da ita yake ba.

"Islam ba ki ji ne?"
Nanma ko kallonshi bata yi ba.

Matsowa yayi kusa da ita ya kama fiskarta ya juyo da ita ta fiskanceshi "Ina magana kin min shiru baki ji na ne?"

Kwace fiskarta tayi ta sake juyawa.

Kamo fiskar ya sakeyi yana kallonta , yanda ta haɗe ran sai yaso ya bashi dariya ya dake.

"Kina so ki sha mari ko?"
Shafa fiskarta tayi, kamar ya riga ya mareta ɗin ta kalli fiskarshi  taga yanda ya haɗe rai, cikin rawar murya tace "To me nayi?"

"Baki ji tambayar da nayi miki ba?"

"To, to, ba itane ina bacci da daddare a ɗakin baffana taje tasheni tace in zo zata aikeni, shine nace mata zan faɗawa innata sai tace min, innata tayi bacci idan na tasheta kanta zaiyi ciwo, shine ta kaini waje wajen yaya yunusa tace na hau machine ɗinshi in bishi zan karb'o mata saqo ne, shine da na hau kuma sai ya kawoni nan."

"Ila kaji ko, tsabar munafurci dare dare ta sa aka tafi da ita kuma tafi kowa nuna damuwarta."
 Ya faɗa cikin tsantsar jin haushin matar kamar ya ganta alokacin ya gaggaura mata mari.

"Habibu ni ina tunanin ma da ba don ya kamata innarta tasan an ganta ba, da wucewa zakuyi kawai kada kowa yasan an ganeta."

"Yanzunma za mu iya yin hakan Ila nasan idan mun roki inna bazata bayyana maganar ba."

"Hakan za a yi."..


*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:05 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJ*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀


*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*55-60*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*C*ikin kunini sukayi sallar magriba da Isha'i.
Daga nan suka sayo balangu da minerals.

Kin ci Bintu tayi ita a dole tana fushi da Habibinta.
Saida ya haɗa da rarrashi, nanma saida Ila yasa baki snn ta yarda ta fara ci.

"Amma Habibi wnn ba naman akuya bane ko?
Nifa bana cin naman akuya idan naci tayar min da saɗaure yakeyi."

"Ba shi bane Islam."

"Kace aradu."

"zan miki karyane."

"Na yarda to, amma fa naman nan kamar yaso yafi na wuro magaji daɗi kaɗan."

"Kina cin balangun wuro magaji ne?"
Ila ya jefo mata tambaya.

"Sosai yaya Ila, sai kaji daɗi kai mutuminnan ya iya gasa nama, da wuta fa yake gasawa."

"Dariya suka sa mata dukansu."
Habibillah yace "Dama akwai inda ake gashi da ruwa ne?"

"Oho, na sani? Yaya Ila inajin harda Kafi zabuwa aka daka yajinnan."
Ta faɗa tare da jefa tsokar nama bakinta.

Ta bayanta Habibullah yakai hanunshi ya tareta yana dariya, "Ila ba sai ka bata amsa ba na sa mata waigi."

"Habibu kasan abinda ya ban dariya ?"

"Sai ka faɗa Habibullah yace."

"Wai fa tace bata cin naman akuya, kuma naga naman akuyar suke sayarwa a garin magajin."

Da sauri tace " Hunu a viya   aradu yaya ila."
(Rantse Kace aradu)

"Hakkunde am be Allah."
(Tsakanina da Allah.)
Ya bata amsa.

"Kai ammafa Dauda ya cuceni, amma na yafe mishi."

"Duk dai ke kaɗai."
Habibullah yace.

Tsula gudu suke tayi yayin da Bintu ta fara Hamma alamar bacci zatayi.
Can ta fara gyangyaɗi.

Haskata Habibullah yayi da wayarshi yace "Islam Bacci."

"A'a nikam ba bacci nake ba inajin duk abinda kuke cewa."

"To me akace yanzu."

"Nidai na sani ba sai na faɗa ba."
Ta faɗa tana qara zuba Hamma.

Sai qarfe 9:47 suka isa qofar gidansu Islam, lokacin tayi nisa da bacci.

Dakyar ya tasheta ta tashi suka fita daga cikin motar, tana tambayarshi wai sun iso ne?
kofar gidan suka nufa tana ta murza idanunta.
Su Ila ko gidansu suka nufa suka barsu anan dan basu so hankalin mutane ya dawo garesu.

"Sallama ya kwaɗa, daga ciki Inna ta tambaya waye.

"Habibullah ne inna."

Cikin sauri ta taso tana cewa "Allah yasa dai lafiya.

"Inna buɗe Bintuce."

Bintu ta fada cikin zumuđin jin muryar innarta.

Ai inna har tuntub'e takeyi wurin zuwa buđe kofar tana fatar Allah yasa abunda taji da gaske ne.

Tana buđewa Bintu ta fad'o jikinta ta kankameta.
"Bintu ase zan ganki?
Ashe kina raye."
Inna ta fađa cikin kuka.

"Inna mu shiga daga ciki."
Cewar Habibullah.

Ciki suka shiga bintu na maqale jikin innarta.

Har cikin đakin inna suka shiga suka zauna "Habibu ina ka samota?"

"Can wani qauye inna ni banma sunan qauyen ba."

A tuni Bintu ta amshe zancen ta fara zubawa inna bayani, nan ta sanarwa inna cewa goggontace ta sa aka kaita qauyen, da zuwan yunusa da duk karairayin da yake shera mata.

Daga baya kuma ta shiga tambayarta labarin 'yan uwanta da qawayenta.

Sosai Inna tayi mamakin goggo Rabi, "in ba rashin hankaliba yarinya da aurenta ki đauke ta ki b'oyeta?"

"Inna waye me auren?"
Bintu ta tambaya.

Basar da zancen tayi da cewa "Sannu Habibu Allah ya maka albarka, Allah ya biya maka buqatun ka sannu da kokari."

"Amin, inna nagode."

"Inna dama nace ko gobe zamu wuce da islam đinne, kuma in so samu ne kada kowa yaji har sai goggon tazo a ji abunda zata ce game da rashin ganin bintun."
Ya fađa yana sosa tsakiyar kanshi.

"Babu komai Habibu, duk yanda kayi daidai ne, amma sammako zakuyi ko?"

"In sha Allah."

"Habibi Ina zaka kaini kai kuma?"

"Gidanmu zan kaiki gurin Baba alhaji."

Cikin murna tace "Harda Baffana ma zan gani."

tausayinta ne ya rufesu dukansu kafin inna tayi magana Habibullah yace "Islam, wanda ya riga ya mutu baya dawowa, addu'a zamu bishi da ita, dan itace gatanshi a yanzu kinji."

A sanyaye ta gyaɗa kai ta tashi ta fita daga ɗakin inna, duk sun ɗauka wani abin zatayi sai ji sukayi ta tura kofar ɗakin Baffanta ta shiga .

Kallon inna yayi itama shi ɗin ta kalla.
A sanyaye ya mike ya shiga ɗakin ya sameta ta haɗa kai da gwiwa tana kuka.

"Yanzu bazan sake ganin baffana ba?"
Ta tambaya lokacin da yaɗago kanta yana share mata hawaye.

"Kiyi haquri Islam, ki kwanta kiyi bacci kinsan gobe sammako zamuyi."

"Da innata zamu je?"

"A,a zamu fara zuwa dake in yaso daga baya inna ma taje, kuma har makaranta za a saki a can kiyi karatunki yanda kikeso."

Zaro ido rayi tana murmushi "Kace aradu Habibi."

"Allah da gaske nake, kiyi karatunki, gaki ga Habibi ga kuma Baba alhajinki, kuma harda wasu sabbin qawaye ma zaki samu."

Saida yaga ta saki ranta har tana dariya snn ÿa fita daga ɗakin yana mata saida safe tare da jaddada mata ta kwanta ta huta.

Inna ko har ranta tana jin daɗi tare da godewa Allah da hukunta Habibullah ya zamo miji ga Bintu, dan ta lura shi zai iya da shiriritarta, sosai take jin daɗin kulawar da yake bata.

Haɗa kayanta inna tayi itako har ce mata tayi ta haɗa mata da litatafanta, na koyon haɗa bakin hausa da na english wanda Habibi ya saya mata, tana kuma jaddada mata a saka mata kayayyakin da baffanta ya ɗinka mata.

Da asubah inna ta tasheta tayi sallah, tana idarwa ta kai mata ruwan wanka da ta surka da ruwan zafi.

Kokon da ta dama kawai suka sha suka kama hanya tun gari bai gama wayewaba.

Daddy Habibullah ya kira yace mishi yana zuwa da wani surprise kada ya fita.
Tun bai faɗa ba jikin daddy ya bashi anga Islam, sbd haka farin ciki ne ya mamayeshi ya zauna zaman jiran isowarsu.

Tun daga bakin gate Islam ta saki baki da Hanci tana kallo har aka wangale musu gate suka shiga.

Fitowa daga cikin motar ma aiki ne, a take taji tsoro ya shige ta, saida yayi da gaske ta yarda ta fito.

Rike hanunta yayi suka nufi cikin gida, itako babu abinda takeyi sai bin harabar gidan da kallo baki sake.

A tsorace take gaba ɗaya ko magana ta gagara yi har suka isa kofar palourn mummy.
Sallama yayi mummy ta amsa.
Da gudu ya idasa shiga palourn ya rungume mummy yana cewa "Ku tayani murna mummy na ganota."

Wani dumm mummy taji, sbd haka ta fara sassauta rikon da tayi mishi, tana kakalo murmushi yake.
"Congrats son, ina take?"

"Kuttuse, aradu da wayona ba za a cuceni, yusa daret no gargada zan koma."
Bintu ta faɗa daidai lokacin da ta leko da kanta cikin  falon.
Shi kuma alokacin ya juya dan nunawa mummynshi ita dan shi duk a tunaninshi tana biye dashi a baya.

Da gudu ta kwasa iya qarfinta tana mai burin ganin ta bar gidan.

Da sassarfa ya biyo bayanta yana kiran sunanta, ganin da gaske takeyi ya sashi fara gudun shima yana cewa Bala mai gadi ya rufe kofa dakyau kada ya barta ta fita.

Daddy da ya fito ya hangota a guje, kafin yayi magana yaga Habibullah ya take mata baya shima agujen.
Dariya yayi yana cewa "Aiki ya sameka Habibullah."

Saman gate ɗin ya sameta ta haye sbd samun shi da tayi a kulle,  kara hawa gate ɗin takeyi kamar 'yar biri dan niyyar dira ta baya takeyi, taji ya cafkota.

Wani irin gigitaccen qara ta saki wanda ya tilasta Bala toshe kunnuwansa.

"Ka sakeni, ka sakeni take cewa  tana ta mutsu da harba kafafu.

" Ki nitsu mana Islam."
Ya faɗa a tsawace.

Fashewa tayi da kuka tana cewa "Aradu na gano wayonka. Yasin komawa yusa zanyi bazan shiga wnn guri ba, dama shi yasa goggona ta b'oye ni dan ta gano ka na so ka sace nine ka kawo ni gidan yankan kai, Wamakaru makaran kubbara, Wallahu gaalibun alaa amrihi." addu'oi ta shiga jerawa duk wanda yazo bakinta yinshi takeyi tun bata qarasa ba sai ta cafko wani....

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:07 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*60-65*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*W*a ya tab'a min Bintun Baba, Habibullah kaine ko?"
Ta tsinkayo muryar Baba Alhajinta.

Cakk ta tsaya da kukan kamar anyi ruwa an ɗauke.
Ta kuma bar buge bugen da takeyi.

Ganin haka yasa Habibullah sauqeta tako dira da sauri tana kallon Baba alhajin.
Share fiskarta ta shiga yi tana smiling.

"Baba alhaji dama nan gidanka ne?"

"Gidanane Bintu yanzu kuma ya zama gidansu Bintun baba ko?"

Dariya tayi ta riko hanunshi tace "Ni na zata gidan yankan kai ya kawo ni aradu, kuma da da qafa zan koma yusa, nasan zan gane hanya , kuma idan na fara gudu daga nan bazan tsaya ba sai na ganni cikin gidanmu, kasan mufa ance mana ana satar mutane a cikin gari irin wnn."
Tana maganarne suna ci gaba da tafiya har suka iso kofar falon.

Ganin tiles shimfiɗe sai walkiya sukeyi ya sata fara ɗangale kafa tana tafiya cikin sanɗa.

"Yaya Bintu muje mana.
"Zamewa zanyi babana, muje a hankali."

Dariya yayi yace "Baza ki zame ba muje."

Duk wnn abunda sukeyi Habibullah na biye dasu a baya.

Suna isa tsakiyar falon ta taka center carpet taji uban laushi, cikin sauri ta dab'ashe a gurin.

"Yaya haka Bintu, karasa ki zauna kan kujera mana."

"Nanma yayi babana."
Ta faɗa tana danna lallausar carpet ɗin da yatsunta.

Kamota yayi yace "zodai ki karasa."
Ya faɗa yana kamo hanunta tare da mikar da ita.

Mikewan tayi ta bishi har gurin kujeru, ta tsaya tana binsu da kallo.

Kusa da Habibullah taje ta ɗosana tana kallonshi tace a hankali "Idan kaga zan zunduma ciki ka riko ni Habibiii."

Bai tankata ba saida yaga ta zauna shima a hankalin yace "Ki zunduma mana ina ruwana."

Kwafa tayi ta maida kallonta gurin baba alhaji tace "Ina kwana babana."

"Lfy lau bintun baba ya kika baro  innarki?"

"Habibii ba tace maka ka gaisheshi ba kayi shiru kana ji yana tambaya."

"To kuma ni ya tambaya ne?"

Bata tanka shi ba sai maida hankalinta da tayi kan mummy "Sannu Hajjajo ina kwana?"

Mummy da ta saki baki tana kallon ikon Allah tace "Sannu 'yanmata."

"Innata tace Habibi ya gaisheku shi kuma yayi shiru bai faɗa ba."

"Muna amsawa."
Suka ce Daddy ya qara da "Mungode."

"Habibu ina aka ganota ne, ashe da rabon zamu sake ganinta."

"Wai dama b'arayin haka suka ce muku baza ku sake ganina bane?"
Ta tambaya tana binsu da kallo."

Daddy da bai fahimci zancen ba yace "B'arayine suka saceta habibullah?."

"Baba alhaji nifa ba b'arayi ne suka sace ni ba, goggona ce ta b'oyeni dan kar b'arayi su saceni. Kasan abinda yasa nayi tambaya?"

Um um, daddy yace yana kallonta.
"Kaga lokacin da Habibi ya ganni can qauyen da goggo ta b'oyeni, sai naji yace "Ashe zan ganki islam."
Ta faɗa tana kwaikwayon muryarshi.
"Snn Innata ma da ta ganni tace ashe zan ganki Bintu."
Itama ta kwaikwayi muryarta.
Da ci gaba da cewa "gashi kaima kace ashe da rabon zaku ganni, shine nayi tsammanin ko dama b'arayin sunce muku baza ku ganni bane."

Kwaikwayon muryoyinsu da tayi ne ya basu dariya, shi kuwa habibullah kokarin gimtse dariyar yakeyi dan Ya nuna mata fushi yakeyi da ita sbd haka sai ya wayance da cije leb'enshi na qasa .

"Bintun Baba yau kin dawo gidan babanki da zama ina fatar kinyi farin ciki."

Gyaɗa kai tayi tana washe haqora.
"To kuje mummynku ta nuna miki ɗakin da zaki zauna sai kiyi wanka kizo ku karya ki huta , kafin su Miemie da Iman su dawo ko?"

Kallon juna suka shiga yi ita da mummyn, sam ita hankalinta bai kama mummynnan ba, ga dukkan alamu haka abun yake a gurin mummyn ma.

Ita ta fara kawar da kanta ta maida kallonta ga Habibullah dake danna wayarshi tamkar baisan wainar da ake toyawa ba.

Wai magana zata yi mishi bata kuma son aji, maimakon ta kai bakinta kunnenshi sai ta haɗa

kunnenta da nashi tace a hankali "Ni bazan bi hajjajonnan ba ka faɗa wa Babana."

Abunda tayinne ya bashi dariya, ita a dole wai tayi sirri.

Yana murmushi yace "Ke ki faɗa mana baki da bakine?"

"Habibullah tashi ka nuna mata ɗaskinsu Iman ka nuna mata komai idan tayi wanka kuzo ku karya."

Mikewa yayi itama tayi saurin mikewa tana kallonshi.

Hanyar upstairs taga ya nufa hakan yasa ta zaro ido.

"Yau akwai rikitowa a gidannan."
Ta faɗa kasa2.
Yi yayi kamar bai jita ba yaci gaba da tafiya.

A tsorace take binshi har ya fara hawa stairs ɗin.

Ganin bai kulata ba yasa tayi saurin binshi.
Ta taka step ɗaya ta kara na biyu na uku sai kawai sunkuya ta fara rarrafe tana magana ita kaɗai "Yasin bazan yi sake jiri yq kwasheni ya zubar a wnn waje ba, inji ciwo innata batanan, baffana kuma ba dawowa zaiyi ba balle ya ce min sannu bintuna Allah ya baki lafiya."

Jin kananan mita yaqi qarewa yasashi waigowa yaga me take yiwa mita, aiko ya ganta ta daddage sai rarrafe takeyi.
Kallo su daddy yayi yaga hankalin su baya wajen taɗinsu sukeyi.

Dawowa yayi daga baya yana cusa wayarshi cikin aljihun jeans ɗinshi, ba tare da yayi magana ba yasa hanu ya ɗauketa cakk ya kama haurawa da ita.
Itako sai zare idanu takeyi har saida suka shiga ɗakin ya dire ta tare da dangware mata goshi.
"Gaki da baki sai shegen tsoro."

"To ba jiri ne zai kama ni ba, ta faɗa tana rike kanta.
Sai kuma ta saki murmushi .
"yasin Habibi akwai ka da qarfi, ji yanda ka ɗauke ni kamar wata bebin roba, kama rainani aradu."

"Ni na raina ki ko, gud, ci gaba da qara wa kanki laifi."

Waro idanunta tayi tace "Dama akwai wanine?"

"Me ɗin?"

"Laifin."

"Ina zaki sani Islam, ba dai ni kika cewa ɗan yankan kai ba, wato baki yarda da ni ba kenan."

Iangab'e wuyanta tayi tace "Kayi haquri ka yafe nima na yafe aradu."

"Akwai aukin yafiya da bada haquri kam, ni ki shiga kiyi wanka ina da abin yi."

" A ina zanyi wankan?"
Ta tambaya tana ninke ɗankwalinta da ta cire.

Kofar toilet ya tura ya buɗu ya nuna mata da hanu.
Wani irin yatsina fiska tayi "Idan ba kazanta ba bayangida a cikin ɗaki."

"Idan baza kiyi wankan ba zan tafi fa."
Nufan bayin tayi ba tare da ta amsa ba.

Tana shiga ta fito da sauri tana yarfe hanu.
"Mene ne kuma?"
Ya tambaya yana kure ta da ido.

"Ni kam dai na shiga uku Habibi har cikin gurinma da wnn abun sa zamewan."

Ya fahimci tiles take nufi, sbd haka yaje ya riko hanunta ya shigar da ita ciki, ya fara nuna mata yanda zata yi amfani da shower, ga kuma bath tube , yanuna mata soso da sabulu duk tana tsaye tana kallonshi saida yazo fita ta riko rigarshi ta marairaice fiska "Nikam Habibi ka kaini bayangidan waje mai yashi."

"Mu kam bamu dashi."

"To na fasa wankan."

"Haba daii."
Ya tambayeta cikin salon rainin hankali.

"Aradu."
Tace cikin dakewa dan ta tabbatar mishi da gaske takeyi.

Bai kara mata maganaba sai jawota da yayi ya kunna shower daidai kanta ,bata ankaraba taji sauqar ruwa a kanta.

Wani irin zabura tayi har numfashinta yana faman ɗaukewa.

Ganin haka yasashi saurin kashewa.

Dogon numfashi taja kafin tace "kasheni zakayi Habibi."

"Sorry yi wankan to."

"Mi sorata ."
Tace tana murguɗa baki.
Dariya yayi ya fita ya barta a gurin.

Mota ya koma ya ɗauko mata kayanta ya shigo dashi ya samu bakin gadonsu Iman ya zauna yana jiran fitowarta kunnenshi makale da earpiece.

Fitowa tayi tana Zumbura baki ɗaurin kirji tayi da towel ɗin da ya nuna mata "Ina kayana?"

Hanunshi ya mika mata ta matso kusa dashi, jin baice komai ba ta ɗaga muryarta tace da qarfi "Ina kayana Habibi, sai kuma tayi qasa da murya "Kai in kasa wannan cegen abin a kunnenka kurmancewa kakeyi.

Jawota yayi ya ajiyeta kusa dashi yasa hanunshi ya zare earpiece ɗin kunnenshi ɗaya ya saka mata a kunnenta.

Tab'e baki ta shigayi  jin american music da yake tashi ta cikin earpiece ɗin.

Mikewa tayi tana zare earpiece ɗin daga kunnenta ta zare na kunnenshi tana kallonshi, a masifance tace "Dama shirmen da kakeji a wnn abun kullum kenan? Shirme zalla, wani Tori ma torii, Kanshika kanshika ,kanshika."
Wai ita a dole wakar da taji takeyi..

*Aunty Ruqayya ce 🥀*
[7/31, 11:08 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers.*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*65-70*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*K*arb'e earpiece d'in yayi daga hanunta yana gimtse dariyarshi.

"Nikam ina kayana nace."
Ta fad'a fiska a had'e ita a dole ya bata haushi.

Da hanu ya nuna mata inda ya ajiye jakar kayan yana maida earpiece ɗin kunnenshi.

Kayan shafanta ta fara fitowa dasu, ta fara da shafa mai tana satar kallonshi.
Kamar baya cikin ɗakin dan ko alama bai nuna yana kallonta ba.

Tana gama shafa man ta shafa powder ta ɗauko kajal ta zizara tana kallon fiskarta cikin 'yar karamar madubin da ta rike.
D'igeɗigenta tayi a fiskarta snn ta shafa jan janbaki.

Kayan sawanta ta fito dasu ta ajiye a gefenta kamin ta juya ta kalleshi.
Duk da taga ba kallonta yakeyi ba sai da tace "Ka fita zan sa kaya."

Bai kulata ba saida ta qara maimaitawa ya juyo gaba ɗaya yana kallonta.
"Rike ki nayi da zaki ce sai na fita zaki sa kaya?"

Cuno bakinta tayi wanda yasha jan janbaki tace "Ni dai ka fita kawai ehen."

Tana ganin ya mike tace "Amma dai kar kayi nisa ka barni ni kaɗai in rikito fa daga saman nan."

Bai tankata ba sai nufota da yayi yana kaɗa kanshi irin kiɗa yayi daɗinnan.

D'ankwalinta ya ɗauka ya goge ɗige ɗigen da tayiwa fiskarta da janbakin, ita kuwa sai kawar da fiskarta takeyi tana hararashi.

Janta yayi gaban dressing mirror dake ɗakin ya fara gyara mata fiskar.

Sakin baki tayi tana kallon kanta a madubi.
Saida ya gama tace "To ina jan baki na?"

Ba tare da yace komai ba ya ɗauko wetlips ya shafa  mata a leb'enta, snn ya ɗauko body spray ya fesa mata.

"Wash Sanyi Habibi."
Tace tana kankame jikinta.
Sai kuma ta lumshe idonta tana jan numfashi tace "Kamshiii."

"Wuce kisa kayanki mu fita yunwa nakeji."

Kallon shi tayi tana b'ata fiska, ganin ko kallonta baiyi ba yasa ta wuce tana sanɗa ta je ta saka kayanta.

Tana juyowa suka haɗa ido.
Kwab'a fiskarta tayi tamkar zata fashe da kuka tace " saida ka kalleni ko?"

Kawar da fiskarshi yayi yace "meye zan kalla a wajen ,na duba ne naga ko kin gama, idan zaki b'ata mun lokaci ne kuma in tafi in barki ki ta rikitowa."

"Oho, Allah ya so ka."

Murmushin gefen baki yayi yace " da me zakiyi?"

"Zan haɗa ka da baba alhaji."

Turare ya ɗauko yana fesa mata yace "Me zaki ce mishi?"

"Kaii, Habibii wannan turare kamshinshi ya fi na wanda yaya yunusa yake sayamin."

A take ya ɗaure fiska "Uban yunusa ba yunusa ba."

Rike bakinta tayi tana zare ido "Kai Habibii ,kasan waye baban shi kuwa? shine fa jauron Jambutu , aradu idan aka jika ba za a barka ba ni dai ba ruwana."

Iza keyarta yayi yace "Wuce muje."

Da sauri ta juya ta rike hanunshi tace "Ka wuce dai."

Bai kulata ba tana rike dashin suka fito daga ɗakin.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Suna barin wajen mummy ta dawo ta zauna kusa da daddy.

"Alhaji, wai wnn yarinyar itace matar Habibullah."

Fiskarshi ɗauke da fara a yace "Itace Sa'adatu."

Dan jimmm tayi kafin ta kuma cewa "amma ai tayi kankanta da aure alhaji, dubi shirmen da take ta zubawa."

"Abinda zaki duba, shi ɗinma ba wani girmane da shi ba, nawa Habibullah ya ke ,yaron da bai wuci shekaru ishirin da ɗaya zuwa da biyu ba."

Jinjina kanta tayi kafin ta kuma cewa "Amma alhaji baka ganin a yanzu dukansu biyu basu san zafin kansu ba, ta iya yiyuwa gaba suce basa son juna ko ɗaya daga cikinsu ya bijire, kuma ma fa ni alhaji dama akwai yarinyar da nayiwa Habib tanadi, sai kuma lokaci guda ... "
Sai kuma tayi shiru ta sadda kanta kasa alamar dai abin bai mata daɗiba.

Gyaran murya daddy yayi kafin yace "Abinda nakeso ki fahimta anan Hajiyata, Wannan *al'amarin ubangiji ne* kuma ba a ja da al'amarin ubangiji a duk yadda ta kasance.
Ki sani cewa Allah da ya hukunta wannan al'amari shi ya barwa kansa sanin dalilin yin hakan, kuma ko menene, ya faru daga baya, Allah yana sane, shi kuma yasan yanda zai tafiyar da al'amarinshi saboda, haka shawarar da zan baki shine, kar ki ja da *al'amarin ubangiji*
Ki rike yarinyar nan tamkar 'yar cikinki, ki kula da tarbiyarta, ki bata farin cikin da ya kamata ace ta samu a gaban iyayenta, ki sani cewa ɗa na kowa ne, dan shi kanshi Habibullah makaranta zai tafi ba wai zasu zauna tare daga yanzu bane, yanzu duk wani hakki na kulawa da ita yana hanunki.

Bayan haka kuma ,maganar akwai wacce kika tanadar mishi da ita duk bai b'aci ba.
Habibullah namijine kuma mijin mace huɗu, sbd haka banga abin damuwa a ciki ba."

Ajiyar zuciya ta sauqe, sai yanzu taji hankalinta ya ɗan kwanta, har taje tayi umarni da ahaɗa musu break fast.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Gurin saukowa daga stairs ɗinne kuma aka shiga drammer dan gaba ɗaya jikinta rawa ya keyi ,shi kuma yace da kafarta zata sauqa.

Gamgam ta rikeshi suna sauka a hankali har suka ida saukowa.
Wani wawan ajiyar zuciya ta sauke tace "Habibi Allah zai saka min wahalar da ka bani."

Wata 'yar yarinya ce ta shigo wacce bazata wuci sa' ar bintun ba ɗauke da tray a hanunta.
Saida ta ajiye kan dinning snn ta duka har kasa da gaisheshi kafin ta kuma fita ta shigo da sauran abin bukata.

Bin yarinyar  bintu tayi da kallo har ta fita snn ta maida kallonta kanshi.
"Wacece wnn Habibi."

"Larai sunanta."
Ya faɗa a takaice.

"Kanwarkace?"

Ba tare da ya kalleta ba yace "Zo ki ci abinci sarkin surutu."

"A ina? A saman?"
Ta jero tambayoyin tana wurwurga idanu.

"Ba zan ci a sama ba fa nikam."
Ta kuma faɗa jin bai amsa mata ba.

Nan tsakiyar falon ya tattaro ya kawo, ta ko zauna ta tankwashe kafafu tana kallonshi.

Soyayyar irish ya fara zuba mata a plate ya tura mata.
Kafin ya zuba nashi.

"Meye wnn Habibi, aradu bazan ci ba. "
Ta faɗa bayan ta furzar da irish din da ta sa a bakinta, tana yamutsa fiska.

"Me yayi."

"Ba daɗi, wani iri, nikam bazanci."

Tashi yayi ya koma dining ɗin ya ɗauko ɗayan warmern ya kawo ya buɗe , luckily pepper soup na naman kaza ne a ciki.

"Wnn fa?"
Ya faɗa yana nuna mata warmern.

Leka cikin coolern tayi ta haɗiyi yawu kafin tace "To ga abunda mutum ya sani kazo kana bani abunda ban sani ba.?

Tana faɗa tana karb'an warmer daga hanunshi.

Cikin damuwa yace "Ai wannan bazai kosar dake ba Islam."

"Yo shi wannan ɗin kosar dani zaiyi da ka bani."

Ta faɗa tana nuna irish ɗin.

Juye irish ɗin yayi cikin warmer, ya zuba mata pepper soup ɗin ya sa mata spoon snn ya je ya ɗauko bread ya kawo.
Ko kafin ya dawo tayi nisa abinta.

"Gashi kici da wnn amma haka kawai baza ki koshi ba."

"Habibi wa ya dafa miyannan, ko dai larai?"

"Mamarta ce."
Ya bata amsa a takaice."

"Amma fa ta iya girki, zan je ta koyamin."

"To ci ki koshi sai in kai ki wajenta ki koya."
Ya faɗa yana haɗa mata tea.

Saida taci tasha tayi nakk, tayi hamdala kafin tace "Ya baka ci ba Habibi."

Hararar wasa ya zuba mata yace "sai yanzi kika san banci ba, da cikinki ya ɗauka ko."

Dariya tayi tana shafa cikinta tace "Aradu na koshi kam."

Cin abinci ya shiga yi tana ta zuba surutanta yana shiru har ya kare.

"Tashi muje na kaiki gurin su larai."

Shiru tayi saida ya sake maimaitawa.
"Nima bazan amsa ba tun ɗazu nake ta maka magana kayi kamar baka jina."

"To baki ga cin abinci nakeyi ba, idan ana cin abinci ba a magana."

"Na sani ai, haka innata ma take cemin, kullum sai ta make ni wajen cin abinci wai na cika surutu, to mutum kuma zai ga abun magana bazaiyi ba dan kawai yana cin abinci."
Ta karishe ta b'ata fiska tamkar a lokacin innar ta maketa.

"Zo muje in kaiki wajen su larai, idan kuma can sama zaki koma kiyi bacci muje na raka ki."

" Wa, ni jikar Buba Yusa, (kamar yadda taji innarta ke faɗa, wani lokacin kuma sai tace ni shashishatu, dan jin innarta takance ni Aishatu ) sai dai dai muje gurin su larai ɗin dai."

Gaba yayi tana binshi a baya suka nufi hanyar kitchen.

Tun kafin su iso larai ta hango su, sbd haka sai ta kama hanyar zuwa falon domin tattara kwanuka.

"Larai, larai, larai kin shiga raina larai."
Bintu tace mata mata tana dariya lokacin da ta zo kusa da su zata wuce.

Kaɗan larai ta kalleta ta kawar da kanta ta wuce.

Bakinta ya ɗan ja yace "wannan bakin tsokana."

Tun bai kare magana ba ta rike hanun ta cuno bakin tace "wnn hanun cin zali."

Hmm, kawai yace suka karasa kitchen ɗin.
Gaisawa yayi da maman larai a mutunce tana tambayar shi ya hanya snn ta maida kallonta kan bintu tace "Bakuwa mukayi ne alhaji karami?"

Kafin ya bada amsa bintu ta duka har kasa tace "Eh, ina kwana goggo Marka?"

Kuttttt😳

*Aunty Ruqayya ce🥀*
[7/31, 11:09 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*70-75*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*D*a sauri Habibullah ya bar wajen yana jinjina rainin wayo irin na Islam.
Tana ji dai yacewa matar Mmn larai, amma tsabar rainin hankali irinnata sai ta ce mata goggo Marka.

Ci gaba bintu tayi da gaisuwarta harda ce mata innarta tace ta gaishesu.

Ita ko Mmn larai duk tayi tsammanin ko ta yiwa bintu kama da wata mai sunan ne shi yasa ta kira ta da hakan.

Kujera yar tsuguno bintu taja ta zauna ta fara zubawa mmn larai surutu kamar dama can sun saba, har larai ta dawo ta samesu.

Tana kallo larai ta wanke kwanukan da sukayi amfani dasu.

"Ku nan a tsaye kuke wanke wanke,?"
Tambayar da tayi wa larai kenan.
Ita ko larai gyaɗa mata kai kawai tayi.

Cabbage da carrot Mmn larai ta fitar ta ajiyewa larai.

Zumbur bintu ta mike ta isa wajen.
"Meye wnn?"
Ta tambaya tana tab'a cabbage.
Tun kan su bata amsa ta kuma cewa "D'obo ɗume jun ba leggal bindigaru ɗo?"
(Wnn kuma menene kamar sandar bindiga."
Ta tambaya tana nuna carrot.

Dariya Mmn larai tayi ta fara mata bayani ɗaya bayan ɗaya.
Haka ta zauna cikin kitchen ɗin sai uban tambayoyi take ta zuba musu,duk abinda ta gani bata sani ba sai ta tambaya har suka kare girkin.

Ko da suka gama binsu BQ tayi nanma sai zuba musu surutu takeyi.
Habibullah da ya leko yaga suna tare ya fita ya tafi harkokinshi dan yasan Mmn larai bata da matsala sai dai asamu akasi ta wajen Islam.

A can wajensu taci abinci, tayi sallar azahar da la'asar.

Sai da yamma Habibullah ya shigo, lokacin su Mmn larai suna kitchen itako bintu ta samu ruwa ta buɗe zai zuba yakeyi a jikinta tana ta tsalle.

Can yaje ya sameta tana ta tsalletsallenta bata ma san da mutum a wajenba.

"Islam, me kikeyi anan?"

"Gashi kana gani wanka nakeyi."
Ta faɗa tana share fiskarta, snn ta kara da "Yaushe kazo nan Habibi?"

Karasawa yayi ya kashe famfon tun kafin yayi magana tace "Yauwa Habibi ɗauko min kayana."

"Da ban dawo ba fa?"

"Sai larai ta ɗauko min tunda kasan nidai ba hawa sololon samnnan zanyi ba."

Gyaɗa kai yayi aranshi yana ayyana za a sha daga da ita kafin ta saba da yanayin gidan nasu.

"A ina zaki canza kayan to?"

"D'akin su larai, anan naci abinci na yi sallah ma."

Waro ido yayi yace "Kina nufin tun ɗazu baki koma ciki ba?  Watakil kinsa mummy tana ta nemanki."

"Wace mummy, oh Wannan Hajjajon?
Ta karishe da sigar tambaya.

"Baza ta nemeni bama na sani."

Juyawa kawai yayi yaje ya kawo mata wasu kayan.
Anan ɗakin su larai ta saka kayan, ya shanya mata jikakkun kafin ya jata suka koma part ɗin mummy tana tambayarshi baba alhaji.

Suna shiga su Iman da Miemie ma sukayi sallama suka shigo. Sun dawo daga makaranta sanye da uniform.
Da murna suka tareshi suna mishi oyoyo dan basu san ya dawo ba sai lokacin, itako tana tsaye tana kallonsu cike da sha'awa dan sun burge ta cikin uniform ɗin.

Da gudu suka haura stairs suna kiran mummy ita kuwa tana tsaye sai kallonsu take tana mamakin rashin tsoro irinnasu da suke iya hawa da gudu, a ranta take cewa nima cire tsoronnan in fara hawa har na iya hawa da gudu, duk tunaninnan da takeyi fiskarta ɗauke yake da murmushi.

"Islam magriba ta kusa dan Allah ki zauna ki nitsu guri ɗaya kinga baba alhaji ma ya kusa dawowa."

D'aure fiskarta tayi tamkar ba ita ke smiling yanzu ba.

Ganin yadda ta gimtse fiskarta ya gane gardama zata yi mishi, hakan yasa shi cewa .
"Muje in raka ki gun mummy."

"Sai dai gurin Goggo Marka."
Ta amsa mishi da sauri ganin nufin shi su haura stairs ne, dan ta gwammaci tayi ta zama gunsu larai da ta je gun mummy ko ta haura stairs.

"Wai me yasa kike cewa matar nan goggo marka ne, bakiji maman larai muke ce mata ba?"

Juya idanunta tayi kafin tace "Kaima dai Habibinnan meye na tambaya, bakaji muryarta tana kama da ta goggo marka, mai wakar, ehhh, goggo mar, goggo mar, goggo marka ba?"

Kaɗan ya hana dariya ta sub'uce mishi ganin yadda ta dage tana wakar a nufinta ya gane wakar da take nufi.

Dakewa yayi yace "ni ban san wakar ba ai balle nasan yanda muryarta yake."

"To tsaya kaji ɗayar."

:Ehh, soyayya,

"Gidan mutuwa ake kuka mata gidan biki sai guɗa.

"Eh, soyayya."
Wannan karo harda rawarta.

"Wnn fa, kasanshi."

"Ban sani ba Islam, wanka zanyi kike ta b'ata min lokaci."
Ya faɗa yana barin wajen da sauri dan yasan muddin ya biye mata saidai yaji ana kiran sallah.

Tab'e bakinta tayi qasa qasa tace "Sannu kifi ko kwaɗo, karewar son wanka."

Yana fita ta fice kitchen, ta samu maman larai tana kwashe tuwo.

"Sannu da aiki goggo marka."

"Yauwa sannu 'yar albarka."

"Ina larai?"
Ta tambaya tana bin kitchen ɗin da kallo.

"Tana sashinmu."

Buďan bakinta sai cewa tayi "Cegiya kurma, wai ita haka take ne bata magana? Ana mata magana sai ta kalli mutun ta juya kai, nifa bana son irin haka."

Murmushi mai sauti Mmn Iarai tayi tace "Dan baku saba bane, in kun saba zata sake ku rika taďi."

Nan ta shiga tayata suka kammala tare ta bita kofarsu.
Yanzuma a can tayi sallah taci abinci.

Sai bayan sallar isha,i ta shiga part ďin su mummy, nan ta samesu cikin main palour.

Shigowarta ba da jimawa ba, Daddy da Habibullah suka shigo.

Duk yadda sukayi tazo suci abinci cewa tayi taci a gun su Iarai, a koshe take, dan ita sam hankalinta bai kama mummy da yaranta ba shi yasa ma bata so ta rika shiga cikinsu, baranma yanzu da ta shigo tana musu magana babu wanda ya amsa mata daga cikinsu, ita kuma uwarsu tana gani bata tambayesu dalili ba, hakan ba kqramin kular da Bintu yayi ba.

Zamanta tayi cikin palour tana kallon T.V har suka gama suka dawo cikin palourn.

Daddy ne ya fara tashi yana mata sai da safe snn mummy tabi bayanshi, daga nan su mie mie ma suka yi ďakinsu suka barta da Habibullah.

"Islam, wato bakyajin magana ko, nace ki zauna kada ki fita saida kika koma gunsu Mmn Iarai, har da cin abinci wajensu."
Ta tsinkayo muryar Habibullah daga gefenta.

A kaikaice ta kalleshi ta maida hankalinta ga T.V kadin ta tab'e baki tace.

"Ni aradu gun innata zan koma dan dukanku haushi kuke bani banda baba alhajina."

Waro idanunshi yayi yace "Haushi?"
Ni da wa."

Tamkar tana jiran tambayar tace "Kaida wannan hajjajon da yarannan da suka tashi, su Mamu ko Mume kuke ce musu oho, aradu dukanku haushinku nakeji."

Kusa da ita ya dawo ya zauna a kasa kamar yadda take zaune dan sam bata son zaman kujeran ganin ko ta zauna ma kafanta ďangalewa sukeyi basa saukowa qasa.

Juyo da fiskarta yayi zuwa b'angaren  da yake ya tambayeta "Me muka miki daga zuwanki Islam?"

Kwace fiskarta tayi ya sake juyo da ita "Ni dai ka mayar dani gun innata bazan iya zama a gidannan ba, mutane daga babba har yaro sai mugun hali, ayi ta ɗaure maka fiska, kayi wa yara 'yan uwanka magana suki amsawa, snn kai kuma kace in zauna cikinsu kar inje gun su goggo marka, idan naje kace bana jin magana?"
Ta karashe maganan idanunta cike tab da kwalla.

Tausayinta yaji ya kamashi jikinshi kuma yayi sanyi, tabbasa yaso ya fahimci yanayin mummyn tashi game da Islam saidai baiso gaskata hakan ba, duba da yanda take sonshi da nuna mishi kulawa a tunaninshi koda dabba ya kawo yanuna yana so zata bashi kulawa ta musamman balle kuma mutum, mutum ɗimma mace mai rauni, marainiya, wacce kuma take a matsayin matarshi.

Katse mishi tunani tayi da cewa "Zaka mayar dani gobe Habibi?"

A sanyaye yace "Yi hakuri Islam bazan iya ba."

Waro idanunta tayi tana kallonshi "Baza ka iya me ba, Habibi?"

"Maida ke gurin innan."
Ya faɗa ya kawar da fiskarshi daga kallon fiskarta sbd yadda expression ɗinta ya nuna bai mishi daɗi, bai tab'a tunani dawowarta gidansu zai sata cikin damuwa ba kuma sam baya fatar hakan ta kasance.

Shesshekar kukanta yasashi juyowa da sauri yana yana kallonta "Ya salam, Islam da gaske kikeyi ne wai?"

Bata tanka shi ba saima ci gaba da kukanta da tayi.

Jawo ta yayi a sanyaye ya kwantar da ita kan cinyarshi snn ya ɗora hanunshi akanta yana cewa "Yi haquri Kanwata, ki bar kukan gobe ma ba a gidan zaki wuni ba, basai sunga idonki ne ba zasu yi miki mugun hali, kuma bazan sake hana ki zuwa wajen su larai ba, snn ke da zaki shiga makaranta ma me zai dameki?"

Da sauri ta ɗago "Kace aradu, yaushe zan shiga makarantar? "tana tambaya ne tana hango kanta cikin uniform irinnasu Miemie goye da schl bag a bayanta.
Take kuma ta fara sakin murmushi tamkar ba ita ke kuka ba.

Share mata hawayen fiskarta ya shiga yi snn ya mayar da kanta ya kwantar kafin yace mata "Wannan term yana karewa zaa shigar dake makaranta kinji."

"To ina zamuje goben kuma?"
Ta sake jefo mishi tambaya.

"Yawo zamuje, zan kaiki gidan Aunty Nafi ma ki ganta, tana sonki sosai fa."

"Wacece aunty Nasin.?"

"Aunty Nafi nace ba Nasi ba."

Dariya ta kwashe dashi tace "Na sani ai, Nasin yafi dađi ne, haka Baba jauro yake kiran wata jikarshi mai irin wnn suna Nasii, ai yafi dađi ko?

"Ni dai banji dađi a Nasi ba, ke dai na lura đabi ar kice canzawa mutane suna..
Ya kara da tambayarta "Wa ya miki kitson nan."

"Babba 'yar Inna wuro muka je gidanta tayi min, dan Yaya Yunusa zai zo ahi yasa kaga tayi min mai kyau, ayya yaune fa zai je kuma bazi sameni ba."

"Islam."

"Habibi."

"Islam, idan na sake jin sunan yaronnan a bakinki."

"Me zakayi ."
Ta tambaya da sauri.

Kwafa yayi yace baza ki sani ba sai kin sake."

Turo baki tayi tace "Kuma mutum da đan uwanshi sai a ace kar ya kira sunanshi , ni ka daina tab'a min kitso da zafi, kuma dan baka san kukan da nayi tayi ba lokacin da ake min kitson."

"Wai kukan kitso kike yi?"

Kamar jira takeyi tace "Sosai ma har da majina."

*Gaisuwa da godiya gareku masoya, na gode kwarai da kulawarku gareni, Allah ya bar zumunci.*
*Kamar yadda kuka sani ba isasshiyar lafiyace dani ba, duk da dai naso na karasa littafin kafin azumi, amma banyi tsammanin hakan zai kasance sbd a yanzu ba ko da yaushw zaku rika ganin posting kamar da ba, sai duk randa Allah ya bani iko zaku gani, Na gode kwarai.*
[8/1, 6:26 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*80-85*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*B*akinki ne kolorogol d'in ai.
Ya amsa mata.
Cuno bakin tayi, "Idan baza ka fad'a ba ka bari kawai ba sai ka zageni ba, sunaye duk ba dad'in ji.

Zuwan aunty Nafi ne ya katsesu ,take ce musu bari ta tambayi Daddyn su Shureim sai su tafi.

Sayayya sosai suka mata kama daga English wears, atamfofi, english gowns da arabian gowns, takalma, hijabai gele, night wears, cosmetics da duk wani abin buqata.
Aunty Nafi ta tafi da atamfofin zata kai mata dinki.

Wurin computernshi ya wuce da ita, suna shiga ciki friends suka fara sowa suna washi "Na fati baban fati."

Shiko sai washe baki yakeyi yana mika musu hanu suna shaking.

A can sukayi sallar la'asar.
Sun d'an jima a gurin dan saida yad'an tab'a aiki, sai tab'e tab'e takeyi tana suburbud'o mishi tambayoyi.

A hanyarsu ta komawa gida suka bi ta bakin kasuwa, sai kalle kalle takeyi.
Ganin yawan jama'ar dake kai kawo ya sa ta jefo mishi tambayar da ta bashi mamaki.

"Habibi wad'annan duk mutanene ? "
Saida ya mata kallon mamaki snn ya kawar da fiskarshi tare da ce mata "aljanune Islam."

A tsorace tace "Dukansu ? "

"Eh, to a had'e suke, da mutane da aljanun amma ba lallai bane ki iya bambancesu."

"Innahu min sulaimana wa innahu bismillahi rrahmanirrahim."

Shi ta shiga maimaitawa a bayyane bayan ta rufe fiskarta da tafukanta.

Sosai abin ya bashi dariya har yana buga steering mota.
Wai ita in an barta da gaske taga aljanu kenan.
Ya ayyana a ranshi.

Itako bata ma san yanayi ba, saima kamo ayatul kursiyu da tayi tana karantawa duk da akwai errors a ciki bata gam a iyawa ba.

Har suka isa gida addu'a takeyi, ba kakkautawa.

A sanyaye ta shiga palourn ta tadda mummy da yaranta.
"Sannu Hajjajo ina wuni ? "
Tace a sanyaye.

Kallon yanayinta mummy tayi ta tab'e baki snn tace "lafiya."

Ko kallon su Miemie batayi ba ta nemi guri a qasa ta zaune.

Niki niki ya shigo da kaya, su miemie suka tashi suka karb'e shi, hakan yasashi komawa ya d'ebo sauran.

"Wannan kayan fa ? "
Mummy ta tambaya.

"Na Islam ne Daddy ya ba da kud'i a sayo mata."
Ya bata amsa.

"Madalla, Allah ya saka da alkhairi."

"Amin."
Suka amsa dukansu.

"Yauwa kuzo muje saman."
Tare suka haura dukansu , yaudai su Bintu anyi jarumta dan babu wanda ta rike saidai a d'ar d'ar ta haura.

D'akin aunty nafi na da mummy ta nuna musu a matsayin ya zama na Bintu, an gyara shi tsaf.

Murna kamar tsyi yaya har ta manta da damuwar da ta shigo da ita.

Fita mummy tayi ,shima yabi bayanta dan tattaro kayan da suka shigo dasu.
kamar tana jira ta zarowa su miemie ido "Ku kuma me kuke min a d'aki, ko dan jiya na kwana a d'akinku zaku rama yau, to aradun Allah baku isaba, babu wacce zata kwanar min ad'aki, ku fita ma tun d'akin bai saba da ganinku ba."
Ta karishe tana mai murgud'a baki.

Mamaki kamar ta kashesu itako ko a jikinta, saima d'ale gadon da tayi ta zauna tana karkad'a kafa tare da bin komai na d'akin da kallo.

A masifance Iman ta nufo ta zata zazzaga mata Habibullah ya shigo, hakan ya taka mata birki, Miemie kwafa tayi ta fita daga d'akin Iman ta mara mata baya.

"Tashi mu shirya kayan malama kin wani hard'e sai kace kin samu kujerar sarauta."
Ya fad'a yana ajiye kayan hanunshi.

Wuf ta mike "To tsaya Habibi barin yi fitsari."

"In kin shiga ki had'a harda kashi ma."

Wani juyi tayi ta rufe fiskarta "Wayyo Allah, ashe haka kake baka da kunya kake kiran wnn abun."

Cikin dariya yace "To bakya yin ne."

Idon a rufe still tace "Kai daina fad'a dan Allah, ka tab'a jin nace zanyi ne, abunda b'oyewa akeyi kai kuma kake bayyanawa, na fasa fitsarinma."
Ta fad'a tare da fad'awa kan gado tayi ruff da ciki taki bud'e idon a dole ya bata kunya."

Kusa da ita ya dawo yana dariya, ya d'agota.
Kam kam ta kankame jikinta sam taki yarda su had'a ido.
"Wasa fa nake miki , je kiyi fitsarinki daga nan kiyi wanka.

A d'ari ta fincike ta shiga bayangidan tana mita , wanka dai wanka dai kullum kullum.

Daga murya yayi yace idan bakiyi  ba fa shigowa zanyi in miki da kaina.

Itama d'aga muryar tayi tace "Kayi sa'a ba a magana a bayan gida aradu da na antaya maka zagi, kamin wanka babba dani sai kace wata 'yar iska, ko an ce maka bani da lafiyane, ko

innata ma ai ta dad'e da daina yi min wanka.

Dariyar da yakeyi ya hanashi amsa mata, ko me tayi yanzu oho da take cewa ba'a magana a bayan gida.

Dressing mirror ya fara shiryawa snn ya koma wardrobe, yashiga jera mata kayan daki daki.

Rai a b'ace ta fito ita an sata wankan dole, dressing mirror tabi da kallo, yanda ya tsara gurin ya burgeta ba kad'an ba.
Mai ta shafa snn ta d'auko turaruka tana juyasu tana kallo.
Can tace "Wannene na fesawa a jiki wannene na kaya ? "

Jin bai kulata yasa tace " Na fati baban fati da kai fa nakeyi."

Barin abunda yakeyi ya yi ya juya ya kallota.
Tun kafin yayi magana tace "Oho, nima ba ji nayi an fad'a ba, suwaye fatinayenkanne ma nikam ? "

"Zo kiga d'aya."
Yace mata.

Ta jikin mirror ya nuna ta yace "Kin ganta ? "

"Ban ganta ba Bintu na gani."

"Shi kenan lokacin ganin nata ne baiyi ba sai kiyi hakuri."
Ya fad'a tare da karb'ar turarukan hanunta snn ya shiga banbance mata..

Doguwar baqar riga mai had,e da hularta ya mika mata, tare da skin tight iya gwiwa ta saka, tana sakawa cikin jin dad'i da annashuwa take cewa, "Aradu kyauta zanyi da tsofaffin kayana dama ai idan aka samu sabo sai a kyautar da tsoho, larai kin samu kaya yasin, ita zan bawa aradu."

Har ta qaraci surutanta bai tankata ba, isa gurin wardrobe d'in tayi ta leqa, La, ilaha illallah, Muhammadu b'ii Abdullahi.(Muhammadu d'an Abdullahi.)
Allah am miyattima. (Allah na na gode maka."

Ta fad'a tana komawa baya baya.
"Habibi wann tulin kayan duk nawa ni kad'ai ? "
Sake juyawa tayi tabi d'akin da kallo, sai ko ta daka tsalle ta d'ale bayanshi, kad'an ya hana su tuntsura.

"Meye haka, zaki ka dani ne ? "

"Aradu duk cikin murna ne, wnn duka nawa ? Duka d'akin fa, d'akin 'yan gayu, nima fa na zama 'yar gayu."

Dirowa tayi daga bayanshi.
"Tsaya kaga irin tafiyar da zan rikayi yanzu tunda na zama 'yar gayu."

Wani taku takeyi tana d'angale hanu tare da mele baki sai wani yauki da yatsina takeyi ita a dole ta zama 'yar gayu.

"Idan kin gama tafiyan  gayun kizo in nuna miki."

Tsalle tayi ta haye gadon tana birgima, tana tsaya in more laushin gadonnan tukuna.

"To na tafi, in kon gama morewa sai ki fito."

Ai da gudu ta sauko ta rikeshi "Tare zamu fita yasin, nuna min toh."

Wardrobe d'in ya bud'e yana nuna mata yanda ya rarrabe kayan, har aka kai kan kayan bacci.

Ido waje tace "Hande en woni.(Yau mun banu)
Bacci ma harda kayanshi, wani abu sai 'yan gayu. "

Shidai zuwa yanzu ya saba da shirmenta shi yasa ko tayi ma baya damunshi saidai idan ta bashi dariya ya dara.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Garin sarki*

Qauyen da aka b'oye bintu.

Sun kasance cikin tashin hankali mara misaltuwa, tun daga lokacin da labari ya riskesu wasu sun d'auke Bintu a mota.

Kauye ne da babu service balle ayi maganar waya, babu ta yanda zasu sanar da goggon Bintu abunda ya faru.

Inna wuro tayi kuka ta tsinewa wanda ya d'auke Bintu yafi cikin kwando.
Haka suka kasance cikin alhini da tashin hankali har zuwa lokacin da Yunusa tazo domin ganawa da sahibarsa Bintu.

Nan yayi *Gamda katar* da mummunan labari.

Cikin tashin hankali mara misaltuwa ya koma ya sanar da mahaifiyarshi abun da ya faru.

Ba tare da b'ata lokaci ba ta nemi izini wajen jauro suka kama hanyar Yusa, sai kwantarwa yunusa hankali takeyi da cewa watakila ma 'yan yusan ta gani ta biyosu ta dawo gurin innarta.

Basu kara shiga tashin hankali ba saida suka iso inna ta nuna musu bata san da zancen ba, dama dai can ta riga tasan cewa bintu b'atacciya ce, kuma har yanzu babu wanda yace ya ganta ko ya ji labarinta.

"To ko alhajinnan ne suka je suka d'auke ta"
Cewar yunusa cikin karin tashin hankali.

Girgiza kai inna tayi tace "Banyi tsammani ba, dan d'azu d'azunnan suka kirani suke tambayar ko anji labarin ta.

Nanfa Goggo Rabi ta tsure ta fita mayafi a hanu zani na faman fad'uwa.

Gidan babban wansu taje ta sa mishi kuka tana ta shiga uku  ta b'atar da 'yar d'an uwanta, kuka sosai takeyi wanda ya d'agawa musu hankali gashi babu wanda ya fahimci inda zancenta ya dosa.

Shiko yunusa yana can ya tasa inna a gaba sai rusa mata kuka yakeyi tana aikin rarrashi.

Kaff ya had'a sauran 'yanuwansu banda goggo Rahi dake aure can wani kauye dan ya fahimci lamarin nata babbane.

Dakyar ta daure ta zayyane musu abun dake faruwa wanda ya jawowa sauran shiga wani sabon  tashin hankali sai salati da salallami suke ta zabgawa.

Cikin matsanancin b'acin rai Babban yayansu yace "To yanzu da kika zo kika tasa mu a gaba kina kuka me kike so mu miki ? "
Wato ki kara samu cikin tashin hankali naki hankalin ya kwanta ko ?
Mu dama a hakan muka d'auka ta b'ata, me yasa yanzu zaki kawo mana wnn labarin ?
Idan ba rashin hankaliba kina sane aka d'aura mata aure amma a haka kika dauketa kika boye sbd son zuciya , wa ya gaya miki ana ja da *Al'amarin ubangiji*
To Wlh kiyi gaggawar nemo mana Bintu idan ba haka kotu ce zata raba mu.
Sauran ma kowa fad'an albarkacin bakin shi yakeyi cikin nuna mata tsantsan b'acin ransu, babu wanda ya sassauta mata a cikinsu.

Gidan innar Bintu suka tattaru suka koma, nan suka had'u sukayi ta jajanta al'amarin , tare da bawa innar bintu hakuri snn kuma suka ce kada goggo ta kuma zuwa gidan d'aya daga cikinsu har sai ta kawo musu Bintu idan ba haka ba basu ba ita.

A cewar wansu babba tunda ta iya aikata haka ga 'yar Barkind'o suma sun tabbata haka zata yi musu ko fiye ma idan taga bayan idansu.

Itadai goggo Rabi sai kuka takeyi tana share majina da hab'ar zaninta.

*Inna da Habibi ku taimaka ku bayyana Bintu ko goggo Rabi zata samu kwanciyar hankali🙏🙏*
[8/1, 6:32 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*90-95*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Congatulations*

*Foulani Cerdia, (marubuciyar Mahaifina)* Our newly wedded Amarya.
Ina tayaki murnar shiga sabuwar rayuwa da samun karuwa na aure da kikayi.

Allah ya baku zaman lafiya mai dorewa, Allah ya azurtaku da zuri'a dayyaba.

*Happy Married life Deeyan papa*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Wasa wasa sai da ta kai sati guda ana jinyarta duk ta zama abar tausayi.
Sosai daddy ke nuna mata kulawa da tausayawarshi gareta, hakama aunty Nafi.
Suma larai da Mmnta sosai ciwonta ya damesu, haka kuma tana samun kulawa daidai gwargwado daga garesu.

Mummy kam dai ba yabo ba fallasa, a gaban daddy ne take bata tata gudunmawar kulawar, saidai yana bada baya itama zata shiga harkokinta ta manta da wata Bintu, balle kuma su Mie mie da ta zame musu abokiyar fada dan sam basa shiri, hakan yasa a yanzun ma babu wacce ta nuna tausayawarsu gareta.

Ita da kanta take matsawa a kira mata shi, amma duk lokacin da aka bata wayar tana jin muryarshi zata fashe da kuka , shi kuma hakan ba karamin kara mishi damuwar yakeyi ba dan dama acikinta yake, gaba daya ya yi sanyi ya zama wani iri ba dadin jikinnashi yakeji ba, ko daga muryarshi ma kaji zaka gane hakan.

Dakyar ta ware ta ci gaba da zuwa makaranta duk da dai abin ba gama sakinta yayi.

Da suka samu hutun makaranta kuma da kanshi daddy ya dauketa ya kaita yusa.
Sati guda sukayi suka juyo bayan ta zaga danginta sai murnar ganinta sukeyi dan dama inna ta sanar dasu komai ganin yanda goggo ta tayar musu da hankali, saidai ita goggo Rabince har yanzu bata sani ba dan wansu babba ya hana a fada mata yace su barta sai taji a jikinta sbd gaba.

A gidan aunty Nafi ta qarasa hutun, cikin kwanciyar hankali kuma kullum sai sun gaisa da Habibullah.

Tun daga lokacin idan akayi hutun makaranta daddy yake kaita da kanshi su dawo tare.
Yawanci kuma a gidan agidan aunty Nafi take qare hutunta, acan kuma take koyon girke girke kala kala, idan ta dawo gida kum a ta d'ora a gun goggo marka inji ta.

Can kuma Bauchi saidai Daddy yaje gurin Habibullah, dan sam ya hana shi zuwa duba da halin da suka shiga lokacin tafiyarshi, yace sai sun saba sosai da rashin ganin juna, hakan yasa saidai suji juna ta waya, da yake kuma a gidan abokin daddyn ya ke zaune, yaji labarin duk wani hali da Habib din ya shiga farkon zuwanshi.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Yau ta kama ishirin da bakwai ga watan Ramadan mai albarka.

Diran bazata yayi musu ko daddy bai sani ba sbd yasan hanashi zaiyi.

Kusan magriba ya iso, saidai mummy ta ganshi kawai kamar daga sama.
Da murna ta tareshi tana tana ta cewa "My son zuwan bazata haka, ba sanarwa."

Shafa kanshi yayi yace "To ya zanyi mummy daddy ya hanani zuwa ni kuma kewarku ta dameni."
Ya fad'a yana rarraba idanu.

"Mummy ina kannena ban ji motsinsu ba."

"Suna gidan Nafeesa yau a can suka wuni."

Shiru ya d'anyi kafin yace "Barin je inyi wanka."

Saida ya biya ta kitchen wajen Mmn larai suka gaisa ta mishi barka da zuwa kafin ya wuce.

Gun mummy ya sake dawowa yace ta bashi key zaije ya dauko su.

Hanashi tayi tace ya huta sun kusa dawowa beside ma magriba tayi.
Ba don yaso ba ya wuce masallaci.

Ko da ya idar da sallar magriba dabino da ruwa kawai yasha ya tashi zai fita, saida tayu magana ya qara da fruits kafin ya koma bakin gate ya zauna, har akayi kiran sallar isha'i ya wuce ya tafi masallaci.

Suna idarwa ya fito ba tare da ya tsaya dogon addua ba, ya nufi gun mummy yana tambayar ko sun dawo.

A gajiye suka nufo palourn tana gaba suna biye da ita a baya.

"Assala...."
Sallamar ne ta katse sakamakon ganin wanda bata zata ba zaune yana facing kofar shigowa palourn.

Wani tsalle ta doka tare da ihun kiran sunanshi ta nufeshi a guje.
Cikin zafin nama ya cab'e ta ya daga ta sama yana juyi da ita cikin shauqi da ishiqi tare da tarin farin ciki marar misaltuwa.

Ihunta yasa mummy fitowa daga dakinta cikin sassarfa, haka ma su miemie suka qaraso da sauri har suna hadawa da gudu dan ganin abunda takewa wnn ihun.

Suma da mamakin ganinshi suke ta kallonsu, saida ya gaji dan kanshi ya direta kan kujera ya bata peck a forehead, kafin ya kamo hannayensu Miemie da Iman yana" i miss u my sisters."
Sannu da dawowa suka mishi cikin farin cikin ganishi snn ya maida hankalinshi ga Bintun dake kallonshi cike da madaukakin farin ciki tamkar yau ta fara ganinshi.

"Habibi yaushe ka iso ? Me yasa baka fad'a ba ? Me yasa baka kira aunty Nafi ka fada mata ba ? "

"Wanne zan amsa a ciki Islam ? "

Yace lokacin da yake zama kusa da ita , suma su aiman nan kusa dashi suka zauna dukansu cikin tsantsan farin ciki.

"Habib kar ka biyewa shirmensu ka tashi kaje kaci abinci,kaje ka huta gajiyar hanya. "
Cewar mummy.

Sai a snn yasan da tana wajen.

Yana tashi Bintu ma ta mike ta bishi tana cewa "da  ka fada mana zaka dawo ai da zama zanyi na had'a maka wani juice mai dankaren dad'i wanda aunty Nafi ta koya min."

"Woow, ashe harda Juice kika iya ? "
Ya fada lokacin da suka isa wajen dining din.

"Kai harda girki mafa na iya."

Serving dinshi ta farayi tana tambayarshi me da me zaici.

"Duk abinda kika sa zanci."
Ya ce mata.

Labari take ta bashi yana cin abinci sai kallonta yake tayi yana mamakin girman da sukayi dukansu cikin shekaru biyu.

Sai washe gari ya fito musu da tsarabarsu da ya kawo musu, Mummy sai korafi takeyi shi da yaje karatu me ya hada shi da tsaraba.

Tare suka je yusa bayan anyi sallah da kwana biyu, sai a  snn goggo Rabi tasan da cewa an gane Bintu, dan sun hadu a can, shi kuwa Yunusa har yayi aurenshi, kawayen Bintu ma su indo duk sunyi aure.
 sosai sukayi ziyara dukansu har da su Miemie, satinshi biyu ya koma.

Wann karo abin da sauki, cikin kwanaki uku ta ware.

Daga nan kuma idan ya dan samu chance yake kawo musu ziyara.

*BAYAN SHEKARU UKU*

Zuwa wnn lokaci su Bintu an zama cikakkun 'yan mata, SSCE suke rubutawa tare da su Miemie dan Habibullah ya bada shawarar haka tunda tana kokari a karatun , sbd da yanda ya tsara da ya qare service dinshi babu bata lokaci Bintu zata tare kuma daddy ma ya yi na'am da hakan.

Saidai suma daddy da mummy suna nasu shirin game da maganar auren da zasu mishi wanda

mummynce ta buqaci hakan, dan ta yanke tare za ayi bikin da kuma tarewar Islam din duk da dai shi uban gayyan bai da labari, saidai suna da yakinin bazai watsa musu qasa a ido ba.

Zuwa wnn lokacin kuma Bintu ta kware wajen sarrafa girke girke kala daga wajen aunty Nafi da Mmn larai, dan sosai aunty Nafi ta ke koya mata su da kuma gyaran jiki da kuma dabarun zaman aure dan yanzu kam tasan cewa ita matar aurece kuma tasan mijin.

Wani irin shaquwa sukayi duk da basa tare amma kusan kullum suna makale ta waya, a hankali da dabara ya cusa mata soyayyarshi wanda tun tana daukan abun wasa har ya zama so serious.

Zaman su dasu Mie mie kuwa dai gashinan dai babu yanda suka iya da ita, dan ta zane musu kadangaren bakin tulu, babu abinda yafi damunsu game da ita illa ganin irin extra kulawa da take samu daga daddy da aunty Nafi da kuma uban gayya Habibullah.

Mmn larai kam tana ganin fi'ili kala daga wajen Bintu a cikin kitchen yanda take sarrafa abubuwa take sha, har ita ma Mmn larai ta saba.

Takan yi blending aya da dabino  da kwakwa tasa cikin fridge idan yayi sanyi tasha, wani lokacin har  ta kara da milk.

Takanyi hadin
Abarba, da kwakwa, tasha.

Ko kuma ta hada fruit salad, ta yayyanka fruits daban daban ta sa fridge tasha.

Takan hada kankana da ayaba ta yayyanka ta zuba milk tasha.

Ko kuma milk din zalla ta hada da zuma ta gauraya tasha.

Dabino kuma tare da aya ta rika hada su haka tana ci, wnn kuma cimar tace ko a makaranta.

Indomie kuma ta dafa ta yanka dafaffen kwai akai tare da danyar tomatoes, taci, wani lokacin har jelouf sin shinkafa ko taliya haka take musu.

Rice and stew hade da plantain ko kuma ta yayyanka ayaba akai tana ci tana lumshe idanu.
Wnn duk training din aunty Nafi ne.
Kuma sun zame mata jiki, babu wayewan gari da baza tayi daya ko biyu daga cikin wadannan ba, duk da dai bata san amfaninsu ba ita dai tana daukan hakan a jin dadinta ta kawai takeyi.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Yau suka gama last papern su , a gajiye suka dawo gida sbd bata lokaci da sukayi da friends

dinsu suna ban kwana harda pictures sukayi ta snapping , last pics with uniform.

Saida ta fara biyawa ta wajen Mmn larai tana ce mata ta tayata murna yau ta rubuta last paper, tayi bye bye da secondry sch.
Ta dan jima a wajenta kafin ta shiga part dinsu .

Su Miemie ta tarar suna ta zuba surutu, daga sallamar da tayi sai sannu da gida da ta yiwa Mummy tayi wuce dakinta ta watsa ruwa ta canza riga da skirt na English wears marasa nauyi kafin ta sauko dan bawa ciki hakki.

Tana sauqowa idonta ya sauka gurin da su miemie suke zaune kan three sitter sunsa wani handsome guy a tsakiya sai bashi labari sukeyi.

Hada ido sukayi da gayen tayi saurin kawar da kanta. saida ta isa kusa da su ta sake dagowa. Ganin yanda ya kafeta da ido ya sata gaisheshi ta wuce.

D'ebo abinci tayi taje ta bude fridge ta dauko kunun ayanta da tasa tun da safe kafin ta tafi sch. ta zo ta zauna nan tsakiyar falon ta basu baya ta shiga cin abincinta.

Tana gamawa ta tattara gurin snn ta koma dakinta dan bude phone dinta da ta kulle kafin ta tafin.

Mssgs din Mutuminnata ne sukayi ta shigowa na taya murna qare exams dnta sai kuma sauran na kalamai ne masu sanyaya zcy.

Tana karantasu tana smiling cikin shauqi har ta gama kafin ta sake saukowa ta tafi wajen abokiyar hiranta goggo marka ,dan larai kam anyi aurenta.

Sai dare ta shigo part din nasu ta zauna a palour tana kallo.

Miemie kawai ta tarar dukansu babu wacce ta kula yar uwarta.

Suna nan zaune ya shigo da sallama, direct kan two sittern da Bintu take zaune yaje ya zauna fiskarshi dauke da fara'a yace Gimbiya kallo akeyi ne? "

Da mamaki ta kalleshi tana tunanin abinda ya sake dawo dashi yanzu kuma snn kuma ma shi wanene, meye matsayinshi a gidan da yake shigowa kai tsaye haka, dan ita in ba yau ba bata taba ganinshi a gidanba.

karamin gyalen data yafa a kanta ya dan rike tare da cewa "Ba maganane queen."

Tsam ta mike tabar musau falon ma gaba day ta haura dakinta tana jin wani irin tsoro na shiganta.

Washe gari abun mamaki saiga kiran Habibullah tun basu gaisa ba ya fara ce mata "I had a terrible dream yester night Habibty ."

"Me ya faru Habibi, wani irin mafarki" ta tambaya a kagauce.

"Ganinki nayi da wani kuna zance, wlh mafarkn ya daga min hankali sosai ba kadan ba."

Zaro ido tayi kamar yana kallonta kirjinta na bugawa tace "Habibi sharrin mafarki ne, kaima kasan saidai a mafarkin hakan bazai faru da gaske ba."

Saida ya sauke ajiyar zcy kafin yace  "I hope so."

Sauran hiran dai anyi shi ne kawai amma gaba daya a tsarge take gani take kamar yasan wani ya mata magana jiya da dare......
[8/1, 6:34 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers.*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*105-110*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

D'akin Bintun ya sake komawa wnn karon da gudu ya haura steps d'in, wanda yasa Miemie da Iman sakin baki suna kallonshi, dan ko kallonsu baiyiba balle yayi musu magana.

Wayam ya samu bata nan, har toilet ya leqa nan ma shiru, hakan ya dad'a tayar mishi da hankali, ya fara tunanin dama can tana ce mishi dan shi da daddy kawai ta zauna a gidan sai kuma goggo Marka dake d'ebe mata kewa, badon su ba da tuni ta bar gidan.
A ranshi ya ce, hakan yana nufin mummy da yaranta suna kuntata mata kenan.
Wnn tabbas haka yake,dan yaga Alamu da dama saidai rashin tabbatarwa.

Me kuma mummy take nufi da had'a shi aure da Miemie, tunda bai tab'a ce mata yana sonta ba, shi asali ma kallon yar uwa ta jini ya ke mata.
Ko hakan yana da alaka da barin bintu gidanne, ta yiwu watakil an gaya mata.

Ganin tunani bazai amfana mishi komai ba yasa shi fitowa daga dakin da hanzari yana kuma tunanin inda ya jefar da wayarshi,  dan tunda ya dawo bai bi takan wayar ba.

D'akinshi ya koma, ya lalub'o wayar ya shiga dialing nambarta, amma ko sau d'aya bai shiga ba, dan switch off ake ta ce mishi.

Iska mai zafi ya furzar kafin ya zauna ya dafe kanshi.
"Allah yasa ba yusa ta tafi ba baiwar Allah."
Ya fad'a a bayyane, cikin nuna tausayawa.

Can aunty Nafi ta fad'o mishi, duk duniya itace abokiyar shawarar shi, dan baya b'oye mata komai game dashi, kamar yadda itama yake abokin shawararta.
Yasan zai samu mafita a gurinta.

Da sauri ya mike ya koma part ɗin mummy.
Iman ya aika da taje wajen mummy ta karb'o mishi keyn mota.

Tare suka fito da Iman, tana mika mishi keyn tana tambayarshi inda zaije.

"Zan ɗan fita ne."
Ya bata amsa.

Har ya fara tafiya ya dawo da baya.
"Mummy ina Islam, yauma ban ganta ba."

Tab'e baki tayi tace "Tana ɗakinta, ɗazu ta fito taci abinci ta koma."

"Amma na duba ɗakin ban ganta ba."
Ya sake tambaya yana kallonta.

"Ta yiwu ta fita ne, kasan idan zata fita ba faɗa min takeyi ba, saidai inga dawowarta.

Shiru yayi yana mamaki al'amarin mummy, wato dai lallai lallai sai ta b'ata Islam a wajenshi takeso.
So take taga sun samu sab'ani.
Ko meye dalilin hakan?"
Ya tambayi kanshi .

D'ayar zuciyarshi ta bashi amsa da sonkai, dan tana son ka auri 'yarta, shi yasa tun farko bata ɗauki Islam da mihimmanci ba.

"Da kyau."
Yace a fili, wanda a tunaninta ta daɗa kufular dashi kan bintu ne, batasan da ita yake ba, yasa kai ya fita.

Gidan aunty nafi ya nufa kai tsaye, yana mai fatar Allah yasa tana can.

Fruits take wankewa cikin kitchen taji muryarshi suna gaisawa da aunty Nafi.
Take taji wani irin fad'uwar gaba ya ziyarceta, ta tsame hanu daga wankin fruits ɗin da takeyi taja kujera ta zauna ta zabga tagumi.

Kiran da aunty nafi ta mata ne yasata fitowa a sanyaye.

"Gani aunty."
Tace tana zama can  karshen kujerun falon.

"Habib ne yake kiranki."
Ta faɗa tana binta da kallon nazari.

Kallo ɗaya tai mishi ta ɗauke kanta, tace "Sannu da zuwa."
Kasa kasa, kamar bata son faɗa.

Bata jira amsawarshi ta tashi taje ta kawo ruwa da kunun gyaɗan da suka dama a flask, ta jera su da kananan cups a kan tray taje ta ajiye mishi ta juya tayi cikin ɗakinta ta kwanta.

Duk abinda takeyi da kallo yake binta, ya ma rasa ta ina zai fara, gashi kuma ya ga a bintunta take dan ko kallonshi bata sake yi ba.

Saida yaga ta shiga ɗakin harda rufo kofa ya sauke ajiyar zcy tare da cewa "Akwai matsala."

Aunty dake kallon sabon salo, a ranta tana cewa dama nasan da wata a qasa.

"Me yake faruwa ne Habib, ban gane muku bafa."

Murya a sanyaye yace "Babu abinda tace miki akayi mata ne aunty?"

"Ni bata ce min an mata komai ba, saidai tazo min a halin rashin lafiya, snn akwai damuwa sosai tattare da ita, saidai taki faɗa min komai."

"Hmm, mummy ta bani mammaki aunty."
Nan ya kwashe duk yadda akayi ya sanar da ita harda maganar auren miemie da Daddy yayi

mishi.

Cikin mamaki da tausayawa Bintu aunty tace "Lallai ka haďu da kaidin mata habib, amma mummy ra ban mamaki , sonkai a fili?
Ba banza ba Islam tafi son zaman nan gidan da can, ba mamaki bata jin daďin zaman gidanne."

"Hakannema sister, dan tasha nuna min hakan nine dai ban maida hankali ba."

"To yanzu ya zakayi da mgnr auren miemien kuma?"

Saida ya ja tsaki, ya daďa ďaure fiska tamkar miemien tana kusa yace "Daddy ne ai, ba don shi ba ko sama da qasa zasu haďu banga abinda zai sa in amince ba, kuma kinga yanzu duk abinda zanyi zaiga kamar bijire mishi nakeson yi, dan lokacin da ya faďa na nuna mishi bana, so, sai yace wai ko dan albarkaci riko da kulawar  da mummy ta bamu bai kamata naki tayinta ba, tunda ma zumunci take so a qarfafa, ni yanxu damuwata islam ya zanyi?"

"Je ka sameta ku sasanta kanku amma kada kayi gigin sanar da ita maganar auren."

Kamar mai tsoron shiga haka ya tsaya a kofar ďakin.
Ita dai aunty nafi tana kallonshi da tausayawa dan dukansu biyu tausayi suka bata, har ya shiga ciki.

Jinginuwa yayi da jikin kofar yana kare mata kallo, ita kuwa daďa lafewa tayi kama tayi bacci.

Jin kamar ana doso ta yasa ta ďaga hanunta tana cewa a hankali "Aunty ki koma nayi bacci kar ki tashe ni sai na tashi da kaina."
Ta maida hanunta ta sake lafewa tayi shiru.

Kaďan ya hana dariya ta sub'uce mishi duk da yana cikin damuwa, wato dai har yau tana nan da halinta na yarinta, in baka ba ina mai bacci zai yi magana.

A hankali ha haura kan gadon ya kwanta ya rungumota ta baya tare da sakin kwakkwarar ajiyar zuciya.

Da saurinta tayi yunkurin tashi ya maida ta.
A kunnenta ya raďa mata "Dama mai bacci yana magana?"

Turo baki tayi kamar yana kallon fiskarta tace "Ina ruwanka dani."

"Haba my Islam kiyi hakuri ki yafe nima na yafe."

"Nidai ban yafe ba."
Ta faďa cikin shagwab'a.

Narke murya yayi yace
"Ba haka bafa nake miki, idan kince in yafe yafewa nakeyi ko kin manta?"

"Aini bana maka tsawa kuma bana saka kuka."

Sake narke murya yayi yace "Nima ai kuskure ne da rashin sani bazan sake ba, kinji?"

Shiru tamishi, sbd haka cikin kasalalliyar murya yace "Kin yafe?"

Maqe kafađarta tayi tace um um.

"Kuka kike son in miki."

"Nidai bance ba." ta amsa da sauri."

To tsallen kwaďo."
Girgiza kai tayi alamar a'a.

"To me kikeso?"
Ya faďa yana daďa shigar da ita jikinshi.

"Ka kyaleni kawai."

"Bazai yiwu ba.
Ya faďa yana juyo da ita suyi facing na juna.

"Islam pls mana."
Ya faďa tamkar zaisa mata kuka.

"Na yafe to."
Ta faďa tana b'oye fiskarta a jikinshi.

"Thank u my Habibty."
Ya faďa tare da pecking kumatunta.

Bata amsa ba sai ce mishi da tayi.
"Ya Babana?"

"Yana can yana fushi dake."

Da sauri ta ďago kanta tace "Da gaske? Baka fađa mishi abinda kuka yi min bane."
Ta faďa idanunta

Suna tara qwalla.

Girgiza mata kai yayi yace.
"Wasa fa nake miki."

"Ni dai kam Allah ya isa tsakanina da Fa'izunnan."

Ya fahimci Hafiz take nufi sbd haka yace "Kada kiga laifinshi, shima baisan kina da aure ba, shi ne kuma ya warware min komai, so munyi laifi kuma mun roki gafara a yafe mana."

Shiru ya biyo baya na ɗan lokaci kamar baza tayi magana ba, daga bisani sai tace.

"Habibi, dan Allah mummy ce ta haife ka?."

Anxo wajen.
yace a ranshi.

Jin yayi shiru tace "Kayi hakuri idan tambayar ta b'ata maka rai."

"Baki b'ata min rai, tunanin nake ko wani irin musgunawa take miki a bayan idonmu, Islam, mummy ba ita ta haifeni ba, mahaifiyata ta rasu tun ina ɗan shekara bakwai, mummy dai ita  ta rike mu bayan rasuwar kakarmu mahaifiyar daddynmu dan ita tayi rikonmu bayan rasuwar mahaifiyar mu.

"Allah yaji kansu."
Ta faɗa a sanyaye.

"Amin."

Shiru duka sukayi na ɗan lokaci kafin daga baya yace su koma gida.

Nan kuma tace fafur baza ta koma ba ita dai ya barta anan.

Saida ya haɗa da aunty Nafi, nanma saida ya mata alqawarin zasuje Yusa snn ta yarda ta bishi suka koma gida.

Mamakin ganinsu tare su mummy sukayi har mummy ta gaza haqura ta tambayeshi ko sun haɗu da Hafiz.

"Bamu haɗu ba."
Amsar da ya bata kenan.

Harkokinta taci gaba dayi kamar da, bata shiga harkar su mummy sosai, su ɗinma dama bata

gabansu, burin mummy dai taga miemie sun daidaita kansu da Habib, wanda shi kuma ko da wasa bai nuna yasan da wata magana akan hakan ba.

Wani lokaci idan mie mie ta je inda yake da gangan yake aikanta ta kira mishi Bintu, kuma tana ji tana gani yayi ta janta da wasannin da zasu sosawa miemie rai, a tunaninshi ko zata zuciya tace bata son auren.
Wani lokacin har goyon Bintu yakeyi a gabanta, ko kuma yace Bintu ta kama shi ya tashi sai tasa hanu ta rike hanunshi da zummar mikar dashi sai ya jawota ta faɗo kanshi yayi ta mata cakulkuli suna kyalkyata dariya.

Hakan kuwa ba karamin konawa Miemie rai yakeyi ba, saidai mummy na daɗa karfafar mata gwiwa da ta kwantar da hankalinta zai dawo gareta.

A haka maganarshi da Miemie tayi qarfi, ba tare da sanin Bintu ba, saidai tana ganin tsana sosai daga garesu, ita yanzu duk wani halin da zasu nuna mata baya damunta tunda tasan mummy ba ita ta haifi Habibinta ba. gurin Daddy, Habibi, da Mmn larai take samu tayi walwala.

Dagewa Mummy tayi lallai saidai a hada bukin da tariyar Bintu, duk da daddy baiso hakan ba, yafi so Bintun ta fara tarewa kafin ayi maganar biki, amma mummy ta kasa ta tsare, lallai yadda takeso hakan za'ayi.

Aunty Nafi ce ta bada shawarar suje su sanar da innar Bintu maganar Miemie in yaso ita ta sanar da ita, dan shi Habib yace bazai iya faɗa ba.
Itama aunty Nafi tace ba za aji mutuwar sarki a bakinta ba, kuma basu so taji a wani waje ko daga bakin su mummy.

Sbd haka Habib da aunty Nafi tafi suka tafi Yusa ba tare da sanin Bintu ba.

Sosai Inna ta fahimcesu kuma ta nuna musu dama ta sani dan daddy yazo da kanshi ya sanar da ita.
In dan Bintu ne kuma su kwantar da hankalinsu Habib ya kawo mata bintun zata yi mata bayani da kanta.

Kwanansu biyu da dawowa ya sake ɗaukar hanyar Yusa tare da Bintu, sai murna takeyi zata je taga Innarta da sauran 'yan uwanta.
Shi kam har cikin zuciyarshi tausayinta yakeji, dan shi yasan irin zafin da yaji a ranshi lokacin da ya ganta da Hafiz, a ranshi yake tunanin ko yaya zataji idan taji labarin wani auren za a mishi...

*Hmm, ko yaya Bintu zatayi idan taji wannan labari🤔🤔*
[8/1, 6:40 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*120-125*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Barka da sallah, da fatar anyi sallah lafiya, Allah ya karb'i ibadunmu.*

💝💝💝💝💝💝

"*M*e ya sameka ka rame haka Habibi?"

Abinda da furta ya dawo dashi hayyacinshi, dan gaba ɗaya expression ɗin fiskarta ya gama tsorata shi, jira yake yaga da me zata tareshi, sai kuma yaji abin da sauki.

Runtse idanunshi yayi tare da girgiza kanshi kafin ya buɗesu a hankali yana binta da kallo. Bintu dake jin kanta tamkar an sauqe mata wani abu mai nauyi, idanunta tamkar an yaye mata wani duhu, har yanzu bata daina mishi kallon mamaki ba.

"Baka da lafiya ne?"
Ta sake jefo mishi tambaya.

Ba tare da ya bata amsa ba ya sake jakar kayanshi dake rataye a kafaɗarshi ya riko hanunta har cikin ɗan madaidaicin falon .
A daidai tsakiyar falon ya saki hanunta yayi sujudu sshukur yana mai jaddada godiyarshi ga Allah (S.W.T ).

"Islam."
Yayi magana a karo na farko  bayan ya ɗago.

"Habibi."
Ta amsa har yanzu mamaki bai gushe a fiskarta ba.

Tsam ya rungumeta tare da furta "Alhamdulillah, kin samu lafiya Islam, Allah ya dawwamar dashi ya daɗa kare mu."

A hankali ta zame jikinta ta zauna kan kujerar dake kusa dasu, tana kallonshi.
Cikin ɗaurewar kai tace "Dama bani da lafiya ne?"

Kusa da ita daff ya zauna jikinsu na gugan juna shima kallon nata yakeyi da bayyananniyar farin cikin ɗauke a fiskarshi.

"Ka matse nifa nikam."
Ta faɗa a shagwab'e.

Murmushi mai sauti yayi yace "Idan akwai abinda yafi matsi ma yau zan miki my Islam."
Ya karashe daidai lokacin da yake
Kewaye ta da hannayenshi, tare da ɗora hab'arshi bisa kanta.

Farinciki ba kaɗan ba inna taji ganinsu tare ba tare da wata matsala ba.
Bata b'ata lokaci ba ta sanar da wan baban Bintu, kan kace me har labari ya bazu Bintu ta samu lafiya, masu taya murna har sun fara zuwa , ita har mamaki abin yake bata yanda kowa yake ta nuna farin cikin karara ciki kuwa har da goggo Rabi.
Sai da daddare Habib yake sanar da Bintu labarin abinda ya faru da ita wanda hakan ba qaramin tsoro da mamaki ya bata, a zcyrta tana tunanin shi yasa ta ganta gidan innarta duk da ita ɗin amaryace an kaita ɗaknta saidai kuma sai yanzu wnn tunanin ya faɗo mata, da can bata tab'a tunanin abinda  ya ajiyeta gun innarta ba tunda tasan ba a gunta take ba.
Har kuka saida tayi snn a qarshe ta godewa Allah da ya bata lafiya yasa ta dawo cikin hayyacinta.

Daddy ma kanshi baiyi qasa a gwiwa ba ya garzayo washe gari dan ganewa kanshi abin farin ciki.
Tare kuwa ya samesu harda inna ana ta hira cikin farin ciki.

Addu'a sosai ya musu tare da nasiha mai mai shiga jiki, yana qara jaddada musu su riqe ibada kar suyi wasa da addu'a, bayan haka suyi riko da al'qur'ani mai girma, saboda akwai lokacin da manzon Allah (S.A.W) ya cewa sahabbanshi.
"Akwai zamani da zai zo fitintinu zasu yawai, zasu zamo kamar yankin duhun dare ga al'umma.
Sai sahabbai suka tambayeshi "Ya Rasulullah menene mafita?"
Sai ya basu amsa da cewa "Mafita shine riko da al'qur'ani."
Sbd haka muyi riko da al'qur'ani 'yan uwa mu yawai karantashi, waraka ne a garemu, zamu samu yayewar matsalolinmu snn Allah zai kawo mana sauqin fitintinun da muke ciki na wnn zamani.
Ga sunan da yawa daban muna ganinsu.
Kashe kashen rayuka babu gaira babu dalili.
Maita na secret cult da na gargajiya.

Zinace zinace da cututtukan da suke haifarwa.
Tarayya tsakanin jinsi ɗaya.
Mutum ya cutar da ɗan uwanshi ba tare da dalili ba.
Rashin riko da zumunci.
Lalacewar tarbiyar yara tun suna kanana.
Mugunta da mugun nufi.
Gasu nan dai, masifu da fitintinu iri iri.
Allah ya karemu ya kare mana da zuri'a da 'ya'yan musulmi baki ɗaya.

Mmn larai da aunty Nafi su suka je suka gyara musu gidansu tsaf har da girki kafin su iso. Anan suka dawo suka tarar dasu har da daddy, ya kara ɗora musu nasiha kan wanda ya musu a can, dan shi a tunaninshi zai samu har da Miemie a gidan tunda su aunty nafi sun ce musu suna can, amma sai ya samu akasin haka.

Murna aunty nafi da Mmn larai kamar su goya Bintu, itako sai tambayar labarin yaran aunty nafi take tayi tana cewa tayi kewarsu.

Saida suka ci suka sha, Bintu ta shiga wanka ta sha kwalliyarta tayi rass, ga jan kunshi da tasha na asalin lallen gargajiya wanda aka yi mata da adon salatif a qafa da tafin hannu, sai kuma yatsunta da ta qawata da lallen sun daɗa fito da sirrin kyaun hannayenta da kafafun, ga kitso da tasha na two step wanda aka yarfa mata su 'yan kanana duk da dakyar da ta yarda akayi mata su amma sunyi kyau ba kaɗan ba.

Bakin swiss lace mai adon green flowers ta saka wanda ya daɗa fito da haskenta tayi rass da ita sai kamshi take zubawa, da ka ganta kaga sabuwar amarya.

"Wooow, kaga amaryar Habib."
Aunty ta faɗa lokacin da Bintu ta fito cikin yauki tana bada step.
Hakan ya maido da hankalin Mmn larai da Kuma Habibullah da rike da remote, shima ya canza kayanshi zuwa kanana da alama shima wankan ya yo, yana canza chanel a T.V. zuwa gareta.

Dukansu ido suka zuba mata wanda hakan ya kusan sata tsarguwa, amma da yake Bintuce sai ta kame ta nufi gurin da Habib yake zaune ta tsaya a gabanshi tare da rike kugu.
Murguɗa mishi baki tayi tare da farfara ido tace " Malam kallon lafiya."

Ramawa yayi shima yace "nayi laifine?"

Dariya su aunty suka kwashe dashi Mmn larai tace "Alhaji qarami kaima ta koya maka kenan."

"Kyaleta Mmn larai ta ɗauka ita kaɗai ta iya ne shine na gwada mata."
Ya faɗa tare da qara murguɗa mata bakin.

Wnn karo harda ita a masu dariyar ta koma kusa da aunty ta zauna.

"Aunty tambaya min ita  dan Allah, wai meye sirrin wnn fresh ɗin da tayi."
Ya maida zancenahi kan aunty nafi da bata daina musu dariyan ba, a ranta tana jin Bintu tana daɗa burgeta dan ko shiriritar bintu zai sa ta qara shiga zcyr Habib balle kuma wasu sirruka da san bintu tana dasu na musamman wanda wasu tasan ita ta koya mata su da kanta, kuma ta fahimci lectures ɗinta yana matukar zama cikin kwakwalwarta.

"Gaskiyarka fa Habib nima zanso inji wnn sirrin."
Ta qarashe zancenta tana mai kallon Bintu.

Saida ta murmusa kafin tace "Aunty kema kin sani madaran shanu ne kawai da inna take ɗura min ,tun ina sha da marmati har yazo ya fita kaina."
Ta bada amsa tana yamutsa fiska.

"Yauwa 'yar uwata Allah yasa kin zo mana dashi dan na daɗe ban sha ba, tun zuwa na yusa na karshe rabona dashi."

"Hmm gashi can cikin kayan da ta haɗo min ina ce mata ta bari ta bari, sai da ta haɗo da shi, shiko Habibi har da cewa bakin ciki nake mishi.

Cikin zumuɗi aunty tace "Ai gwara da ta haɗo dashi da nima haka zance kinmini bakin ciki."

"Balle kuma ni da baza ayi babu ni ba."
Cewar Mmn larai da ta zame musu uwar ɗaki kuma abokiyar shawara.

"Bari in kawo muku wlh, danni basha zanyi ba."
Ta faɗa tana mikewa .

"Zauna abinki amarya, barin in ɗauko kar ki wahalar min da kanki, ammafa ba duka ba sister, nima zaku rage min."

B'ata fiska bintu tayi, dan Allah ka basu duka, jiya yasha fa aunty yauma kuma haka."

"to ke me ya dameki tunda ba da bakinki zansha ba."

"Sanin hali ne ai, dan nasan sai ka tilasta ni nasha."
Ta faɗa tamkar zatayi kuka,  ta kuma cewa.
"Rowa ma dai ba kyau."

"Kyautar da bakayi niyya bafa akwai lada ?"
Ya tambaya yana barin wurin.

Dakyar aunty ta samu ta korashi ya fita ya basu waje.

Shawarwari sosai suka shiga bata na irin zaman da zatayi da mijinta da kuma kishiyarta.
Hakuri, ladabi da biyayya, juriya, kau da kai, tsabta na jiki da muhalli, iya girki, bawa miji kulawa ta musamman, kama daga abincin shi, abinsha, sutura, biya mishi buqatunshi ba tare da gardama ba, faranta mishi, kada ki gujewa shimfiɗarshi, kada kuma ki ki amsa kiranshi a ko wani lokaci, ki kasance mai yawan  sakewa kuyi hira kina faɗa mishi kalamai masu daɗi, ko shi bayayi a hankali zaki ga ya fara,  da kiyaye harshenki da faɗa mishi munanan kalamai,  kada ki zamo mai yawan ɗaure fiska sbd idan kika saba mishi da hakan ko da kina cikin damuwa ko !b'acin rai ba lallai bane ya maida hankalinshi gareki ,kokarin danne bacin ranki a gabanshi, yawan shiga jikinshi, ya zamo abokin shawaranki, abokinki, ɗanuwanki, uwa uba ki bashi girmanshi da darajar shi a matsayinshi na mijinki.
Ki nuna mishi baki da kamarshi, ki kuma bi umarninshi muddin bai kaucewa addini ba.
Maida kanki tamkar karamar yarinya a gun mijinki, yi mishi shagwab'a, ki kasance mai son jiki tamkar mage, yawan kwanciya a jikinshi, cin abinci tare, idanma kin riga kinci kafin ya dawo, ki kasance kina zaune kusa dashi a lokacin da yake cin abincin.
Ki zamo jajirtaciyya a kula da lamarin gidanki, ki zamo uwa, kanwa, abokiyar hira, abokiyar shawara, ga mijinki, ki zamo sirrinshi, ki kuma kasance mai rike muku sirrinku, dss.
Waɗannan duk makamai ne na zaman aure ammafa sai an daure.

Mmn larai ce ta qara da cewa "Na manta ban tuna miki yanda ake tada miji daga bacci ba ta yiwu ko kin manta,
Nan Bintu ta fashe da dariya sbd abinda Mmn larai ta tuna mata, itama Mmn larai ta shiga tayata dariyar.

Dariya sosai aunty nafi  ma tayi lokacin suka kare bata kabarin abunda bintu ta tab'a yi tun kafin ta qare sec sch.

Wani lokacine Habibullah ya zo hutu gida, da yake yana yawan yin azumin litini da alhamis, sai ya kasance idan zai yi tare sukeyi da bintun.
Wata rana ya dawo gida a gajiye da azahar ga axumin yana bashi wahala, sai ya shige ɗakinshi ya kwanta.
Ya fara bacci kenan bintu ta shiga ɗakin.
Tsayawa tayi tana qare mishi kallo, daga kanshi har yatsun kafafunshi, nan idanunta suka faɗa kan babban yatsan kafarshi, ta shiga kallon suman dake kwance kan yatsar.
Can dai ta duqa ta kama suman taja, wanda hakan yayi sanadiyyar farkawarshi a gigice, sbd azaban zafin da yaji baisan sanda ya kwasheta da mari ba.
Itako tamkar jira takeyi ta sa ihu ta fito da gudu har ta tsorata Mmn larai, da ta fito daga kitchen zata tafi sashinta.
A gigice ta shiga tambayarta sbd ganin da gaske take kukan.

Buɗan bakinta sai cewa tayi Habibi ne ya karya mata azumi.
Habib da ya biyo bayanta yayi still sbd jin sharrin da tayi mishi.
Ko da Mmn larai ta kuma tambayarta sai cewa tayi bari tasha ruwa tukuna ta faɗa mata abinda

ya faru, ai daga shan ruwa sai ta zarce da cin abinci, karshe dai Habib ne ya faɗa Mmn larai yanda abin ya kasance.

Ko da Mmn larai taso ta fahimtar da ita cewa mari baya karya azumi, sai cewa tayi wnn kam ya karya sbd zafinshi da qaran da yayi lokacin da akayishi.
"Kyaleta Mmn larai dama sanadi take nema dama, ai ɗazu da na kira ta ce min tayi azumin yau yana jijjigata."
Abinda Habib yace ma Mmn larai kenan.
Mmn larai da ci gaba da cewa, kinsan me yafi ban dariya da Mamaki?
Dagewa tayi ta b'ata rai sai ciccijewa takeyi a dole ita anyi mata laifi.
Amma kafin magriba sai gata tana haɗa mishi abin buɗa baki cikin annashuwa tamkar ba ita ke fushin ba sai shi ya san yañda yayi ya lallab'a mutuniyar tashi.

Haɗuwa sukayi  sunata dariya karshe aunty ta zolayeta da shi kenan ma ai ita kam ta gama sanin yanda zata tashe shi a bacci cikin sauqi, itama cikin dariyar take cewa ɗan ba qara, Allah ya tsareta da shan mari.

Shiru shiru ba labarin Miemie har suka qarashi zamansu suka koma gida.

*Gaisuwar barka da sallah, gareku, Halima Auwal, Maryam A.I Gital, Hauwa .S.Zaria tare da ɗaukacin grp members na fasaha Online writers, Allah ya maimaita mana.*
[8/1, 6:44 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*115-120*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*C*ikin ruɗewa da tashin hankali ya shiga jijjigata yana kiran sunanta.

Karshe kwantar da ita yayi ya samu ruwan sanyi ya yayyafa mata.

Shiru bata motsa ba hakan ya jawo mishi rikicewar da ya rasa abinda ya kamata yayi, sai kawai ya durkushe a gurin yana tattab'a, bugun heart da pulse na hanunta .
Ji yayi tamkar babu alamun numfashi a tare da ita.

Aunty ya fara kira cikin muryar kuka yake shaida mata abinda yake faruwa.

Kuka sosai yakeyi yana maganganu "Islam, ki rufa min asiri kada k min haka, dan Allah kiyi hakuri ki tashi da dss."

Cikin wnn hali aunty ta shigo ta samesu dan ko gida basu isa ba, ya kirata suka juyo.

Itama ganin halin da take ciki hankalinta ya tashi, ta rasa ma dame zata fara.

Daddy ta kira ta sanar dashi lkacin suna tare da mummy.
Ba tare da b'ata lokaci ba ya tashi ya kamo hanyar gidan.

Cikin wnn yanayi ya taddasu, habib sai kuka yakeyi aunty tana tayashi.

Asibiti yace su kaita, nan suka kwasheta suka kaita asibiti, shi kuma mijin aunty ya wuce gida sbd yara.

An ɗauki lokaci sosai kafin aka samu ta farfaɗo, har rige rigen shiga sukeyi.
Habib gaba jin jikinshi yakeyi kamar paper, ba karfi sam.
Hakan yasa aunty ta rigashi shiga ciki, sji kuwa daddy saida ya riko Habib ganin halin da yake ciki.

Kwance take hawaye na zuba ta gefen idanunta tana tunani da kuma mamakin abunda ta gani fikin ɗakinta ɗazu.

To ina Habibin kuma?
Tambayar da tayiwa kanta kenan.

"sannu my sister, me kikeji yanzu?"
Aunty ta faɗa lokacin da ta riko hanunta.

Share hawayen da suka gangaro mata tayi tace "Aunty ina Habibi?"

Daidai shigowarsu su tare da daddy ,aunty tayi pointing mata shi, tana cewa "Gashi yana shigowa."

D'agowarnan da zatayi, sai kawai tayi saurin kankame aunty tana pointing ɗinshi da yatsarta

bakinta na karkarwa ta gagara magana.

"Menene?"
Aunty ta tambayeta hankali a tashe.

Zaro idanunta tayi sosai kan shi kafin dakyar ta iya cewa "Baba...
Bata qarasa ba ta zube a wajen ta sake suma.

Inna lillahi.. Me zan gani haka Islam?"
Cewar aunty."

"Daddy ka gani ko?"
Habib ya faɗa yana kuka mai tsuma zcy.

"Ba kuka zakayi ba Habibullah, addu'a zamuyi mata, zauna ina zuwa."
Daddy ya faɗa yana zaunar dashi kan ɗaya daga kujerun ɗakin.

Kiran doctor daddy yayi suka shiga duba ta.
Ko da ta kuma farkawa bata sake buɗe idanunta ba, sai cewa aunty takeyi tayi mata addua.

Addua sukayi ta karanto mata suna tofa mata har bacci ya kwasheta.

Daddy yana fita daga gidan bayan ya sanar da ita abinda yaji mummy ta tashi tana ta zagaye palourn.

Can ta kuma kiranshi ya sanar da ita halin da ake ciki na sake sumar da tayi da kuma abunda takeyi.
Adduar samun lafiya ta mata  ta tambayeshi Miemie, sai a snn ya tuno da Miemie yace ta tura a ɗauko ta ta koma gida dan bai kamata a barta ita kaɗai ba.

Turawa tayi a ɗauko tan kafin tayi dialing wata namba ta yi shiru na ɗan lokaci.

"Me kika sa akayiwa 'yar mutane?"
Abinda ta fara faɗa kenan.

Daga ɗaya b'angaren aka ce mata "Me kuwa zan sa a yi mata bayan abinda ya dace da ita."

"Gaskiya ni bance ki haukata musu 'ya ba, nace ya manta da ita kawai ta fita ranshi, ya komawa Miemie kawai ko ba haka mukayi dake ba?"

"Share kawai, sun cancanci susha wahalan dukansu harda uban shi yasa na musu haka, kuma kada ki matsa dan babu abinda zai canza, a hakan ma zasu manta da juna ke dai zuba ido

kisha kallo kawai."

Kashe wayar tayi ta zauna tana tunanin ,anya wnn aikin yayi kuwa, gaskiya ba haka taso ba.

A haka suka kwana suna mata addua, Washegari da ta tashi kamar abun da sauqi, dan Habibullah daga window yake lekota dan yana tsoron ta sake ganinshi ta sume.

Da kanta ta sake nemanshi, yana shigowa kuwa ta qwalla qara tare da zubewa.

Ganin abun sosai ne yasa daddy ya sanar da Baffanta wan babanta, shi kuma yaje ya sanar da Inna.

Tare suka zo da innar tata, suka tarar da mummy da miemie da Iman duk suna nan, aunty kuma taje gida, sai Habib dake rakub'e, yaki tafiya gida kuma tsoron shiga yakeyi.

Sosai daddy yayi musu bayanin yanda abun yake hakan yasa wan babanta ya ce a nemi sallama, wnn cuta ba na asibiti bane.

Hakan kuwa akayi, sai dai suna fitowa ta hango Habibullah ta fara neman hanyar guduwa.
Da kyar suka rirriketa, a haka suka tafi gida gaba ɗaya bata cikin hayyacinta.

Alfarma baffanta ya nema da abar musu ita suje su nema mata magani.

Firr mummy taki amincewa, ita lallai a bar mata bintu zatayi jinyarta ai itama uwace.

Da mamaki Habibullah ya kalleta, snn ya cewa daddy, shi kam yanaga zaifi a barsu su tafi da itan su jarraba aga abinda Allah zaiyi.
Daddy yayi na'am da tafiyar nasu wanda sam ba haka mummy taso.

Daddy ne ya kaisu da kanshi, saidai habib baije dan gudun kada ta kuma ganinshi jikin ya tashi.

Kafin su tafi saida suka fara biyawa ta wani shahararren islamic chemist, daddy yayi wa malamin bayanin matsalar Bintun.
Magunguna ya haɗa musu da adduoi, snn ya bada shawarar Habib ya nisance ta na wani lokaci har sai maganin ya qare.

Bayan komawan daddy baffanta ya haɗa duka sauran 'yan uwanshi har da goggo rabi da goggo habi da basu cikin garin sunzo.

Bayani ya musu kan abinda yake faruwa ya qare da cewa yana fata ba hanun goggo Rabi cikin wnn al'amari, dan yasan halinta na rashin yarda da kaddara.
Wnn maganar ba qaramin qona mata zcy yayi ba, har ta gagara haqura ta fashe da kuka ta hau rantse rantse kan bata da masaniya kan abinda ya faru da Bintu.

Tabbas ayau tayi nadamar abinda ta aikata, abu ya faru wajen shekaru shida amma har yanzu yana bibiyanta.
A zcyrta taci alwashin muddin in har yi ma bintu  akayi itama bazata bari ba har sai asirin wanda ya aikata hakan ya tonu.

Kulawa sosai take samu daga wajen innarta  da'yan uwanta, saidai wajen shan magani ne sai anyi daga da ita, sbd sam bata son maganin, sai inna tayi da gaske take yarda tasha.

Tun da aka tafi da bintu mummy ta kudura cewa yanzu ya kamata ta shigar da miemie gun habibullah, sbd haka duk wani kulawar da ta dace a mishi take sanar da miemie yanda zatayi. Kullum kuma cikin kwalliya da kamshi take.

Shi kam Habib mamaki ma take bashi dan shi sam bai tab'a mata kallo da wata manufa ba da ya wuci ta kanwarshi tamkar yadda take a da, snn bai nuna alamar yana da niyyar komawa gidanshi bama balle ace su koma da miemie.

Shi a yanzu cutar Bintunshi yafi ɗaga mishi hankali, tunda ta tafi yake ciwon zcy dana gangar jiki, ga kewarta duk ta dameshi kuma an hanashi  zuwa ya ganta, shima kuma in ba warkewa tayi ba bazai so yaje ta shiga halin da take shiga ba idan ta ganshi.

Shima kuma daddy bai barshi haka ba dan maganin tsari yake nema mishi, ga addu'oi da yakeyi ba dare ba rana.

Duk da bata ganin wnn halittar yanzu amma bata mance da halittar ba, duk lkacin da abin ya faɗo mata takan tsinci kanta cikin matsanancin tsoro da faɗuwar gaba.
Hakan yasa duk tabi ta rame dan yawanci sai tazo bacci kamannin abin yake dawo mata, sai ta gagara yin baccin ,sai inna tayi ta tofeta da adduoi, haka kuma tayi wani irin sanyi tamkar ba bintu ba, yawacin lokuta zaka ganta zaune jigum har idan anyi mata magana takan zabura.

Suma dangin maman habib ba a batsu a baya ba wajen kawo gudunmawar taimakonsu.

Abinda yake bawa inna mamaki shine yanda kwata kwata bintu ta manta da wani Habib.
Yawancin lokuta idan ana maganar Habib bata nuna ko alamun tasan da wanda akeyi.
Haka kuma idan daddy yazo yace mata Habib yana gaisheta sai tayi shiru tana kallonshi kamar tana so ta tuno wanene Habib ɗin.
Aunty Nafi ma tana kokarin zuwa dubata, haka idan tazo bintu zata nuna farin cikin ganinta amma tana kawo mata maganar Habib zata shiririce wajen kokarin tuno mai wnn suna.
Da wayarta dake snapping ɗinta ta tura mishi, wanda sam baijin daɗin ganin ramarta.

Inna bata fasa kawo mata zancenshi ba haka kuma idan ya kira wayarta tana bata su gaisa, saidai duk lokacin da taji muryarshi takan tsinci kanta cikin faɗuwar gaba, amma sam bata iya amsa shi, har ya karaci maganar da zaiyi bata tankawa duk a kokarinta nason gano ko shi ɗin wanene.

Bata kuma tab'a tambayarsu waye shi ba saidai idan anyi maganarshi tayi ta binsu da kallo.

Cikin ikon Allah satinta uku ta fara samun sauqi, dan ta daina ganin wnn halittar dake bata tsoro, yanzu tana baccinta peacefully, tana sakewa suyi hira da mutane ta fara dawowa asalin bintunta.

Ganin haka inna ta fara sata shiga gidansu Habib dake kusa dasu ta gyara duk a tunaninta hakan zaisa ta tuno da Habib, amma ko da wasa bata tab'a kawowa inna maganarshi ba.

Cikin sati biyu da warkewarta ta maida kibarta tayi kyau tamkar bata taba rama ba.
Shima kanshi yaji daɗin ganin hotonta wnn karon da aunty tazo, zuwa wnn lokaci kuma mummy tayi maganar su koma gidansu ya kai sau uku, daddy ne dai bai bada karfi kan maganar ba dan baya so ya takurawa Habib.

Goggo Rabi kuwa bayan addua da taimako da take nemawa Bintu harda kaikayi koma kan masheqiya ta dage take nema.

Zaune take a harabar gidan ta kurawa kasa ido guri ɗaya take kallo, ba komai a ranta sai son tuno wani abu da take ji cikin kwana biyunnan game da gidan da inna take yawan sata ta gyara.

Tabbas akwai wani abu mai muhimmanci dake tattare da gidan, amma baza ta iya cewa menene shi ba.

Da sallama ya turo kofar gidan  shigo yana mai cike dason ganin wanene a cikin gidan nasu tunda yasan daddy bai zo ba.

Cakk ya tsaya yana kallonta zcyrshi na bugawa, wata zuciyar tana bashi shawarar ya isa gareta ɗayar tana hanashi, tunda bayi da tabbas ɗin samun lafiyarta, sbd yanzunma malamin dake musu jinyanne yace yazo a gani ko an dace.

So yake yabar wajen tunkan ta ganshi, tunda yaga kamar tayi nisa cikin tunani da alama bata san da shigowarshi ba ma.
Idon shi ya gagara janyewa daga kanta ,kafafuwanshi kuma sun gagara yin motsin kirki da zasu bashi damar barin waje, shi bai shiga ba kuma bai koma ba.

A hankali ta ɗago idanunta ta sauqesu kanshi, wanda hakan yayi sanadiyyar qara qarfin bugun zuciyarshi.

Sun jima suna kallon juna kafin ta mike ta fara takowa zuwa inda yake, fiskarta na nuna alamun tsoro da mamaki.....

*Alhamdulillah, 'yan uwa anan zan dakata, in sha Allahu sai nan da bayan sallah idan Allah

yasa muna cikin rayayyu.*
*Allah ya yanuna mana farkon wann wata mai alfarma lafiya da kuma qarshensa, Allah ya bamu ikon yin ibada cikin koshin lafiya da tsaftaťacciyar zuciya, Allah kuma ya karb'i ibadunmu, ya biya mana buqatun na alkhairi.*

*Yan uwa idan akwai wanda na taba batawa rai yayiwa Allah ya yafemin, nima na yafewa kowa, Allah ya sadamu da alkhairi*

*RAMADAN MUKARRAM.*
[8/1, 6:46 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljajal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*125*130*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*K*iranshi mummy tayi kan yazo ya ɗauki miemie da daddare snn kuma ta sanar dashi washegari za a turo mai tayata aikin gida.
A inda sukayi maganar nan ya watsar da ita ya shiga sabgoginshi.

Mummy ko ganin har goman dare yayi baizo ba ta shiga cika tana batsewa, sai mita takeyi, Habib ya nuna mata matsayinta ya nuna mata ba ita ta haifeshi ba, snn daga yanzu ya nuna bazai iya yin adalci tsakanin Mie mie da  Bintu ba.
Washegari ta samu daddy da maganar tare da nuna mishi tsantsan b'acin ranta kan abunda Habib yayi mata, wanda shi kuma Daddy mamakin rashin komawan Miemie yayi dan mummy da bakinta tace mishi Miemie zata koma a jiyan, har ya kirata ya mata nasiha da fatan Allah ya basu zaman lafiya ashe bata koma ba.
Hakan yasa a lokacin yace maza mummy tace mata ta shirya driver ya maida ta da safen duk da mummy ba haka taso ba taso Habib yazo da kanshi ya ɗauketa su koma.

Kawarta da kanwarta ta kira suka shirya Miemie shirin amare dama tun jiya taje saloon aka

zana mata lalle, gyaran jiki kuma dama kullum cikin yinshi suke.

Hmm akwai gasa kenan a gidan Habibullah.

Shigowar mota cikin gidan yasashi lekawa ta tagar kitchen .
Haushi ne ya cikashi ganin su miemie, dan shi tuni ya manta da zancen ɗauko ta.

'yar karamar tsaki yaja a zcyrshi yana tunani  ba abinda dawowarta zai qareshi dashi sai takura
.
Da sauri ya qarasa haɗa tea ɗin da ya keyi ya ɗauki plate na soyayyar kwai da  tanada sbd karyawar gimbiyarshi kafin ta farka daga baccin wahalan da takeyi.

Yana shiga ɗakin yaji ana kwankwasa musu kofa. Haka yaje ya buɗe kofar yana mai jin haushin su daga ita har waɗanda suka rakota.

Ja da baya yayi suka shigo ɗaya bayan ɗaya, dukansu suka kame kan kujera.
Kawar mummy ya fara gaida wa ta amsa a yatsine tare da qara ɗaura ɗamarar ci mashi mutunci fiye da  yanda ta yi niyya tun daga gida.
Gaisheda Kanwar mummy yayi, ita kam ko amsawar ma bata yi ba sai muguwar hararar da da zabga mishi, wanda zamu iya cewa aikin banza takeyi  dan baisan tanayi ba tunda bai  kalli fiskar ko ɗaya daga cikinsu ba.

Ta buďi baki zata fara zazzaga mishi masifa kenan ta ji miemie ta zabga wata firgitacciyar qara wanda ya razana su gaba ki ɗaya.
Kafin suyi wani yunkuri tuni tayi hanyar fita falon a guje.

Cikin azama Habibullah ya bi bayanta su kuma sai ihun kiran sunanta sukeyi.

Yana cafko ta ta qara kwalla wata qarar da tafi waccar sauti idanunta duk sunyi waje.
Kafin su qaraso tuni ta sume .

Rike kanshi yayi tare da rintse idanunshi yana salati, sbd abinda tayin yayi kama qwarai da wanda Bintu tayi kwanakin baya.
Me yake faruwa a gidanshi ne?"
Ya tambayi kanshi.

Jin kiran da su aunty lami suke mata mai haɗe da sautin kuka ya sashi buɗe idanunshi yana binsu da kallo ɗaya bayan ɗaya, kafin ya sauke idanunshi kan Miemie dake kwance shame shame sun jikata sharkaf da ruwa.

Kinkimarta yayi da zummar su kaita asibiti ta kuma ware idanunta a kanshi.
Wannan karon tsabar firgitar da tayi ihunma ya gagareta sai karkarwar da takeyi, take kuma ta saki fitsari a jiki wanda hakan ya matukar tsorata shi yayi saurin sauketa cike da faɗuwar gaba.

Ko ba a faɗa ya fahimci itanma shi ɗinne bata son gani.

Cikin barin jiki da bayyananniyar tsoro take nuna shi da yatsarta, bakinta har rawa yakeyi amma sam ta gagara furta koda kalma ɗaya.

Menene?"
Kawar mummy ta tambayeta cikin faɗuwar gaba tana kuma binsu dukansu biyu da kallo.

Janyeta kanwar mummy tayi suka shige ɗakinta ta shigar da ita toilet dan ta tsabtace jikinta.
Kawar mummy da take binsu da kallo ta shiga wani nazari, take kuwa wata muguwar fargaba ta rufeta.

Me ke shirin faruwa dasu? Ba dai aikin da sukayi ba ne yake so ya koma musu?"

Da sauri tabi bayansu, nan ta tarar sun fito daga ban dakin amma sam miemie bata cikin hayyacinta, har yanzu kuma jikinta bai bar karkarwan ba.

"Ya zamuyi yanzu."
Kanwar mummy ta tambaya cikin alhini.

"Gida kawai zamu koma da ita asan abinda za ayi."

"Ba asibiti ba ? "
Ta kuma tambaya.

"Muje gidan dai, banyi tsammanin akwai buqatar muje asibiti ba."

Cikin d'aurewar kai kanwar mummy ta kuma cewa, " mu bari zuwa anjima mana to mu gani, daga dawowa sai komawa gida ? "

"Baza ki gane bane Saudatu, bakiga shigowarta gidan ya kawo wnn matsalar ba, ko baki lura kamar ma ba ta son ganin shi Habibun ba ? "
Da haka dai suka yanke shawarar maidata gida dan asan abunda za ayi.

Dakinshi ya koma cikin kullewar kai, yana mamakin faruwar wnn al'amarin.
Bintu ya tarar zaune bakin gado tayi zuru tamkar akwai abinda take sauraro.
"Kin tashi ? "
Abinda ya fara ce mata kenan yana gyara yanayin fiskarshi.

Cikin disasshiyar murya tace "Me ya faru naji ihu a cikin gidannan."

Maxewa yayi yace "Nima abinda naji kenan na fita ashe ba anan bane gidan neighbours ne."

Wani kallo ta mishi tamkar bata yarda da zancenshi ba, shi kuwa ya juyar da kanshi ga brkfast din da ya kawo mata.

"Bismillah, yace bayan ya matso da shi kusa da ita.
Kallon plate din tayi kamar zatayi magana sai ta fasa.

"Sauko in baki."
Ya sake fad'a.

Hararar kasan ido ta bishi dashi kafin kamar bata son mgn tace "Dama kullum kaike bani ne ? "

"Ko ba kullum nake baki ba ina baki kam dai ko."

"To yau bana so."
Ta fad'a tana qara d'aure fiska.

"Tsare gida, mutuncin dandi."
Yace yana mata dariyar tsokana.

Ganin da gaske yake batan zaiyi ta sauko ta bud'e plate din ba tare da ta sake kallonshiba.

Kasa kasa tace "Ba dan ina jin yunwa ba babu abinda zai sani cin jagwalgwalonka."

"Daure dai kici bari in had'a miki ruwan wanka."
Yace mata yana mai nufan toilet.

"Ashe dai ya iya."
Ta fad'a tana kara kaiwa bakinta.

Tass ta cinye ta tashi ta shiga wanka, kafin ta fito ya je ya d'auko mata kayan da zata saka snn ya leka d'akin Miemie, ya sameshi a kulle, hakan ya tabbatar mishi da ba sa gidan kenan.

Mmn larai ya kira ta tabbatar mishi da suna gida, dan shakkar kiran mummyn yakeji tunda jiya yaki bin umarninta yau kuma ga abunda ya faru, dad'in dad'awa yanayin da suka shigo dashi d'azu yasan da wata a qasa, bayan haka har suka tafi da ita ba tare da ya sani ba kuma bai bi bayan su ba har na tsawon lokaci.

Aunty Nafi ya kuma kira ya sanar mata abinda ya faru, cikin d'imbin mamaki take ta jajanta al'amarin, daga nan ta ce mishi su had'u a can gida anjima kad'an zata je.

Kicib'is sukayi a kofar d'akin, ita zata fito shi kuma zai shiga.
Hannayenshi yasa ya tare bakin kofar yana binta da wani irin sihirtaccen kallo,
qasa tayi da kanta hakan yasashi murmusawa dan shi gaba d'aya yau dariya take bashi, wai

Islam da ta maida shi tamkar wani kakanta shine yau take kin had'a ido dashi.

A marairaice yace
"Ina zakije  kuma? "

Bata yi mgn ba kamar yanda bata d'ago ta kalleshi ba.

A tab'are ya kuma ce cewa "Yanzu Islam baza ki zauna kiyi jinyata ba, ni da bani da lafiya, ki ga fa cizon da kika yi min har zazzab'i ya saukar min..

Jin bata yi magana ba ya sake kofar yana kokarin shiga d'akin ya kamo hanunta ya maidata ciki.

"Kinga sanyi nakeji, kwanciya zanyi ki lullub'eni kinji."

Cikin azama ta kwace hanunta had'e da yin kwafa tunowa da tayi, jiya haka ya mata dabara yace sanyi yake ji ta lullub'eshi harda wani marairaicewa, itako har wani tausaya mishi takeyi ta d'auko abin rufa, daga kokarin rufa mishi ya jawota ya d'and'ana mata kud'arta.

Tunowa da haka da tayi yasata saurin barin d'akin, shi kuma ya bita da dariyar shakiyanci.

Saida ta fita ya zauna ya shiga tunanin abinda ya faru da miemie, abun kamar almara, Bintu tayi ta warke yanzu kuma miemie.

A kasalance ya tashi ya shiga wanka tunanin bai bar zcyarshi ba har ya qare shirinshi.

D'akinta ya nufa tana zauna ta baza kayan english wears da aunty Nafi ta kawo mata tana binsu da kallo d'aya bayan d'aya tana tab'e baki.

Kusa da ita ya zauna yana duba kayan ita kuma kokarin b'oyesu takeyi yaki bata damar yin hakan.

"Zanje gida, in dawo yanzu, me kike buqata."

"Ka gaishesu dukansu, na babana double."
Ta amsa ba tare da da yarda sun had'a ido ba.

Ashe kina da kunya haka ban sani ba ? "
Ya zolayeta yana dariya.

"Me za a kawo miki to ? "
Nanma shiru tayi tamkar bata jishi ba.

"Kada kiyi aikin komai yanzu zan dawo kinji."
Ya fad'a yana mikewa dan ficewa daga d'akin.

"A dawo lafiya Allah ya tsare."

"Ba rakiya ? "

Shiru tayi ta maida kanta ga kayanta ta fara tattarasu tana mayarwa cikin jakar kayan.

"Bashi kikaci."
Yace kafin ya fita daga d'akin.

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

Dawowarsu tare da miemie ba karamin d'agawa mummy hankali yayi ba.
Cikin rawar baki ta fara tambayarsu abunda ya dawo dasu tare, tana kuma karewa miemien da kenan gaba d'aya a hargitse kallo, kayan da ta tafi dasu ba dasu ta dawo ba, kuma ba wani dad'ewa sukayi ba.

Kanwarta ce ta yi mata bayanin abinda yake faruwa.
Cikin tashin hankali take kallon kawarta, ga abin magana ba damar yi.

"Mummy irin ciwon Bintu ? "
Sukaji iman ta tambaya.

A tare suka kalleta cikin fad'uwar gaba.

Miemie kam ba magana sai ido da take rarrabawa.

"Ina mijinnata kuma ? "
Mummy ta tambaya.

Nan suka fara zazzaga mata bayani wanda babu abinda suka kara mata sai haushi da bacin rai.
Dan ce mata sukayi tunda miemie ta fad'i ya shige d'akinshi bai kuma fitowa ba har suka bar gidan.

Kwafa tayi tace zaizo ya sameni."

Sun jima a wajen suna jimanta al'amarin, qarshe kawar mummyn tace ita zata nema mata magani.

Tare suka fita da mummy da sunan zata yi mata rakiya nan sukayi ta shawawrwarin yanda zasu

b'ullowa al'amarin dan ga dukkan alamu reshe ne ya juye da mujiya tunda ga Bintu ta warke miemie kuma ta karb'a.

Kusan tare suka iso da aunty Nafi gidan sbd haka tare suka qarasa ciki.
Aunty ce ta fara gaisheda mummy snn shima ya gaisheta.

"Me ya kawo ka, ai na yi tsammanin bazakazo bane kana tare da 'yar gwal, ita kuma wnn ko oho, ta mutu ma babu abinda ya dameka ko ? "
Ta fad'a cikin nuna b'acin ranta.

"Ayi min afuwa Mummy na shiga ne domin in shirya, kafin in fito kuma na samu sun riga sun tafi.

"Ka kyauta ai."
Tace fiskarta sam babu walwala.

"Allah ya huci zuciyarki."
Ya fad'a cikin girmamawa.

Tab'e baki tayi ta wuce aunty Nafi tabi bayanta.
A hankali ya tashi ya bisu.

"Sannu mie mie."
Aunty nafi ta fad'a tana mata kallon tausayawa.

Da ido ta amsa mata batayi magana ba.
Yana shigowa ta mike a firgice ta fara neman wajen b'uya.

Rikota aunty nafi tayi dan kada ta jiwa kanta ciwo nan kuma ta fara fizge fizge tamkar mai hauka sabon kamu..........
[8/1, 6:47 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*130-135*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*F*ita Habib" aunty nafi ta fad'a hankalinta a tashe.
Da sauri ya bar d'akin ya nufi wajen Mmn larai.

Saida ya fita ta daina buge bugen da takeyi.
Iman kuwa wani irin kuka mai ban tausayi ta saki tana maimaita Innalillahi a bayyane.
Itama kanta mummyn kukan takeso tayi amma ta ari dauriya ta yafawa kanta.

A mutunce suka gaisa da Mmn larai take jajanta mishi lamarin.
Shiru sukayi na d'an lokaci kowannensu da abinda yake saqawa a ranshi, har aunty nafi tazo ta iskosu .
Bayan sun gaisa nanma suka jajantawa juna, aunty tana ta nuna mamakin ta na abinda ta gani yanzu dan taga tabbas ita d'inma Habib ne bata son gani.

Bud'an bakin Mmn larai sai cewa tayi, "Ni dai a tunanina cikin biyune za a yi d'aya, ko dai cikin gidan Alhaji qarami akwai wasu b'oyayyun halittu ko kuma kaikayine ya koma kan mashekiya."

"Kamar yaya ? "
Suka had'a baki wajen tambayarta."

"Allah masani, shi yasan abinda ke b'oye da bayyane shi ne masanin gaibu, addu'ar da zamu yi kawai itace Allah ya bayyana wnn b'oyayyen lamarin dan shi kad'ai ke da ikon yin hakan."
Ta basu amsa cikin sanyin murya dan bata so uwar d'akinta taji maganar da suke tattaunawa akai kenan.

"Amin."
Suka amsa mata, ita dai aunty Nafi taso ta fahimci inda mmn larai ta dosa, shi ko Habibullah, yaso ya kara mata wata tambayar, amma amsar da ta basu na cewa Allah ne masanin gaibu yasashi had'iye tambayar.

Basu wani dad'e ba Habib yace zai koma gida dan dai shi kam yana zaune ne amma gaba d'aya hankalinshi na ga Islam da ya baro ita kad'ai a gida, ga kuma Mmn larai ta qara sa mishi tsoro, indai b'oyayyun mutanenne da gaske yana tsoron kada su cutar mishi da ita gida ba kowa.
Sbd haka ya sallamesu ya tafi, duk da aunty ta so ya d'an kara zama kad'an gudun kada ya jawo wata maganar gun mummy .

Sai dare daddy yasan da abinda ya faru.

Al'ajabi sosai ya nuna, washe gari ya nemi Habib da maganar kaita gurin magani, nan kuma mummy tace ai tun jiya da abin ya faru aka nemo mata magani, kuma mai maganin yace kada a had'a mishi maganinshi da na wani.

Saida ta kwana biyu da wnn matsala Bintu da ji labari, a ranar kuma suka je tare da Habib dan dubata.
Iyakanshi gaisawa da mummy ya tambayi mai jiki dan baya shiga inda take.

Bintu ce dai bayan sun gaisa ta shiga d'akin da Miemien take, nan ta taddata zaune sai raba idanu takeyi kamar ma a firgice take.
Duk ta zama wata iri tamkar ba Miemie 'yar kwalisa mai ji da kanta ba.
Ko gaisuwar da bintu ta mata bata amsa ba, sai kallonta da tayi na d'an lokaci ta kawar da kanta.

Zama tayi tana tofa mata addu'o'i, tana jin kwalla suna taruwa a idanunta sbd tausayawa halin da ta ganta ciki mummy ta shigo.

"Lallai yarinyar nan kin san kan munafurci, tofe tofen me kuma kike yi mata ? "
Mummy ta fad'a fiskar nan a d'aure kamar hadari.
Sbd ganin da tayi musu tare ya bala'in bakanta mata, dukansu biyu sun yi fresh, tsaf dasu da gansu kasan basu da wata matsala, sai wani kaffa kaffa sukeyi da juna.

"Addu'a nake tofa mata mummy."

"Rike addu'ar ki munafuka, yau kwananta nawa da ciwon kika gagara zuwa ki duba ta dan bakar zcy sai yanzu da kika dama zaki wani zo ki ishe mu da tofe tofe har da hawayen munafunci.

"Yi hakuri mummyyau naji rashin lafiyan."
Ta sake amsawa a sanyaye.

"Eh, lallai kuwa, abun ya faru cikin gidan kuma kina ciki kice sai yau kika ji, to aniyarki ta biki, idanma kun had'a kai da iyayenki kun cutar min da 'ya asirinku zai tonu, kuma zaman miemie a gidan Habibu daram dakam saidai bakin ciki ta kashe ku, dama ku kauyawa haka kuke , idan idan idonku ya d'an bud'e sai ku nunawa duniya kunfi kowa wayewa da sanin kan duniya, munafukai dangin mayu, fice min daga d'aki, makwad'aita."

Zafin zagin da mummy tayi mata yasa kwalla suka surnano mata tayi saurin gogewa.
Barin d'akin tayi da sauri tana kokarin b'oye damuwar dake kan fiskarta.

Can gurin mmn larai ta sameshi suna hira ta zauna aka ci gaba da yi da ita, duk kokarinta na son b'oye damuwar da take ciki saida ya gane, saidai kuma da ya tambayeta dalilin canjin da ya gani a tattare da ita sai tace mishi, halin da miemie take ciki ne yasata cikin damuwa.

Fitarta daga d'akin ba da jimawa ba, aunty lami kawar Mami ta kira ta take shaida mata cewa malaminsu ya bata tabbacin cewa  mummunan aiki aka yiwa miemie acan kauyen su Bintu, karyashi zai d'au lokaci mai tsawo, idan kuma ba a tsaya su Bintu sun warware aikin da kansu ba dole har sai sun kashe auren abun zai karye, idan kuma auren bai mutu ba kuma suka ce zasu warware aikin ta wajensu dan rabata da matsalar haukacewa zatayi gaba d'aya. karairayi dai kala kala tayi ta jera mata kamar yadda malaminsu ya shirga mata itama.

Hankalin mummy yakai kololuwar tashi, a fili take cewa dolema ta tashi tsaye kada a haukatar mata da 'ya, batun mutuwar aure kuma baima taso ba, dan idan haka ya kasance burinta bai gama cika ba kenan.
A ganinta gwara dai miemie ta dad'e a wnn hali ta samu sauqi daga baya akan ace auren ya mutu.

Suna nan zaune sai ga mummy ta zo ta tsaya kansu kamar wata dogari, batayi wata wata ba ta d'auke ta da mari saida suka razana dukansu.

"Me tayi miki mummy ? "
Habib ya tambayeta cikin rawar baki da qunan rai.

Idonta jazur ba komai a ciki sai zallar b'acin rai ta zabga mishi harara tace "ko zaka rama mata ne, shanyayye sallamamme, zo ka rama mata, nace kazo ka rama mata."
Ta karishe cikin d'aga murya tana haki.

Kallon bintu da ta kifa kanta jikin mmn larai tana shessheka yayi ya maida kallonshi ga mummy yace "Bazan rama mata ba sbd ke uwace a gareni amma Allah yana gani shi zai sakawa wanda aka zalunta."

Rike bakinta tayi tace "iye, dama ai na sani daga kai har ubanka basu barku banza ba, to ni nan zan yi maganinsu, sai na nuna musu cewa ba a ja dani a zauna lafiya, zasu san cewa basu ci bulus ba, har ni zasu asircewa 'ya su hana ta zaman gidan miji, wato tayi karyar ciwo ta tafi kauyensu dan ta had'u da iyayenta su cutar min da'ya, to ta Allah ba tasu ba, kuma ni nan sa'adatu sai na warware duk wani kulli da sukayi daga kan miemie har kai da ubanka,."

"Mummy."
Ya katseta cikin b'acin rai.

"Ba laifinka bane Habibullah, duk abinda zakayu min bazan ga laifinka dan ba a cikin hayyacinka kake ba, dama ni tunda naga  rawar kafar da kakeyi a kan yarinyar nan tun tana 'yar karamarta nasan basu barka banza ba, idan ba haka ba baza ka ki kula 'yar uwarka kan wata bare, 'yar matsiyata dangin mayu."
Ta karishe  har tana cije hakoranta.

Sautin kukanta ta qara dan jin qazafin da mummy take mata.

Cikin b'acin rai Habibullah ya d'agota ya shiga share mata hawaye, yana bata haquri wanda hakan ba qaramin qara qular da mummy yayi ba.

Kwafa tayi ta qara da cewa "Muddin kina son kanki da lafiya kuyi gaggawar zuwa ku karya asirin da kuka yiwa 'yata idan ba haka ba kema bazan tab'a barinki ki zauna lafiya ba.

Da sauri habib yaja Bintu suka bar wajen dan gudun abunda b'acin rai zai sashi ya aikata.

Suna barin wajen ta koma kan Mmn larai da zagi tayi mata tatas tayi gaba tana huci.

Gidan aunty nafi suka biya ya bata labarin abunda mummy tayi nan suka had'u sukayi ta bawa bintu baki har suka samu ta sake, saidai fa can cikin zcyrta ita tasan abinda take ji idan ta tuna qazafin da akayi musu ita da iyayenta.

Tun daga ranar basu qara d'ago maganar ba, haka kuma Habib bai qara zuwa gidan ba, idan yana son gaisawa da daddy gurin aikinshi yake binshi.

Ita kuwa bintu bawai ta manta da abinda mummy tayi mata bane saidai kulawar da habib yake bata da kokarin mantar da ita duk wata damuwarta, da kuma riritata da gwada mata soyayyarshi mai tsayawa a rai yasa ko kad'an bata nuna damuwarta.

Sati guda mummy taga Habib bai lekasu ba ba ko kiran waya, ta samu daddy da maganar.
Ba tare da b'ata lokaci ba daddy ya qirashi dan jin dalilinshi na rashin zuwa .
Kamar yana jira ya shiga zayyane mishi abunda mummy tayiwa bintu.
Cikin b'acin rai daddy ya shiga yi mata fad'a kan abinda ta aikata, snn ya ritsata sai ta fad'a mishi inda ta jiyo cewa su suka asirce mata 'yarta.
Nan kuma ta shiga kame kame.
Ya kuma cewa "Indai miemie asiri akayi Mata to itama bintu shi akayi mata kenan, idan kuma ta yarda cewa iyayen bintu sukayi mata, to ita mahaifiyar miemie ita ta fara yiwa bintun."

Sauke kanta tayi tayi ta bada haquri da cewa bazata qara aikata hakanba, ammafa na ciki na ciki.

Cikin sati biyu sau d'aya Habib yazo gidan nanma bai wani dad'e ba, bai kuma nemi ganin miemie ba ya bar gidan.

Wasa wasa miemie takai wata biyu tana fama da abu d'aya ta zama so silent bata son magana, ga yawan razana, kullum kuma a tsorace take ko toilet zata shiga sai an rakata.

Ko da yaushe daddy cikin nema mata magani yake saidai har yanzu ba canji sai ma abinda ya qaru, dan yanzu muddin habib ya shigo gidan ko da bata ganshi ba ta rika ihu da buge buge

kenan har sai ya bar gidan.

Zugan aunty lami tabi ta bi Bintu har gidansu, bayan fitan daddy .

D'umamen tuwon masara da miyar busasshiyar kub'ewa suke ciyar da juna cikin annashuwa da shauki.
Ba sallama ta bankad'a labule ta shigo dan duk a tsammaninta Habib bayanan.
Suko harkar gabansu kawai sukeyi basu ma san ta shigo ba.

Lomar karshe da ta sa mishi a bakiya had'a da yatsunta ya ciza.
"Wash." tace tana yarfe hannaye.

"Mu gani."
Yace yana mata dariyar mugunta.
Janye hanun take kokarin yi daga rikon da yayi mata shi kuma yaki bata damar yin hakan ya fara hurewa kafin yace "sannu to yi hakuri akasi aka samu."

Maqe kafad'arta tayi tace "Naki sai na rama."
Tana fad'a ta cafko hanunshi zata kai baki yayi sauri fizgewa ya bar wajen da gudu yana mata dariya.
Bin bayanshi tayi a guje tana cewa bata yarda ba sai ta rama, da haka suka rika guje guje cikin falon suna zagaye kujerun dake ciki.

"Wayyo Allah na."
Ta fad'a tare da duqawa tana rike cikinta.

Da sauri ya matso kusa da ita ya duka, cikin kulawa yake tambayarta menene ?

Caraf ta rikeshi tana kyalkyata dariya "Wa na kama."

"Habibullah ."
Ya bata amsa yana marairaicewa.

Dariya abin ya bata ,tana dariyar tace "Ko me zakayi yau sai na rama."

"Tsaya to banda  cizo, fad'a min me zan miki ki huce."

"Goyo ." ta amsa tamkar dama jira take ya mata tambayar.

Murmusawa yayi ya duka ,dama yasan  hukuncin bazai wuci haka bane.

Nad'e skirt d'inta tayi ta d'ale bayanshi tana cewa "Kuma sai ka zagaye palourn nan dani sau goma."

"An gama ranki shi dad'e."
Ya fad'a lokacin da yake mikewa da ita.

Dirowatayi da sauri lokacin da sukayi ido hud'u da mummyn dake tsaye bakin kofa tana aika musu da kallon takaici.

Kallonta yayi zaiyi magana yaga ta kurawa kofar falonsu ido, hakan yasashi maida kallonshi zuwa gurin.

Tamkar bai gane ma'anar kallon da takeyi musu ba yace "Sannu da zuwa mummy bamuji shigowarki ba... .
[8/1, 6:49 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*135-140*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*T*ayaya zaku san da shigowana kuna ta shiririita, abinda ka zama kenan ko aikinma ka daina zuwa kenan kana nan kana biye mata kuna ta zuba shirme ."

"Bismillah."
Yace yana nuna kujera ba tare da ya damu da abunda tace ba.

"Ba abinda ya kawoni ba kenan, in dan gurin zama ne akwaishi a inda na baro, jan kunnenki na zoyi, ki gaggauta zuwa gurin iyayenki ku lalata abinda kukayiwa miemie, idan ba haka ba matakin da zan d'auka bazai miki dad'i ba, na gaya miki."
Ta maida akalar maganarta ga bintu.

Tuni idanun bintu suka ciko tayi saurin barin wajen ta shige d'akinta.

"Mummy me yasa kikeyin haka ne ?  Lokacin da Islam tayi nata ciwon, cikin 'yan uwanta babu wanda yasa zargi a ciki, me yasa ke baza ki yarda da kaddara ba."
Habib ya fad'a a tausashe.

"Ni zaka gayawa kaddara Habib, tun kafin a haifeka nasan kaddara, ga a bu a bayyane kuce kada a fad'a dan baku son gaskiya, idan ku an shanyeku ni ba ashanye ni ba sbd haka dole in biwa 'yata hakkinta.
Batun ita ta fara ciwo da kuke cewa wnn kuma ku ta dama, matsalarkuce, ni dai na fad'a mata, idan taki ji baza taki gani ba, saura kuma ka fad'awa alhaji nazo gidanku na zagi 'yar gwal kamar yadda kayi ranan, tunda duk kun zama sallamamu"
Tana kare maganar ta ta juya ta fice.

"Hasbunallahu wa ni'imal wakeel, Allah ka kawo min agaji."
Ya fad'a bayan ya zauna kan cushion hannayenshi rike da kanshi.

Kwance ya sameta tayi ruf da ciki, tayi luf tamkar mai bacci.
Sau uku yana kiranta tana shiru.

Kusa da ita ya kwanta ya mirginota suna fiskantar juna saidai har yanzu idanunta a rufe.

Murya a shaqe yace "My islam dan Allah ki daina d'aga hankalinki kan maganganun mummy, zafin ciwon miemie ne yake sata duk wad'annan abubuwa."

Idanunta a rufen tace "Zafin ciwo kuma sai ta sauqe a kaina ? Lokacin da nayi nawa ciwon kan wa innata ta sauqe ? "

"Yi haquri dear, kinsan kowa da yanda yake karb'ar kaddara idan ta sameshi."

"Hmmm."
Kawai tace ta sake lafewa.

Cikin son basar da zancan da son cire mata tunanin yace "Muje na miki goyonki ko kin fasa."

"Ni bacci nakeji."

"To muyi baccinmu abinmu."
Ya fad'a yana dad'a kwakumeta.

"Wai yau baza ka fita bane."

"A hakan, bayan matata ta makance, in fita in barta dawa."

Da sauri ta bud'e idon tana cewa "Wa, wlh bintun baffa bata makanceba."

"Aradu na d'auka ta makance ne."
Ya fad'a yana kwaikwayon muryarta."

Murmushi tayi mai sauti  ta kai mishi dukan wasa a kirji tace "ka tabbatar ai, yanzu zaka fitan ko ? "

"Um, um, sai munje na miki goyon ki."

"Na fasa."
Tace a takaice.

"Nima na fasa fitan yasin, musha baccinmu mu more."
Ya qarasa yana gyara mata kwanciya a jikinshi.

Itakam bintu maganganun mummy ta shiga tunawa shima din dai basarwa kawai yakeyi amma abin yana damunshi.

Da haka baccin ya kwashesu dukansu kowannensu da abinda yake saqawa a zcyrshi.

Wasa wasa miemie takai watanni Biyar cikin wnn lalura, idan ka ganta gata nanne kawai, ita ba mai hauka ba, ita ba mai cikakken hankali ba, ihu da buge buge kuma idan Habib ya shigo gidan sai abinda ya qaru, duk wani magani kuma da daddy yake kawowa karb'a kawai takeyi amma bata mata amfani dashi gudun kada maganar malaminsu ya tabbata miemie ta haukace gaba d'aya, haka dangin baban miemie suna nasu iya kokarin har sun buqaci ta basu ita suje suyi mata jinya a wajensu nanma taki, gudun tonuwar asirinta.

Haka dai rayuwar take gungurawa da miemie ta zama abar tausayi, su kuwa Habib da Bintu suna rayuwarsu cikin kwanciyar hankali, tun zuwan da bintu tayi  gidan mummy tayi mata tijara bata kuma zuwa ba, saidai ita mummy ta biyo ta har gida idsn 'yan rashin mutuncin sun motsa tun abun yana d'aga mata hankali har ta saba.
Daddy kuwa har gidan yake zuwa duba lafiyar bintu, tana kuma yin waya sosai da Mmn larai, wani lokacin itama mmn larai takan saci jiki ta je gidan bintun.

Ganin abin ba na qare bane kuma har yanzu malaminsu sai dad'a tunzurata yake  kan lallai su takura a karya asirin ta wajen su bintu, a cewarsu bawai bazai iya bane saida i idan shi yace zai yi za a samu akasi dan sai miemie ta tona duk abunda suka aikatawa bintu a baya.
Hakan yasa mummy da qawarta suka shirya zuwa yusa dan su samu iyayen bintu ayi ta ta qare.

Daddy na fita ta hau shiri.
Iman da Mmn larai aka bari da bintu su kuma suka kama hanyar yusa.

Sunyi nisa da tafiya tsautsayi ya ritsa dasu suka had'u da hatsari  dan wnn ba mai kyau bane, asalin drebobi sai sun yi taka tsantsan suke wuce wajen.

Lokaci guda aka cika gurin ana kokarin fito dasu daga cikin motar.
A daidai lokacin kuma Habib suka zo zasu wuce dan zuwa yusa shi da abokinshi.

Ganin yanda hanyar ta cika babu wajen wucewa yasa suka parker motarsu suka qaraso da qafa.

Mamaki qarara bayyane a fiskar Habib yake bin su Mummy da kallo lokacin da ya isa wajen, tambaywr kanshi yake me ya kawo su hanyar yusa.

Taimaka musu akayi aka sasu cikin motar Habib kamar yadda ya buqata, dukansu biyu sun fita hayyacinsu, sai tashin nishinsu kake ji.

Daganan suka juyo dasu suka dawo cikin jalingo, direct sai Specialist hospital suka wuce dasu.

Saida aka karb'esu kafin habib ya kira daddy da aunty nafi ya shaida musu abunda yake faruwa.

Ba da jimawa ba daddy ya iso, daga baya kuma aunty nafi da mijinta, sai kannen mummyn kuma da suka zo suma.

Bayan wucewan wasu lokuta likitocin suka fito inda suka nemi ganin wad'anda suka kawota, daddy da habib suka je, nan suka shaida musu cewa, mummy ta samu karaya a hanu da kukkujewa sai kuma wani qarfe da ya soketa a kafarta ta dama.
Ita kuma kawarta ta samu karaya biyu a kafarta ta hagu, sai gurd'ewar da tayi a gwiwar hannunta.

Bayan fitowansu aunty nafi taja shi gefe take tambayarshi a inda abin ya faru, nan yake sanar da ita inda suka samesu.

"To me ya kaisu ? "

"Nima tambayar da nake tayi wa kaina kenan sister, kuma tabbas a inda muka gansu yusa suka nufa."

"Ba dai zuwa zasuyi suyiwa su inna rashin mutunci ba kam."
Ta fad'a tana ware idanu .

"To ko ma dai menene gasu sun kare da kwanciya a gadon asibiti."

"Allah ya kyauta."

"Amin."

Saida aka gama musu komai kafin daddy ya kira habib shima ya tambayeshi inda ya samesu, bai b'oye mishi komai ba ya sanar dashi kamar yanda ya sanar da aunty nafi.

Jinjina kanshi kawai yayi bai sake wata maganar ba, daga nan habib ya sallameshi ya wuce gida.

Tun da abun ya faru take tsorace da daddy, tun tana sa ran zai tambayeta dalilin fitarta ba tare da izininshi ba da kuma dalilin ta na zuwa can inda abun ya sameta har ta cire rai, dan sam bai nuna mata ba ko a fiska, hakan yasa ta saki ranta.
Kulawa ta musamman ake basu har suka samu lafiya cikin ikon ubangiji aka sallamesu suka koma gida.

Kwana biyu da sallamosu daddy ya jefo mata tambayar da ta kad'a mata hanjin ciki dan ita sam ta cire ran za a mata wnn bincike.

"Sa'adatu ina kikaje ranar da kukayi hatsari snn me ya fitar dake ba tare da sanina ba."

"Neman maganin miemie mukaje."
Ta bashi amsa a diririce.

"A ina kukaje neman maganin ? "

Shiru tayi tana tunanin amsar da zata bashi ta fitar da kanta.

Ya jima yana binta da kallon takaici kafin daga bisani yace "Wato sa'adatu maganar nan da na hanaki kina nan akanta baki fasa bako ? Da kika kama hanyar yusa idan kikaje me zakiyi ? Me kike tunanin zasuyi miki wanda Allah bai miki shi ba, ko kina tsammanin mutum yana iya cutar da d'an uwanshi ba tare da izinin ubangiji bane ? "

Tabarmar kunya ta fara nad'ewa da hauka , cikin dakewa da nuna cewa itama jarumar kanta ce sai ta hau surfa masifa.
"Alhaji shi kenan ni sai in zuba ido a cutar min da 'ya ba damar inyi magana, ga gaskiya ina gani an taketa ni sai inyi shiru, yarinya tana cikin yanayi wata da watanni ba sauqi amma kuma ace kada in tsaya in nemo mata lafiyarta."

Hankali kwance yace "A ina kenan kike tunanin zaki nemo mata lafiyar ? "

Ido a bushe tace "A inda aka cutar da ita, mutanennan suna son ganin bayan miemie ne, basu

da burin da ya wuce su kashe mata aure amma ku sam baku gani ba damar mutum yayi magana sai kuce kaddara, to ni na gaji ,dole asan abinyi dan baxan zuba musu ido suyi ta cutata ba,'yarsu tana zaune lafiya ni kuma ina nan ina ta faman jinya, duk gurin maganin da mukaje magana d'aya ake jaddada mini, miemie baza ta warke ba sai sun karya asirin da kansu ko kuma idan aurenta da Habib ya mutu, kaga ko idan auren ya mutu burinsu ya cika kenan dama haka sukeso.."

Cikin son ya nusar da ita ya kuma cewa "Wnn fa zargi kawai kikeyi baki tabbatar ba, uwar yarinyar nan babu ruwanta da irin wnn shirme, dan ko da 'yarta ta shiga wnn hali cewa take haka Allah ya tsara, kuma shi da ya d'ora mata shi zai yaye mata, haka akeson mutum ya kasance da yarda da kaddara, haka kuma ake so mace ta gari ta koyar da 'ya 'yanta su tashi da irin wnn tarbiya ba kamar yanda kike yi yanzu ba."

Cikin b'acin rai ta dakatar dashi.
"Dakata alhaji, so dai kake kace kucakar 'yar kauyennan ta fini imani , sanin ya kamata da tarbiya ko, aini bazaka burgeni ba har sai naga kaje ka aurota ka ajiye a gidanka kamar yanda ka aurawa d'anka Habib d'yarta."

Dariya yayi yace "na gode qwarai da shawararki Haj. Sa'adatu ko ince Hajjajo inji d'iyata Bintu."
Har ya sa kai zai fita ya dawo fiskarnan d'aure tamau tamkar bashi ya gama dariya yanzu ba yace "Kuma ina mai gargad'inki muddin kikaje kauyennan kika tayar wa baiwar Allahnnan hankali kan wani shirmenki na banza a bakin aurenki na fad'a miki kenan."
Ya sa kai ya fita.

Bakin ciki ,takaici su suka had'u suka tokare mummy kirji, ji take kamar ta d'aura hanu a kai ta rusa ihu, sai tsaki take taja a wunin ranan .

Tunda Habib ya ji maganganun da mummy take fad'awa daddy hankalinshi ya gaza kwanciya, yaje gaisheta ne zai shiga Allah ya jiyar dashi maganganun sbd haka yayi saurin barin wajen jin kaman daddy zaifito.

Washegari haka ya wuni da tunani har zuwa dare ya yankewa kanshi hukuncin da yake gani shi yafi dacewa.

Yana idar da sallar isha'i daga masallaci gidansu ya nufa, cikin d'akin mummy ya shiga yana jin yanda miemie take ihu da bugebuge daga d'akinsu.

Kan sallaya ya sameta ta idar da sallah tana zaune ta rabka tagumi, ya gaisheta ta amsa a dakile, tana kallon yanda hutu da kwanciyar hankali suka ratsashi .

Yana durkushe kanshi a qasa ya ce "mummy, kiyi min aikin gafara idan abunda zan gabatar a gareki zai b'ata miki rai, hakika jiya naji abinda ya d'aga min hankali ya kuma hanani sukuni , mummy, tunda muke da ke a gidannan ban tab'a jin inda kukayi sa 'in sa da daddy ba sai ta

dalilina da miemie, sbd haka nayi tunani nema mana maslaha, sbd samun zaman lafiya, ko Allah zaisa a dace."
Shiru yayi yana tunanin ta yanda zai gabatar mata mata da abinda yake ganin shine kwanciyar hankalinsu gaba d'aya, kamar yanda itama ta bashi dukkan hankalinta tana jiran jin inda ya dosa...

*To, mai karatu , ko ya zata kaya ?*
*Ku ci gaba da bin 'yar mutan jalingo dan jin a labarin zata qare*
[8/1, 6:50 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W.*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*140-145*
🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*C*ikin fad'uwar gaba take kallonshi wanda shi kuma har yanxu bai d'ago ya kalleta ba sbd nauyin abinda yake kokarin aikatawa.

"Mummy kiyi haquri, miemie 'yar uwatace, bana jin dad'in ganinta cikin wnn hali, snn ku kuma bazan so ku kasance cikin tashin hankali ba."

Shiru ya kuma yi kafin yayi qarfin halin cusa hanunshi cikin aljihun half jafa d'inshi ya fito da nad'add'iyar takarda ya mika mata, har yanzu kuma bai yarda sun had'a ido ba.

Hanunta na rawa ta karb'a zcyrta na harbawa.
"Menene a ciki Habib ? "
Ta tambaya muryarta na cracking.

Qasa ya kuma yi da kai baiyi magana ba, hakan yasa ta daure ta bud'e takardar ta kura mata

idanu.

*Ni Habibullah, na saki matata Maryam (Miemie) saki d'aya ......*

Abinda ta iya karantawa kenan bata qarasa ba ta dunkule takardar tare da furta Inna lillahi wa inna ilaihirraji'uun."

Da sauri ya tashi ya fara tafiya da zummar barin d'akin  tayi saurin dakatar dashi ta hanyar kiran sunanshi.

"Habib, abunda zaka saka min dashi kenan ? Na gode, na gode qwarai Habib da wnn halacci da kamin, na gode."
Ta qarishe tana goge qwallan da suka zubo mata.

Da sassarfa ya bar d'akin gaba d'aya jikinshi yayi sanyi yana jin kamar bai kyautawa mummynshi ba, idan yayi la'akari da cewa da aurenshi miemie ta samu wnn cutar kuma bata warke ba ya datse igiyar dake tsakaninsu.

Wayarta ta d'auka ta rike ta fara zagaya d'akin sai kuma ta fita da takardar rike a hanunta, d'akinsu miemie ta shiga ta iske zaune ta dafe kanta tayi shiru tamkar da akwai abinda take tunani.

"Miemie kin ga abunda Habib ya aikata mana ko, ya mayar min dake 'yar karamar bazawara."
Sai ta fashe da kuka ta zauna dab'as a kasa.

Yana fita kofar gida suka yi kicibis da daddy ya dawo daga masallaci zai shiga gida, kallo yake mishi mai cike da nazari lokacin da yake gaisheshi ganin yanayinshi kamar yana cikin damuwa.

"Yaya dai Habibullah ? "

"Daddy ka bata hakuri."
Abinda ya iya cewa kenan.

"Wa zan bawa hakuri ? "

"Mummy, ka bata hakuri"
Ya sake fad'a tare da saurin barin wajen dan ya tuna a gurin daddynma shi mai laifine tunda ya yanke hukunci ba tare da ya sanar dashi ba.

Kallo daddy ya bishi dashi kafin ya sa kai ya shiga gida da nufin yaje yaji yau kuma me ya had'a Habib d'in da mummynshi.

Dialling wayarta tayi cikin kuka tace "Lami shawararki batayi ba, batayi min rana ba sam, gashi

ni buri  na bai cika ba, miemie kuma ta zama karamar bazawara, cutar da muka sawa bintu ya dawo kanta , yanxu bani da tabbacin zata samu lafiya ko a'a tunda abinda na aikata ne ya dawo mini."

Shiru tayi na d'an lokaci kafin ta kuma cewa "Wani irin kara hakuri kuma bayan kina gani komai ya wargaje min tun ba aje ko ina ba, kina sane da burina na mallakan dukiyar alhaji, kin kuma san ko da ya mutu bani da wani kason kirki tunda yana da d'a namiji ni kuma ban haihu da shi ba. babban burina bai wuce ace miemie ta kasance matar Habib ba dan karshe dole dukiyar nata ita da yaran da zata haifa ne, kinga ni ina da gadon alhaji ita kuma tana da na habib."
Kuka ta kuma fashewa dashi tace.

"Kin dai cuce ni lami, tun farko dama ba aikin da nace ki sa amin ba kikayi, ce miki nayi ki saka musu kiyayyar juna su manta da juna shi kuma habib yaso miemie kika je kika canza mini tsari, gashi yanzu komai ya lalace , kai nidai nayi alawadai da shigowar tsinanniyar yarinyar nan cikin rayuwarmu."

"Mummy ! "
Miemie ta kira ta da kakkausar murya.

A tsorace tayi jifa da wayar ta d'ago tana kallon miemie dake mata kallon kurilla.

Kafin tace wani abu saiga Iman ta fito daga toilet.
Cikin kuka tazo ta durkusa a gaban mummy ta fara magana .

"Mummy sbd abin duniya kika aikata shirka, mummy dama ke kika cutar da bintu ya dawo kan 'yar uwata.
Mummy me daddy ya rageki dashi, mummy wani irin biyayya ne yaya da aunty basu miki ba, wani irin gata ne daddy bai bamu ba, me kika nema kika rasa, kina da gidan kanki, kina da mota, kina da ajiyayyun kud'i a account, duk a jikin daddy da yaranshi kika samu, su yaya sun d'auke mu a matsayin 'yan uwa babu banbanci, mummy damu dake bamu aikin komai a gidannan sai ayi a bamu muci.
Mummy hakan bai isa ki godewa Allah da ni'imar da yayi mana ba, daddy ya hana mu kukan maraici amma ke har tunanin ya mutu kici gado kikeyi ?
Dama ba rikon Allah da annabi kika yiwa su yaya ba dan Abin duniya kikayi ?
Mummy bazan iya wnn abun kunyar ba, bazan zauna a gidannan ba dan duk ranar da asirinki ya tonu bansan da wani ido zan kalli daddy dasu yaya ba, zan koma gurin dangin mahaifina."
Ta juya ga miemie tana kuka.

"Allah ya baki lafiya 'yar uwata, kiyi haquri zan tafi in barki cikin lalura ba da son raina ba ...

Cakk ta tsaya da maganarta tana kallon miemie dake zubar da hawaye.

A hankali ta mike ta tako ta durkusa a gabanta.

"Me ya saki kuka miemie."

Ga mamakinsu sai sukaji tace "Nima bazan zauna ba Iman, binki zanyi mu tafi, bazan iya wnn abin kunyar ba, mummy ta cuce ni ta cusa min soyayyar yaya tun ina 'yar karamata, ina da masoya da yawa amma na kasa sauraronsu sbd son wanda baya sona, yana da wacce yake so ta barni nayi ta rayuwar son maso wani, ashe duk ba dan karfafa zumunci tayi ba kamar yanda take fad'a, mummy tasa munyi ta cin zarafin bintu a gidannan ba tare da tayi mana laifin komai ba, hakkin bintu bazai barmu ba Iman..
Nan itama ta fashe da kukan suka rungume juna.

Mummy da tunda iman ta fara magana ta shiga girgiza kai sam bakinta ya gaxa furta koda kalma d'ayane.

Sai lokacin da miemie ta fara magana ta kuma tabbatar a cikin hankalinta take ta mike tsaye tana kallonsu.
Cikin murna ko kuka ta rasa wanne zatayi.

"Kuyi hakuri ku yafemin, duk abinda nakeyi domin ku nakeyi, so nake na inganta rayuwarku , ku gafarceni kuji tausayina kada ku gujeni, ku nake kallo inji dad'i a rayuwata, ku biyu kawai Allah ya bani idan ku kun gujeni wa zai soni ? ....
Kukane ya kwace mata ta had'asu ta rungumesu dukansu biyu.

Cikin sanyin jiki daddy da yazo jin ba'asi ya juya yana mai jin al'ajabin abunda yaji daga bakin mummy da kuma tausayawa su miemie.

Koda mummy takai mishi takardar ga mamakinta sai taji yace "Haka Allah ya tsara, dama shi aure rai ne dashi, idan lokacin mutuwarshi yazo babu yanda aka iya, Allah yasa hakan shi yafi alkhairi a garesu da mu duka, Allah yayi dama Bintu ce matarshi, kuma ina alfahari da hakan sbd shigowarta rayuwarmu alkhairi ne babba, ta sanadiyyarta Allah ya haska mini abubuwa da dama dake cikin duhu, Allah ya bawa  miemie lafiya,ya bata miji na gari."

Gaba d'aya kwakwalwar mummy ta cushe ta rasa yadda zata fassara kalaman daddy, ita da tayi tsammanin zai kira Habibi ya sashi janye maganar saki, sai kuma buge da gaya mata maganganu.
Hakan yasa take taji zazzab'i ya rufe ta, ya tabbata kowa ya juya mata baya kenan.
Haka taja kafafunta a sanyaye ta bar mishi d'akin tana mai jin sanyi na shigarta.

Washegari kuwa yanda suka fad'a tun da asubah suka had'a kayansu suka je suka sallami daddy cewar zasu koma gun dangin babansu, yayi farin cikin ganin miemie ta samu lafiya.

Bai tsawaita bincike ba dan ya san inda matsalar take kuma shima yana ganin haka zaifi ko uwarsu zata horu sbd yasan yadda ta kwallafa ranta a kansu.
Fatar alkhairi yayi musu tare dasa albarka, ya kuma yi musu nasiha da uba yake yiwa 'ya'yanshi

kuma ya musu alkwarin zai rika zuwa duba su, snn yace duk abinda suke buqata daga gareshi su nemeshi.

Haka suka tattara suka tafi ba tare da sanin mummy ba, sai bayan tafiyarsu da awa biyu ta gane cewa basa gidan, sun barta kenan da gaske.
Ranar haka ta wuni cikin d'akinta ko abinci bata nema ba.

Satinsu biyu a gidan wan babansu, suka shirya suka je gidan Habib.
Bintu da aunty nafi suka samu, bintu ta baje sai d'ura faten tsaki da aka yi da ganyen yakuwa takeyi ba ji ba gani.

Sosai tayi mamakin ganin miemie da lafiyarta dan batasan cewa ta samu Ify ba.

Da fara'arsu suka shigo hakama aunty ta taresu da fara'a, hakan yasa bintu ma ta saki fiskarta suka gaisa a mutunce har tana yiwa miemie barkan samun Ifyrta dan taga zahiri .
Saida ta gama sambad'ar abincinta su aunty suna hiransu da su miemie, kafin ta mike dakyar dan ba cin wasa tayiwa fatenba.

Kitchen ta shiga ta kawo musu ruwa da abin motsa baki, a zcyrta dtana mmkin hali irinna habib, dan bai sanar da ita miemie ta samu Ify ba.

D'akin habib ta nufa ta sameshi yana ta aikinshi na fama, dannedannen laptop.
Daga baki kofa ta tsaya ta mishi magana yayi shiru tamkar baijita ba.

"Habibi."
Tace cikin d'aga murya.

"Aspen."
Yace ba tare da ya d'ago ya kalleta ba.

"Habibi."

"Aspen." ya kuma cewa.

"Kayi bak'i nace."

"Ba ya nan nace miki ko baki ji bane ? "

"Ba fa da wasa nake ba da gaske kayi bak'i."

Sai a lokacin ya kallota yace "Kin gama cin abincin rowanne, ina fata yau ba'ayi over feeding yanda aka saba ba? "

Har ta juya zata tafi ya ce "Su waye bak'in ? "

"Su matar ka."

"Mata ? "
Ya maimaita yana kallonta.

Juyawarta tayi tayi tafiyarta tana mita ita kad'ai "Ji wai tambaya yakeyi, mata ? Kamar bai san yana da wata matar ba."

Tana zama sai gashi ya shigo, saida yaga miemie ya gane abunda bintu take nufi.
Gaisheshi sukayi dukansu ya amsa musu kamar dai yanda suka saba yi da kafin suka gabatar da abunda ya kawosu ,wato neman gafarar bintu.

Kusan sandarewa bintu tayi jin abun da ke tafe dasu.
Saida iman ta dafa ta tukun ta dawo cikn nitsuwarta.

"Aunty bintu ki yafe mana abubuwan da muka yi ta miki, mun gane kuskurenmu dan Allah ki gafarta mana ni da 'yar uwata."

"Aunty bintu."
Ta maimaita a zcyrta, wata sabuwa.

Daurewa tayi tace ya wuce, Allah ya yafe mana.

Da sauri miemie ta durkusa gaban bintu, kafin tayi magana bintu tayi saurin d'agota, "Na yafe wlh."

"Mun gode aunty bintu."
Suka had'a baki wajen fad'a.

Bintu dai mmki ya kusa kasheta sai jinjina abin takeyi a ranta.
Daga nan suka nemi gafarar su habib tare da rokawa mahaifiyarsu gafara, suma suka ce ya wuce.

Basu dad'e sosai ba suka ce zasu tafi, aunty nafi tace su tsaya ta saukesu.

Tare sukayi musu rakiya, sai a ranar takejin labarin sakin miemie da yayi da kuma barin gidan daddy da sukayi.

Tunda abun ya faru mummy ta rasa sukuni, babu abokin hira, yaransun tafi sun barta, daddy yanzu sam baya shiga harkarta gashi bata saba sakewa da Mmn larai ba, duniyar tayi mata zafi,kullum cikin kunci.

Daddy ne ya kirata Kiran da ya tsinka mata zcy dan yanzu zaman kila wa kala take, gani take kamar ko da yaushe zai iya ce mata tafi gidanku.

Fiska a sake tamkar babu abinda ya had'asu ya fara mata magana.

"Sa'adatu, na kira kine dan na miki albishir na abu biyu zuwa uku.
Na farko dai inaso kisan cewa zaki ci gaba da zama a gidannanne sbd darajar rikon da kikayiwa yarana sbd ban hada su da kowa ba, ko da dai b a dan Allah kikayi ba amma nasan sun samu kulawar da ta dace uwa ta bawa 'ya'yanta.

Na biyu, shawarar da kika bani na auren mahaifiyar bintu ya karb'u kuma har an d'aura auren cikin kwanannan zata dawo nan gidan da zama.

Na uku kuma ina son kisan cewa dukiyar da kike hari na kasata kashi hud'u na bawa Habibullah kashi biyu, kashi d'aya kuma na bawa nafisatu, zan yi managing da kashi d'aya kafin Allah yayi ikonsa a kaina ,ina fata kin fahimta.....
[8/1, 6:51 PM] +234 814 290 6707: 🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*AL'AMARIN UBANGIJI*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*Fasaha Online Writers*

*F.O.W*

*Na Mmn Abduljalal*

🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*145-150*
🥀🥀🥀🥀🥀🥀

*W*ani irin kululu cikinta ya bada batayi aune ba sai fitar tusa ji kake Buum.
Hhhh, su mummy tsabar razana har da sakin bama bamai.

Lokaci guda zufa ya tsattsafo mata.
Yau kam daddy ya tabbatar mata cewa yasan abunda ta aikata.

Wani irin kunya taji ya lullub'eta tamkar ta nitse a kasa take ji.
Wace irin mara sa'a ce ni ? "

Ta ayyana hakan a ranta.

Har ya mike zai fita tayi saurin durkusawa a gabanshi.

"Dan girman Allah Alhaji, ka gafarceni, sharrin shaid'annne."

"Kekasasshiyar zcyr da take manta cewa mutuwa zata iya riskarta a kowace rana cikin ko wace lokaci, sai mutuwar waninta take tunawa har zata iya karaya cikin sauri haka?
Sam ban tsammaci raguwar zcy daga gareki ba, bani ya kamata ke nemi gafara ba sa'adatu dan ni bakiyi min komai ba.

Gafarar wad'anda kika cuta ya kamata ki nema, duk da dai Allah ya nuna miki ikon da buwayanshi,  a yanzu nasan ki tabbatar da cewa ba a ja da *Al'amarin ubangiji*

Rashin ganewa ne yasa na biye miki tun farko, na manta cewa mai aikata abu shike saurin zargin wani yana aikatawa, yanzu kuma kin tunatar dani saidai muci gaba da neman tsari da masu hali irin naki, Allah kuma yasa ku gane hanyar gaskiya ku bita.
Yana gama fad'in haka ya rab'a ta gefenta ya wuce.

"Wayyo Allahna."
Ta fad'a tana rike kanta tare da zamewa tayi zaman dirshan.
Yau ta tabbatar darajarta, kimarta da mutuncinta sun gama zubewa a idon daddy, fatarta d'aya Allah yasa su aunty da Habib basu san da wnn zancen ba.

Ranar naka sai naka , inji hausawa, sai yau tayi tunanin ta nemi 'yar uwarta ta sanar da ita halin da take ciki ko zata samu shawara mai amfani sbd tasan indai lami ce sai dai ta dad'a kwab'a al'amarin, Allah ya rabamu da kawaye masu gurguwar shawara.

_*Two weeks later*_

Cikin sati biyu aka kammala duk wani shirye shirye na tariya inna, mummy kam ba baki sai ido, duk tayi laushi.
Tare da habib akaje ɗauko amarya inna da 'yan uwanta.
Duk wnn abinda akeyi bintu bata sani ba, saida suka dawo daga yusa ya kira wayarta.

"Yes Habibina."
Daga d'aya b'angaren yace "Me kike yi yanzu?"

"Favourite ɗinka nake dafa maka."

"Godiya nake dear, ki gama da wuri anjima kad'an zan dawo akwai inda zamuje."

'Yes sir, Allah ya dawo min dakai lafiya."

Ta fad'i cikin d'oki.

Da sauri ta kammala komai ta shiga wanka ta tsantsara kwalliya tana jiran dawowarshi.

Yaran aunty nafi ta fara gani a kofar gida, suna shiga kuma ta hango Haulatun innarta dija da kanwarta.

"Wai me ya farune?"
Ta tambaya mamakin ganin su haulatu bayyane a fiskarta.

"Surprise ne ai nace miki ko kin manta?"

Itakam hankalinta bai kwanta da wnn surprise ɗinba, saukin ta dai dan bata ga alamun damuwa a tattare dashi ba, saima wani extra ordinary fara'a da take gani kwance kan fiskarshi.

Bata ida mamaki ba saida ta shiga ciki taga yar innarta da kannenta biyu sai matar kawunta, da goggonayenta biyu da kuma matan baffanayenta biyu sai yayyunta mata.
Sai kuma 'yan uwan daddy.

Tsalle tayi ta faɗa jikin inna Dija ta koma kan yayyunta a ma rasa wa zata kama sai murnar ganinsu takeyi.

"Éasy sistèr, kada ki mana b'arna."
Taji aunty  tana faɗa daga bayanta.

cikin fara'a ta  juya ga aunty nafi tace "Me akeyi ne aunty?"

Cikin zumud'i tace daddy ne yayi aure.

Sai a lokacin ta lura da canjen canjen dake cikin falon, anyi sabon  fenti snn an canza sabbin kujeru.
"Aure? Ina amaryar? Ta tambaya cikin rawar baki.

"Zo muje kiga amaryar."
Aunty ta riko hanunta suka shiga ɗaya daga cikin ɗakunan dake downstairs.

Buɗe baki tayi tana kallon innarta da ta juya kai tamkar bata ganta ba.
"Inna dake aka zo?"

"Itace ma amaryar, rakota akayi."

Salati ta doka ta kuma kamo laa haula, ta sake ta koma innalillahi, ta ma rasa wanne ɗaya zatayi.

"Babana?"
Ta fađa da karfi tana dariya, sai kuma ta daka tsalle ta fađa kan inna.

Duk da taji dađin ganin 'yar tata cikin koshin lafiya, ga alama kuma har an samu qaruwa amma sai ta dake ta ce.
"Ni kar ki karya ni."
Inna ta fađa tana tureta daga jikinta.

Bata damu ba taci gaba da dariyarta tace "Amma tsoffinnan kun mana bazata, dama soyayya kukeyi bamu sani ba?"

"Kaniyarki ke kam bintu, fita ki ban guri."
Inna ta fađa tana mata dankwalo.

Dariya aunty take musu, shima Habib da ya shigo yanzu gimtse  dariyarshi yakeyi ya gaisheda inna.

"Habibu me yasa ka kawo min wnn marar kunyar?"
Inna ta fađa bayan sun gama gaisawa.

Bintu tayi caraf ta cafe "Mutum da gidan ubanshi za a hana shi zuwa ne, balle kuma an samu qaruwa."

Banza inna tayi da ita tayi ta surutanta qarshe aunty tace suje ta rakata su gaisa da mummy.

Bayan sun gaisa da mummy gurin mmn larai suka shiga, nan kuma Habib kawai suka samu Mmn larai tana kitchen.
Cinyarshi tahau ta zauna tana cewa "Badai kwađayin abincin gidanmu zakayi ba."

"Wai, wai, wai, tashi wlh ashe haka kikayi nauyi, shi yasa inna take korarki a jikinta đazu."

Daure fiskarta tayi tace "Ya nake da buhun masara?"

"Duk da ban tab'a đagawa ba nasan kinfishi nauyi."

Maida kallonta tayi ga aunty nafi.
"Aunty kina jinshi fa."

"Kyaleshi kanwata zo muje nasa mmn larai ta miki mutumin naki."

"Yauwa auntyna."
Ta fađa tare da mikewa.

Har ta fara tafiya, ya kamo hanunta ya dawo da ita baya, "Ki kula idan kika sake irin tsallen ɗazu ranki zai b'aci."

"To, ta amsa kamar abin kirki, saida takai bakin kofa tace "Da yake da jikinka nake tsallenba." Tayi wuff ta fice.

Girgiza kanshi yayi yana dariya yace "Zaki dawo ne ki sameni."

Har dare suka kai ita da aunty nafi, sai labari suke tayi da 'yan uwanta.

A ranar daddy yake sanar dasu mafarin amintakarshi da mahaifin bintu.

Kamar yadda yake basu labarin.
Mahaifin bintu ya yi mishi hallaci da sadaukarwan da bazai tab'a mantashi a rayuwarshi ba, shi yasa baya wasa da kula da iyalan shi tun yana da rai har zuwa bayan ranshi.

Asalinshi ɗan cikin jalingone, shine kaɗai ɗa na miji a gurin mahaifinshi, sauran duka mata ne, yayyunshi  uku, sai kannenshi biyar.

Tunda ya taso yake ganin mahaifinshi yake yawan zuwa kauyen yusa, hakan yasa lokacin da ya kare makarantar gaba da primary ya fara binshi suna zuwa, nan ya fahimci ashe gonaki da dabbobi ya ke dasu a wajen, kuma akwai mutane biyu da suke kula mishi dasu.

Kasancewar 'yan kauyen suna da kara da son jama'a ga iya mutunta bako da ɗaukakashi shi yasa shima yaji kauyen da mutanen cikinta sun burgeshi, ga kauyen akwai yanayi mai daɗi.

Hakan yasa yaci gaba da zuwa tare da mahaifinshi.
A haka ya haɗu da wata yarinya mai nitsuwa, kunya da hankali, mai suna Fatu, wacce yaji mahaifinshi yake kira da Fatima.

Sosai nitsuwar yarinyar da tarbiyarta suke burgeshi wanda hakan yasa ko yaushe zasu je baya rasa abinda zai rike mata a matsayin tsaraba, har ya tafi karatu.

A lokacin yarinyar kwata kwata bata wuci shekaru sha uku bane.

Bayan yayi shekara ɗaya da fara karatu ya sake zuwa tare da babanshi, baisan dalili ba haka kawai yaji yana ɗokin ganin fatima.

Bai tashi sanin dalilin da yasa ya damu da lamarin fatima ba saida yaji labarin bikinta saura sati biyu da ɗan aminin babanta wanda shi kuma duk samarin kauyen sun fi shiri dashi, dashi suke zagaya kauyen yana  nuna mishi gurare da bashi labarin al'adun kauyen wato , Barkinɗo mahaifin Bintu.

Tashin hankalin da ya shiga a lokacin ba mai faďuwa bane har takai ga kowa dashi kanshi suka fahimci cewa son Fatima yakeyi.

Duk da abin ya tab'a mahaifinshi amma sai ya basar yayi kawaici ya nuna mishi yayi haquri fatima ba rabonshi bace dan iyayensu sun riga sun yi alqawarin aurar da yaransu ga juna.

Wasa wasa saiga daddy ya kwanta rashin lafiya kafin ranar ďaurin aure, shiko Barkinďo da ya shigo cikin jalingo yazo har gidansu yaga halin da yake ciki, kasancewar ya fahimci abokinnashi sai yayi mishi fatar samun lafiya ya tafi.

Kamar abun almara ranar da mahaifinshi ya tafi ďaurin auren fatima da Barkinďo washe gari sai gasu sun dawo da amarya da danginta gidansu daddy harma dashi kanshi Barkinďon.

Yana dariyar yak'e dan shima ďin daurewa yakeyi, ya ďakawa daddy dake kwance duka a baya yana cewa "Ango tashi ga Fatun na kawo maka."

Daddy bai tashi gaskata zancen abokinshi ba saida babanshi ya kirashi ya tabbatar mishi da cewa dashi aka ďaura auren, Barkinďo ya bar mishi Fatima.

Daga nan daddy ya tashi wasai tamkar bashine yake rashin lafiya ba.
Aka ci gaba da gudanar da biki.

Anan gidan babanshi Fatima ta zauna har saida ya kare karatu kafin suka tare a gidan da mahaifinshi ya kera mishi.

Saida suka haifi Aunty Nafi da shekara guda kafin shi kuma Baban Bintu yayi aure, amincinsu kuma nanan kamar da koma fiye da haka dan sosai daddy yake ganin kima da mutuncin mahaifin bintu.

Bayan aunty nafi sun haifi ďa namiji saidai baizo da raiba, daga baya suka haifi Habibullah.

Yana da shekara bakwai a duniya Allah yayi wa mahaifiyarsu Fatima rasuwa, daga nan rikonsu ya koma gurin kakarsu mahaifiyar daddy dan yaki ya sake yin aure.

Wnn gida da suke sauqa ciki filin mahaifiyar su Habib na gado wanda ta gada itama shine daddy ya gina suke sauqa a wajen.

Saida aka kara wajen shekara takwas kafin ya auri mummy kanwar abokinshi wacce itama mijinta rasuwa yayi ya barta da yara mata guda biyu kanana.

Anan yake basu labarin shi ya raďawa Bintu suna, sbd a ranar da aka haifeta ya isa yusa ba da jimawa ba ta zo duniya, lokacin da ya shiga ganin jaririya nan baffa ya mika mishi tare da ce mishi yayi mata huďuba, shi kuwa babu sunan da ya faďo mishi sai na Fatimarshi, sbd haka ya

mata huɗuba da sunan su kuma suke kiranta bintu.

Ikon Allah kenan haka Allah yake tsara al'amarinshi gashi yanzu kuma ya sake auren wata 'yar kauyen yusa a karo na biyu, kuma tsohuwar matar amininshi Barkinɗo, Allah yaji kansu yaji kan dukkan musulmi baki ɗaya.

Bayan watanni Biyar, abubuwa da dama sun faru ciki harda auren da miemie tayi ita kuma iman makaranta take nema zata ci gaba.

Amarya miemie dai ansha amarci kamar ba gobe saidai matsala ɗaya sa ango ya fahimta game da ita muguwar malalaciya ce, bata son aiki sam, ita dai barta da chatting da karatun Online novels.
Gashi shi  kuma mai gida bai yarda da girkin mai aiki ba, hakan ya fara kawo musu sab'ani dan sau tari sai ta ɗora girki taje tana chating ko karatu ta manta da abinci ya kone ko kuma ma ta manta da batun wani girki tabar cefane yayi ta zama sai taji yunwa yana kwakularta take tunawa ta tashi.
A haka wata rana ya turo cefane ta ɗora ɗanyen kifi a wuta ta kama harkokinta yanda ta saba har girki ya kone hayaki ya turnike kitchen bata sani ba, shiko sanin hali yasa yake  yawan lekowa kada wata rana tayi mummunar b'arna, ilai kuwa ya dawo ya tarar saura kaɗan wuta ya kama gashi da electric cooker take aikin.
Yana gama kashewa ya leka ɗakinta tana kwance rub da ciki sai chatting takeyi tana ta zuba murmushi.

Tsabar takaici takarkarewa yayi ya ɗaka mata duka a baya ya kuma ce ta tashi maza ta tafi gidansu bazai iya zama da ita a haka ba.

Dakyar iyaye suka sa baki ta koma nanma saida aka karb'e wayarta aka bata karama ta recieving calls kawai.
Mata mu kula dan Allah, ba karatun nvl ne abu mai muhimmanci ba, amfani da abinda aka karanta na faɗakarwa shi yafi muhimmanci.

Manyan  gidajen mai Habibullah ya gina ɗaya a Yusa ɗaya a garin magaji, da taimakon daddynshi ya bawa Ila ɗan kawunshi kuma abokinshi na Yusa ragamar kula da wajen, sanadiyyar haka Matasa da yawa suka samu aikin yi.

Bintu kuwa cikin Hukuncin ubangiji ta santalo ɗanta namiji kato dashi mai kama da babanshi. Farin cikin ciki gun daddy baya b'oyuwa, aunty Nafi kuwa kamar ta goyata, bar ta maganar Uban gayya.

Ranar suna yaro yaci sunan Baffan bintu Muhammad Mubarak (Barkinɗo)

Mummy kuwa yanzu tayi sanyi suna zaune da lafiya da Inna babu wata matsala, gata da kulawa sosai take nunawa Bintu da ɗanta.

Haka ma Mmn larai da suka zamo tamkar kawaye da Innar Bintu dan babu ruwanta shiga kitchen takeyi suyi aiki tare .

~Haɗaɗɗen tsumi take tsiyayawa a kofi wanda aka haɗa shi da sassaken b'aure da citta da kanumfari, sai kuma mazarkwaila da zuma, sai tashin kamshin kayan yaji yakeyi.

A hankali ya turo kofa tare sallama kasa kasa.

"Dattijo baka tafi ba har yanzu?"
Ta tambaya bayan ta ɗago tana kallonshi dan wani lokacin haka take ce mishi, a cewarta yanzu ya tsufa dan ya shi baban baffanta ne."

Idonshi kan kofin da ta tsiyaya  tsumin yace "Yau nan gidan zan kwana."

Kwankwaɗe tsuminta tayi ta ajiye kofi gefe.

Kusa da ita yazo ya zauna yana binta da mayataccen kallon da ya sata tsarguwa.

"Bacci zamuyi fa kaga dare yayi."

Baice komai ba sai kallon ɗanshi dake kwance yana bacci yayi ya shafi kanshi kafin ya sake kallonta.

"Yunwa fa nake ji Mmn Fatima."

Yunkurin tashi takeyi ya rikota yace "ina zakije kuma?"

"Abincin zan kawo maka."

"Ba wnn yunwan nake ji ba."
Ya faɗa bayan ya kwantar da ita a saman jikinshi yana mata kallon kasan ido.

Zazzaro idanu tayi tace "Kaga nifa banason haka kaje kayi kwanciyarka."

"A nan zan kwana to."
A tsorace tace "Innalillahi idan mummy ko inna suka shigo...

Kafin ta karasa ya haɗe bakinsu yana mata wani irin passionate kiss da ya kashe dukkan gabb'an jikinta.

A hankali ya zare bakinshi yana kallonta a kasalance yace "Ina son ki Fatima, ina qaunarki har ban san iya adadin son da nake miki ba, Allah ya bar minke, ya raya mana yaranmu wanda kika

haifa da wanda zaki haifa in muna raye Allah ya albarkaci rayuwarku."

Ido a lumshe ta kwantar da kanta bisa kirjinshi a hankali tare da zagayeshi da hannayenta......

Ni da ke shirin yi musu ban kwana nace amin tunda kin gagara amsawa kuma babu ruwana idan Mummy ko Inna suka shigo suka ganku...

*Wassalam.*

*Alhamdulillah*